*KAUNAR ƊOYE!!!*
💖 💞💖💞💖

© _2021_

*By*
_Fatima Batula_

*Wattpad:mrsbalarabe* .

*Dedicated*
_To My Bilkisu(matar soja) ubangiji Allah ya baku zaman lafiya ya baku zuri'a ɗaiyiba,y shiga tsakanin ku daga sharrin maƙiya da mahassada._

*Special gift to;*
_My Ahmed ubangiji Allah ya rayaka ya albarkaci rayuwarka ya shiryar da kai kan tafarkin addinin tsira addini gaskiya yasa ka zama me kira domin addinin musulunci, Amin Amin._

_Page_
_1-2_

✍ *✍ ǴŐĹĎĚŃ ṔĚŃ ẂŔĨŤĚŔŚ ÁŚŚŐĆĨÁŤĨŐŃ* ✍✍

*ωє αяє вєαяєя's σf ѕσ gσldєn pєn*
*ωє ωrítє αѕѕídíσuѕlч pєrcєívє nσ pαín,*
*ѕσ mαgícαl σur crєαtívє gσldєn pєn* ✍ *,вєhσld σur wσrdѕ.α prσduct σf σur pєn* *,ѕαvσur σur wσrdѕ, fσr ít wíll* *cαuѕє чσu nσ pαín.*

*Yadda Annabi, Tsira Da Amincin Allah Su Tabbata A gareshi , Yake Kirga Tasbihinsa.*

Daga Abdullahi bn Amr, Allah ya yarda da shi, yace; Na ga Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, yana kirga tasbihi da (yatsun) hannun damansa.

*INA MASOYAN LITATTAFAN KUNGIYAR GOLDEN PEN?*

*NESA TA ZO KUSA, TUNANIN RASHIN SAMUN NEXT PAGE YA KARE!.*

Kasance mutum na farko da zai fara karanta sabbin littattafan marubutan mu, a duk lokacin da muka yi typing. Kina/Kana iya samu, ta wannan damar ce kawai idan ka bi wannan links tare danna *LIKE* a shafin mu na Facebook zaka/zaki iya samun cigaba ko kuma ki samu duk littafin da kike buƙata namu daga farko.

https://www.facebook.com/Golden-Pen-Writers-Association-102095951667849/

Sai kun zo, kar ku manta a koda yaushe comments da sharhin ku yana ƙara mana ƙarfin gwiwa a wajen rubutu mai yawa.

_*Bismillahir~rahamanir~rahim*_

Rass! rass!! zuciyarta ke wani irin bugawa cike da tsananin tsoro da fargaba me illata ruhi da tunani.
Buɗe rufaffun idanuwanta tayi wanda suka cika da tsantsar tsoro da fargaba, jikinta ne ya hau ɓari da karkarwa tamkar wacce ke cikin matsanaicin zazzaɓi, ba komai ya haifar mata da hakan ba, illa sake sauke idanuwanta da tayi a kanshi a karo na uku sau uku a ɗan lokacin da bai fi awa uku ba.
Duk da sanin cewa ita jaruma ce jaruma kuma me jan hali da juriya amma a wannan karan ta rasa jarumtar ta.
Cigaba da karkarwa jikinta ke yi. Kallon ta yayi yana sakar mata kyakkyawan murmushin shi na ƙauna.
"Ina ƘAUNAR ki! zan cigaba da bibiyarki har sai kin ƘAUNACE ni kamar yadda nake miki".

Naji kalmar nan sau biyu kafin wannan duk wancan lokacin ko nace ɗazun ban taɓa ɗauka cewa ƙara jin wannan kalmar zata haibar min da rudewa ba, kalmar zai bibiye ni kuwa na dauka zan ji ta sau miliyan banji komai ba.
Yunƙurin tattaro jarumta ta nayi wacce ni kai na nasan ni jaruma ce, amma ina ban iya komai ba bayan rawar da vaki na yahau yi, Allah ya so ni ma a zaune nake da na tabbata yanzun na daɗe zube a ƙasa.
Wani irin buguwa naji zuciyata tayi wacce lokaci daya naji ta karamin karfin gwiwa tare da haifar min da wata zabuwar jarumta da karfin hali.Idona cikin nashi na zuba duk da har lokacin jiki na be gama rawa ba, amma na buɗe bakin da nake ji tamkar na rasa shi na ce, "Malam ka daina bibiyata haka karka dauka neman ka tsorata ni zai yi tasiri a raina har na ce ina sonka, dan haka kabar ma bi na dan bazan taɓa cewa Ina ƙaunarka ba", ban dauka bakina yana da saurar tsiywar da na sanshi da shi ba sai jin ina zaro kalamai cikin tsiwa yasa na tabbatar da cewa ni din ce dai, sai hakan ya ƙaramin ƙaimi ya kuma cire min tsoro ko ba komai baki na zai kwace ni, inma shi *MUTUM* ko *ALJANN*.
Bazai taɓa cin galaba a kai na ba, juyawa nayi da nufin nabar gurin naji yana fadin, "Nifa ina ƘAUNAR ki dan haka dole ke ma sai kin so ni".
Yana daga cikin abunda na fi tsana a duniya wato umarni da gadara cikin iko isa, ko uwar da ta

kawo ni duniya cikin kwantar da kai take umarta ta da lallami da ban baki duk da isarta akai na amma bata saka ni yin abu cikin isa dan isarta, shi waye da har zai min magana haka cikin isa da gadara a fusace na juyo gareshi na sauke mishi wani mugun kallo na ce cikin tsiwa, "Dole na so ka! a matsayinka na wa? tukunna kai waye? to bari ka ji ni *MEENAL* bazan so ka ba, ni ban ma taɓa jin ƙarfin hali irin haka ba wato dole na soka an gaya ma ana ƘAUNA dole ne da har kake wani umarta na cikin isa, bazan so ka ba, karka ɓata wa kanka lokaci ni dan bani da lokacinka, "ina kai aya na juya a fusace dan ya ban haushi da takaici haka ake yi.

Lumshe kyawawan idanuwanshi yayi masu jan hankali, wannan dalilin ne yasa bazai taɓa barin ta ba, tun daya ganta a tashar mota tana faɗa da wani me moto yaji kalamanta sun mishi zubun tsiwarta sun mishi tana da zafi amma bata gayan munanan maganganu duk zafi da tsiwarta kenan kan giskiya take magana, sai kuma jarumta da karfin hali da juriya da rashin shakka da rashin tsoron da ya gani tare da ita, ita ce zaɓin shi yaji kaunarta ta shige shi tun kallon farko.

Cikin sarsarfa ta isa cikin garejin motor, hango motar su tayi har ta kusa ciki da hanzari ta je ta hau gidan baya can inda nan  ne daman kujerar mata, bude jakarta tayi ta dauko korar ruwa ta bude ta sha ko taji sanyi a ranta, lumshe ido tayi ita kanta tasan tayi jarumta tuno irin yadda haduwarsu ta faru a yau din nan abun tamkar alamara wanda bata tunanin mutum dai mutu ɗan mutum jikin mutum zai yi hadda yayi, tun  fitowar ta daga kano suka haɗu a tashar moto suka rabu yana me shaida mata kalamanshi akan yana kaunarta ta kaunace ko yaita bibiyarta har sai ta amsa mishi tana sonshi,  anan ta barshi suna tsaka da tafiya motar ta dan tsaya aka sauka taje shago domin siyan ruwa sai kawai ta ganshi zaune cikin shagon me hade da gurin cin abinci, a haduuwarsu wannan kuwa da ta kasance ta uku a garejin Kaduna wacce anan zata hau motar zuwa Lagos ta kara ganinshi.

Duk ganin da take mishi da wasu irin kaya daban na canjin ƙabilu farko dai cikin shigar Fulani komai da komai harda sanda a hannun shi, amma da ta ganshi a gurin cin abinci shigar nufuwa yayi yanzun kuma cikin shigar  yarbawa.
Nannauyar ajiyar zuciya ta sauke tare da lumshe ido a ranta ta ce, "Ya Allah karka ƙara haɗani da wannan mutumin kuma, kasa har na isa Lagos lafiya," tana idarwa ta ƙara hangoshi tsaye da shigar Fulani ni kuma bayan dazun na yarbawa da ganshi, sannan kuma da rabuwarsu da shi bai fi minti hudu b ko uku.
Rass taji gabanta ya faɗi gashi ta kasa dauke idanunta daga gareshi.
Shi kuwa murmushi kawai yake yi mata hankali kwance cikin nuna so da ƙauna.
Ganin motar su ta tashi gashi a can gafe yana kallon ta yasa taji dan dama-dama, dan duk rabuwarsu hakan take hangoshi amma ta sameshi a gaba, kafin ta gama wani tunanin motar har ta fita daga tashar, ajiyar zuciya ta sauke a ranta ta fara addu'o'in tsari kallon ilahirin mutanen da ke cikin motar tayi taga duk kafirai ne ita kadaice macce musulma sai kuma wasu maza da ta gani da shigar hausawa wanda hakan ya tabbatar mata cewa musulmai ne su.

Shiruu bayan munyi tafiya me nisa mun fita daga cikin garin Kaduna munyi nisa sosai mun dau hanyar Lagos amma bamu yi rabin isa ba, tun ina duba lokaci har n gaji tun ina

muskuce-muskucen gajiyA da zama har na kife kai na wani irin barcin gajiya ne naji yana son kama ni, tun biyar da na baro gida zuw.
Har barci ya fara fusgata naji ringin din wayata wacce ke cikin jakata tashi nayi cikin jin daɗina dan ringin din ya sanar min da me kiran tawa.
"My sweet Aunt!"
Da sunan da ya baiyana akan screm din wayar kenan. Murmushi tayi tare da daukar wayar tare da fadin, "Hello Aunty waiyo Allah na Aunty haka daman Lagos din ke da nisa, kamar n koma gida ma". Wata sabuwa inji yan caca ashe masu tsiwa sun iya shagwaɓa haka, to gani nayi tayi mgnr cikin wata irin shagwaɓa kamar ƴar shekara sha shidda.

Daga can ɓarin naji ta ce, "Sorry Autar Maama gani nan muna ta murna haba  Autar Maama shekara nawa rabon mu da juna, baki son ganin Aunty ki ne da yaronki".
  Ƙara shagwaɓewa tayi, "Ina so mana amma kin san ban iya jure zama guri daya duk na gaji, gashi yanzun kusan goma fa".
"Sorry kinji ai kun kusa nan da 12pm zaku iso, ko da zaki iso muna tashar muna jiranki".
Ji nayi kamar nayi kuka har ga Allah n gaj iya gajiya kuma ace yanzun a hakan ina da zaman awa biyu tabb.
A hakan muka gama waya da Aunty na wacce na dau shekara shidda har da rabi ba tare da na saka ta a cikin idona ba, bayan kuma ita ce ni nice ita yayata ce ina mugun sonta so mara misali ita tai min komai, tun bayan aurenta da shekara daya mijinta aka dawo da shi legos da aiki yanzun haka ita ma ta aikin take yi, ban taɓa zuwa ba sai yau munyi munyi Mama tabar ni inje taki sai yau bayan nima na kammala karatu na na H N D. Ji nake kamar zani Makka za bar murna da zumudin haduwa da farinciki na.

Dan a zahirin gaskiya Lagos bata min ba ko kadan garin arna garin matsafa duk wani bariki sunyi kaurin suna, amma yau gani ina daukin zuwa daran jiya tsabar murna ko barci ban yiva fatana da Allah yasa kamar yarda nake Ify n dawo lafiya.
  Munyi nisa sosai har barcin wuya ya dauke ni ƙiii naji motor ta tsaya da sauri na ɗago kai na dan ganin abunda ke faruwa mun isa ne ta tsayan ko kuwa yaya. Hayaniyar da naji ita ta ƙara tabbatar min da cewa mun isa kenan, dan guntun tsaki naja jin yaruka iri daban daban  ina da ƙavilanci matuƙa bana so ko sha'awar wata ƙabila bayan tawa ta Hausa hasalima ni haushi ƙabilu suke ban.

Juyo da kallo na zuwa jikin motor naji, juyowar da zan sakata a shafin farkon shafukan rayuwata.
Wani rasss naji tare da jin tsull ta kasa ne, fitsari ne ko zawo ba zan iya tantancewa ba ko da kuwa duvawa nayi, dan ina cikin yanayin da yafi tsoro tsoro, tsoron da ke haddasawa kai da ruhi zuciya kwakwalwa tsoro wannan ƙaran ban ma iya runtse idon na sake buɗewa ba zuba mishi ido kawai nayi ina kallon shi yana yimin murmushi  "Daman tun can yana cikin motor ko kuwa? kai ina bazan manta ba  ina kallon shi a ƙasa aka kulle motar bayan kuma ta cika sannan kuma duk na kalle mutanen da ke ciki ba ko me kalar kayan fulani balle na fulani, oh ni *MEENAL* na shiga uku ta tabbata kenan Aljani ne meye nai mishi yake son dagulamin lissafi.

Ban iya dauke ido na a kanshi ba, gashi ina jin abunda ke fita ta kasa na yana ta ƙara fitowa jikin nawa ma yayi sanyi libes balle na yi wani irin yunkuri ina cikin wani irin hali wanda ganin wannan halittar cikin motor ce yahaifar min da hakan kuma wai a gabana a zaune.
"Ina ƘAUNARKI *MEENAL* ki amince da ni kaunar gaskiya nake miki ki amsamin kina so na", yana kallonta yana mgnr bai damu da ganin halin da take ciki ba.
Bana ce banji ba ji ma kai ma isarwa dan hatta hancin ciki na saida suka shaida naji, ji nayi wllh kamar na yi me n ɓace n ganni a gida a kwance ko me ma ni?

Ace wai har mutane cikin motar sun sauka Meenal bata sani ba me motar yayi mgn su sukai zai yi gaba ne ita ina ta ji tayi nisa cikin duniyar saƙau.
"Zan tafi Meenal amma zan dawo zaki yi ta gani na har inda bazaki yi mamaki va, zan cigaba da bibiyarki ne har sai kin amsa min kina so na", yana gama faɗa ya tashi ya fita daga motar bayan ya gama yi mata kallon tsantsar so.
Taji jin daya ƙara rikitar da ita duk da a zaune take amma yadda jikinta ke rawa tamkar wacce aka tsirawa wutar lantarki.
Jijjigar na naji anyimin da karfi yasa na juyo da sauri tare da sakin wata irin ƙara wacce wllh zan rantse ban iya irin ta ba.
"Meenal lafiya na shiga uku lafiya kike kuwa Meenal," a ruɗe take yi mata mgnr.
Janyota suka yi daga motor ita da kyakkyawan mijin ta shi ma faɗi yake, "Tsiwa baby lafiya kuwa meye sameki?"
Ganin bata cikin halin da zata iya yin mgn yasa suka ja ta gurin motarsu suka shigar da ita, shi ya dawo ya kwashe uban akwati nan da ta jibgo kamar wacce zatai hijira....

*~Mrsbalarabe~ .*

*ƘAUNAR ƁOYE!!!*
_(THE SECRET LOVE!🖤)_

*Fatima Batula✍🏼*

_Wattpad:mrsbalarabe._

*Dedicated to my Anup(my happines) Allah ne kawai yasan irin son da nake yi miki, ke abun so ce dole duk wanda ya raɓeki ya soki, baki na bashi da kalaman godiya da nuna irin matsayinki a gurina sai dai kawai na ce ke ta musamman ce a cikin rayuwa ta, Allah yabaki Ify ya baki miji na gari. Amin thumma Amin.*

_Page_
_3- 4_

✍ *✍ ǴǪ́Ĺ́Ď́Ę́Ń́ Ṕ́Ę́Ń́ Ẃ́Ŕ́Í́Ť́Ę́Ŕ́Ś́ Á́Ś́Ś́Ǫ́Ć́Í́Á́Ť́Í́Ǫ́Ń́* ✍✍

*wє αrє вєαrєr's σf sσ gσldєn pєn*
*wє wrítє αssídíσuslч pєrcєívє nσ pαín,*
*sσ mαgícαl σur crєαtívє gσldєn pєn* ✍ *,вєhσld σur wσrds.α prσduct σf σur pєn* *,sαvσur σur wσrds, fσr ít wíll* *cαusє чσu nσ pαín.*

*Yadda Annabi, Tsira Da Amincin Allah Su Tabbata A gareshi, Yake Kirga Tasbihinsa.*

Daga Abdullahi bn Amr, Allah ya yarda da shi, yace; Na ga Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, yana kirga tasbihi da (yatsun) hannun damansa.

*INA MASOYAN LITATTAFAN KUNGIYAR GOLDEN PEN?*

*NESA TA ZO KUSA, TUNANIN RASHIN SAMUN NEXT PAGE YA ƘARE!.*

Kasance mutum na farko da zai fara karanta sabbin littattafan marubutan mu, a duk lokacin da muka yi typing. Kina/Kana iya samu, ta wannan damar ce kawai idan ka bi wannan links tare danna *LIKE* a shafin mu na Facebook zaka/zaki iya samun cigaba ko kuma ki samu duk littafin da kike buƙata namu daga farko.

https://www.facebook.com/Golden-Pen-Writers-Association-102095951667849/

Sai kun zo, kar ku manta a koda yaushe comments da sharhin ku yana ƙara mana ƙarfin gwiwa a wajen rubutu mai yawa.

_*Bismillahir~rahamanir~rahim*_

Duk yadda suka so da na buɗe baki nayi magana na kasa, badan kuma bana jin su ba sai dan kawai na rasa baki na dama abunda ke sarrafa magana.
Kuka sosai Auntyn ta fara yi, "Dan Allah *MEENAL* kiyi magana meke faruwa ne? meye ya same ki?". Duk a ruɗe take jero tambayoyin.
Mijinta da yake gaba yana duƙi shi kan shi ya ƙara tsorota sanin wacece Meenal, "to ko zamu wuce asibiti ne," y faɗa jiki a mace.
Ji nayi kamar an hura min isa a ido hakan yasa na ƙifta su, wanda hakan yasa tunani na yai nasarar dawowa jiki na.
"Aljani ne Aunty bibiyata yake yi, na shiga uku ni zan koma gida gurin Maama wllh Aljani ne

shi", n fashe d kukan tsoro dan har ga Allah n tsorotan tsoro ma me ban tsoro.
"Aljani kuma wani irin aljani kuma Meenal?  shi waye shi? a ina kika san shi da har kika san shi aljani ne??“
Idanuwanta cikin nawa ta dafa duk kafaduna biya take yimin maganar cikin kulawa da nuna damuwa dan Aunty Sadiya tawa ce ni kuma ta ta ce.
Ban kai ga buɗar baki ba naji ƙii alamar tsayawar moto, in kai kallo na na gan mu cikin wani gida babba duk da kasancewa dare ne sosai amma na ga kyawun gidan.
"Ku fito mu shiga," yana faɗa ya fito riƙo ni Auntyn  tayi muka fito nima nayi lamo jikin ta a tsora ce gani nake zan ƙara ganinshi.
A babban falon gidan muka tsaya a ina Auntyna Sadiya ta zaunar da ni kan daya daga kujerun daka dakin itama ta zauna.
  Yaya Miftahu kuwa(Sunan d nake kiranshi da shi kenan) yake ya dauko min ruwa me sanyi ya kawomin.
Amsa nayi dan ina da bukatar shan ruwa na sha sosai sannan na miƙa mishi kurar ina ta sauke ajiyar zuciya.
Shi ma zama yayi kusa da ni cikin kulawa ya kalle ni ya ce, "Tsiwa baby gayamin abunda ya faru".
  Daki-daki na fara basu labarin haduwata da shi tun a tashar motar Kano har kawo yanzun kuma da na sake ganinshi a cikin motar bayan bashi na gani na daura da fadin, "Kuma yace dole sai na so shi indan ba haka ba zai daina bibiyata ba har abada," harda ƴar kwalla ta na karasa mgnr ina yi, dan na tsinke matuka.
Shiru suka yi suna nazartar abun inda su kan su suka sha mamaki yaya Miftahu ne ya fara cewa, "Ba aljani ba ne Autar Maama kawai yana son ya tsoratar da ke ne, ki kwantar da hankalinki ba abunda zai faru kina tare da mu, yanzun dare yayi sosai karfe biyu saura ki je ki kwanta karki ji komai ba abunda zai faru," yakai ƙarshen mgnr yana kallon matar ta shi.
" Ehm Auta kawai dai ki je ki kwanta dare yayi karji ji komai abunki ba wani aljanin da ya isa ya cutar da mu ko kin manta ne? balle shi ma ba aljanni  ba ne kawai ki samu muje ki kwanta ki huta dare yayi".

Tashi na tayi muka nufi wani ɗaki babba ne sosai dan harda kujeru a ciki daga gefe kuwa bayi ne, Yaya Miftahu na biye da mu tare da jibgin kayan da na jibgo, bakin gadon ta zaunar da ni cikin tsantsar kulawa ta ce, "Meenal dan Allah ki kwantar da hankalinki ki kwanta ki huta kiyi wanka sai kiyi salla ki kwanta".
 Sai yanzun da naji Aunty Sadiya tayi mgnr wanka na tuno da abunda ya faru da ni na jin fitar abu ta ƙasa na, wata irin kunya naji, "Na shiga uku ni Meenal waye wannan? tun ina ƙarama rabona da yin fitsarin kwance balle na tsaye," n gane fitsari ne ta hanyar jin zarnin da naji yana tashi a jiki na.
  Runtse idon bacin rai nayi wllh ba abunda yafi min wannan ɗaci a duniya wai ni ce *MEENAL MANSUR MANGA* da fitsarin tsaye, bazan taɓa yafewa wannan halittar ba inma mutum ne ko aljann.
Duk sun fahimci halin da nake ciki hakan yasa suka yimin sallama cikin kulawa suka fita tare da janyomin ƙofar.
Da sauri na tashi na faɗa bayi dan ni kaina naji ina ƙyamar jiki na dan warin da nake bugawa

dan ma su ɗin nawa ne. Na daɗe sosai a bayi ina wanka tare da tunanin shi a rai na, ina fatan nayi ramuwar gaiyya a gareshi na saka shi yin zawo a wando kamar yadda yasa nayi fitsari, tsabar rashin hakuri irin nawa da mugun fitina sai naji dama na ƙara ganinshi naci mutuncinshi na manta da wahalar fargaba da tsoron da na faɗa dazun.
Da wannan tunanin na kwana a rai na bayan na gama jeru dukan sallolin da ke kai na dan ma kasaru zanyi.
Ban ji ma da kwanciya ba barcin wuya ya dauke ni, dan ina da gajiya sosai a rai na, tafiya yankin azaba.

ASUBA TA GARI MEENAL.

Sama-Sama nake jiyo muryar Aunty Sadiya tana faɗin, "Meenal daure ki tashi kiyi Sallah sai ki koma".
Cikin barci nace da ita, "to!.
Vata barni ba saida ta tabbatar na tashi sannan ta fiti, ni kuma na je na dauro alwala na dawo na tada salla ina idarwa na koma na kwanta dan ji nayi ma kamar ina kwanciya ta tashe ni.

Ƙarfe goma sha biyu saura kwata na tashi, tare da taimakon wata irin muguwar yunwa a ciki na, hakan yasa kawai ina tashi na fito, sakin baki nayi ina duvan gidan gaskiya gidan ya fitino ainun kamar ba'a nan ba tsari da fasalin gidan bai yi kama da na ƴan 9j.
"Auta kin tashi daman yanzun nake son zuwa na ƙara duboki".
Sagaga nayi ina kallonta ko nace shigar da tayi Aunty na ce haka cikin shigar arna to na arna mana zance, lagos ta lalatamin ƴar uwa ban kai karshen tunani n ba naji an rungume ni da karfi.
"Oyoyo Aunty Meenal kin zo lafiya jiya naƙi yin barci na tsaya jiran ki baki zo da wuri ba",da turanci yake yin maganar cikin kwarewa.
Duƙawa nayi na rungume shi a ƙirjina ina jin sonshi har raina.
"Am sorry dear nayi dare jiya". Baƙir kenan yaron yayata.
Ban taɓa ganinshi ido da ido ba sai a waya sunkutarshi nayi.
"Muje ki ci abinci nasan kina jin yunwa karki biye Baƙir sarkin surutu".
Ni duk sai naji bana jin yunwar ma tsabar ɗaukin ganin baƙir.
Muna nan tsaye Yaya miftahu ya fito, "Tsiwa Baby kin tashi lafiya ya kwanan legos amma baki ƙara yin wani fitsarin ba dai ko,kai ni kuwa zan so ganin wanda ya saka Tsiwa baby fitsari," cikin zolaye yayi mgnr da harshen Hausa.
Wani irin kututun bakin ciki naji ya kama ni ai fa abun nema a gurin yaya Miftahu ya samu na bani da zolaya bata rai nayi nai kici-kici da fuska nace," Wllh tafiya zanyi gida zan koma abuna bazan zauna ba kuma bazan kuma dawowa ba," ina faɗa na juya ɗakin duk suka biyo ni.
Da ƙyar suka shawo kai na, na hakuri falon muka fito nan na hau cin abinci haniƙan.
Ina cikin farin ciki sosai ni har na manta da zancen wani can daban wanda ban san shi ba, Baƙir baya jin hausa ko ƙadan ko zo in kashe ka bai ji abun takaici nai ta fada ina masifa basu son ƙabilarsu daga zuwa bariki sai su manta da asali,shiru kawai duk sukai min dan idan ina fada na shiru suke yimin dan ina yinshi ne kan gaskiya.

Haka muka wuni ranar dan ranar yau ta kasance sati ba su da aiki basu fita ko'ina, haka muka wuni muna firar yaushe rabo.
Sai dare naje dakin da a yanzun ya zama nawa na kwanta.

Yau da kai na na tashi duk da ban ji kiran sallah ba tsaki naja bayan na tashi sam ni legos bata yimin ba bayan mutane ukun nan wllh kaf legos ba wanda nake so duk na tsane su ba to me zanyi da arna ina musulma me zanyi da yarbawa ko igala ibra ina bahaushiya, gari duk arna ace badai kaji kiran sallah na tashi ba, bayan na gama yin mitata a fili sannan na tashi naje da dauro alwala na dawo na tada salla bayan na idar na koma na kwanta.
Sai bakwai na tashi, wani wankan na ƙara yi na dawo gaban mirrow Light makeup nayi kamar yadda daman na saba, ina da kyau iya bakin gwargwado dan ni wankan tarwatsa ce abu mafi kyawu cikin hallitar fuskata sune bakina da dimple dina me lutsawa ko murmushi nayi sai fararen idanuwa na duk da dai ba manya ba ne amma tarr suke, bani da wani hanci  amma kuma ba gajere ba ne kamar yadda yake ba dugo ba, ina kuma da qiba ta ta fuskar da ta jiki.
A halitta kuwa zan iya cewa bani da wani naƙasu dan ina da zati abu mafi kyawu nidai a gurina hips dina amma sauran mutane ƙawayena classmate yafi burge su a tare da ni ƙirjina dan Allah ya azurtani da su tantsan-tsantar irin kuma cikakkun nan masu faɗi kuma a sama suke.

Cikin shigata na hausawa na shirya wato atamfa riga da siket kaya na kenan duk inda za'a je zanyi irin wannan shigar abu na. Falon na fito wani daddanan ƙamshi ne ya duki hanci ne lumshe ido nayi da Aunty na ta sauya sosai amma bata sauya gurin hada girki ba, kicin din na nufa da sauri na kau da kai, wato dai yanzun yaya da Aunty basu da kunya legos ta cire musu yar kunyar nan ta Hausawa juyowa nayi zan tafi.
"Twiya Baby ya zaki juya kuma ki shigo mana ki ga abunda Honey ke dafa mana".
  "Ya bazan juya ba, na shigo kuna haka da alamar yanzun dai baku da sauran kunya gani na bazai hanaka shafata ba," a zuciya na faɗa a fili kuwa ma na rasa abun cewa.
"Meenal ki shigo waina nake dafawa dan ke nasan kina son waina".
Juyowa nayi tare da arowa fuskata wani murmushin ƙarya.
"Kun tashi lafiya? to tunda ga gwani nan yana tayaki bari ni naje gurin Baƙir, kuma naji wainar bata yi dadi ba sai ka sake yinta tunda ba zaka barta tayi ita kaɗai ba", ni dai nasan bazan canja ba duk yadda naso kar nayi mgn makamciyar hakan sai da nayi tsabar rashin gani a ƙyale.
Dariya yayi harda sauti, "Idan bana kusa ne ma zata yi ta ba dade idan ina kusa kuwa duk abunda zata yi shi zai fi domin....
" Am ni kam na tafi, "na fada  lokacin ma har na kusa barin gurin dan Yaya ba kunya ne da shi ba dukkan su ma.
Dariya suka yi sosai, su kansu sun san sun sauya to ya zasu yi aka ce idan gaje garin da ka ga suna yawo da bindi samu igiya kai ma kayi bindin da shi, wannan shi ne cin ribar zama a legos da mutanen cikin ta.
Dakin Baƙir na dufa wani tanƙamemen daƙi ne yakai nawa abun takaici wannan dan shekara shiddan ne ke kwana a ciki ko da naje y a tashi hakan yasa nai mishi wanka na shirya shi tsaf sannan muka fito.
Tana kan cinyarshi yana bata wainar a baki, guntun tsaki naja iya laɓɓa abun takaici a gare ni dan a gare ni kam mutanen da sun manta su hausawa ne.

Ban iya ko kallon su haka na samu naci wainar abun takaici kuma suna a gaban Vaƙir yaron ma da alama ya saba da ganin hakan dan ko a jikinshi.Su kuwa wani abun dan ganin ta ne yasa basu yi.

"Tsiwa Baby ya kamata mu fita dake ganin gari".

"Am kamar wani garin arziƙi me zan gani bayan tsiya".
dariya yayi yana kallon fuskarta ita kuwa kanta na ƙasa gudun kar ta ga wani abun.
"Tsiya ko baki zo ki ga yadda tsarin garin yake da mutanen ciki".
Taɓe baki nayi, " hm Arnan ni me zan gani a gurin arne".
 "Ke waya gaya miki wai duk arna ne a garin da musulmi sai da ki ce yare ne".
"To ni me zan gani a gurin yare kuma, ni wllh bayan ku da bazan tava zuwa legos ba".
"Zaki zo mana ina ji a jiki na bayan mu da wani abun alkairin da ya kawoki legos".
 Bai jira na kara bude baki ya ce, "Karki cika min baki yau gobe naji kin ce min kin fara son wani a nan zaki zauna tare da shi kuyi rayuwa", cikin zolaya ya ƙarasa mgnr yana ƴar dariya abunshi.

"Wllh Allah ya kyauta Allah ma ya tsare ni wllh dan ku ne kawai na zo garin nan, duk fadin duniya na rasa wanda zan so sai dan legos naci baya wllh Allah ya tsare ni ma", na faɗa cikin tsiwa kamar yadda na saba.
"Kyaleshi kinji auta daman haka yake so ai yaga ya ɓata miki rai, tashi ki shirya mu fita shoping".
 Tashi nayi Bakir na rike a hannun na bar gurin, ba canja kaya zanyi ba kawai mayafi zan dauka na zaro wani farin gyale cikin kaya na, na dauko flatshoe fari na saka da farar jakata ta rikewa na fito hayaniyarsu naji a waje hakan yasa na biyo bayan su.
Ya isa na daina mmkn su amma n kasa dainawa yanzu dan Allah a haka zasu fita yadda suke dai a daki, gida da waje ya zame musu daya kenan.
Kau da kai nayi basu tsaya bi ta kai na ba suka shige cikin motar, shiga baya nayi ni da Baƙir yaja motar direba ya bude mana wangalelen get ɗin.
Bana da ra'ayin wani kallon gari hakan yasa na maida hankali gurin wasa da Baƙir abu na, ƙarar saƙo naji ya shigo wayata ban kawo komai a rai na ba na ɗauka na shiga karantarwa.

 _Haba MEENAL ya zaki min ruwar ganin fuskarki bana so kuma na shigo cikin gidan,amma ba komai tunda yanzun gashi zaki fito zai na ganki. daga me ƘAUNAR ki fiye da kowa da komai a duniya Meenal ki yarda da ni son gaskiya nake yi miki ki amince da soyayyata. Sai mun haɗu ina fatan dai kin shirya cikin shigar fararen kayan da suka fi yi miki kyau"._

Na duba number na ga an ɓoye tsaki naja me karfi wanda har yasa su Aunty ji na Yaya ne ya fara cewa, "Lafiya Meenal?" kusan a tare suka haɗa baki da Aunty sadiya.
Wayar na miƙa mu su hankali kwance dan a shirye nake dana ƙara ganinshi sai ya gayamin shi waye mutun ko aljann, sai na raba alaƙa ta da shi ko shi waye kuwa.........

~Mrsbalarabe~✍🏼

*ƘAUNAR ƁOYE!!!*
_(THE SECRET LOVE!🖤)_

*Fatima Batula✍🏼*

_Wattpad:mrsbalarabe._

*Dedicated to my Anup(my happines) Allah ne kawai yasan irin son da nake yi miki, ke abun so ce dole duk wanda ya raɓeki ya soki, baki na bashi da kalaman godiya da nuna irin matsayinki a gurina sai dai kawai na ce ke ta musamman ce a cikin rayuwa ta, Allah yabaki Ify ya baki miji na gari. Amin thumma Amin.*

_Page_
_5- 6_

_Tnx for d correction *Queen Indo* (Missparrot) baki abun magana ki huta na gaishe kyauta._

✍ *✍ ĠÓĹĎÉŃ ṔÉŃ ẂŔÍŤÉŔŚ ÁŚŚÓĆÍÁŤÍÓŃ* ✍✍

*wє αrє вєαrєr's σf sσ  gσldєn pєn*
*wє wrítє αssídíσuslч pєrcєívє nσ pαín,*
*sσ mαgícαl σur crєαtívє gσldєn pєn* ✍ *,вєhσld σur wσrds.α prσduct σf σur pєn* *,sαvσur σur wσrds, fσr ít wíll* *cαusє чσu nσ pαín.*

*Yadda Annabi, Tsira Da Amincin Allah Su Tabbata A gareshi, Yake Kirga Tasbihinsa.*

Daga Abdullahi bn Amr, Allah ya yarda da shi, yace; Na ga Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, yana kirga tasbihi da (yatsun) hannun damansa.

*INA MASOYAN LITATTAFAN KUNGIYAR GOLDEN PEN?*

*NESA TA ZO KUSA, TUNANIN RASHIN SAMUN NEXT PAGE YA KARE!.*

Kasance mutum na farko da zai fara karanta sabbin littattafan marubutan mu, a duk lokacin da

muka yi typing. Kina/Kana iya samu, ta wannan damar ce kawai idan ka bi wannan links tare danna *LIKE* a shafin mu na Facebook zaka/zaki iya samun cigaba ko kuma ki samu duk littafin da kike buƙata namu daga farko.

https://www.facebook.com/Golden-Pen-Writers-Association-102095951667849/

Sai kun zo, kar ku manta a koda yaushe comments da sharhin ku yana ƙara mana ƙarfin gwiwa a wajen rubutu mai yawa.

_*Bismillahir~rahamanir~rahim*_

Dariya naga sun fashe da ita, "ah lallai wannan masoyin gaske ne MEENAL, ke fa kinyi kamo Allah yasa ma dan Lagos ɗin ne".

Cike da zolaya yayi maganar.
Shiru Aunty Sadiya tayi tana son fahimtar wani abu, wasu daga cikin kalamanshi abun dubuwa ne taya to aka yi ya san yanzun zata fito? Saurin kauda zancen tayi dan bata so ta karaya balle kuma ƙanwar tata.

"MEENAL wannan mutum ne fah amma dai da dukan alama masoyi ne na gaskiya, ya kamata ne ma ki saurare shi ki ji".

Sai naji na gamsu da abunda Aunty Sadiya ta ce, tabbas hakan ne kuwa. Ɗaga kai nayi alamar to.
Dan ban kawo komai a rai na ba, na cigaba da wasa da Baƙir abu na.
Bayan mun yi ƴar tafiya naga an tsayar da motor su ne suka fara fita sun wani rike juna kamar za'a raba su.
"MEENAL ku fito".

Ya faɗa da turanci, har da nayi niyar cewa a'a na tuno idan ban fito ba a ina zan ganshi. fitowa nayi rike da Baƙir a hannu na.
Gurin yayi kyau, shoprite ne babba, ya ƙawato daman ai ko naƙi Allah bazan kushe kyawun lagos ba.
Su gaba suka yi abunsu ni kuwa ina baya kadan ni da Baƙir.

Duk sai naga an fara kallo na, na san shigata ce ta jawo hakan, duk da bana son kallo yana kashe min jiki idan kuma tafiya nake yi naji ina hardewa, amma duk da naji ina hardewan bai hana ni cigaba da tafiya abu na ba, kallon yayi yawa hakan yasa na fara hardewa dan har saida naci tintiɓe, da Allah yaban sa'a muka haɗa ido da wani yana kallo na na banka mishi uwar harara har da murguɗa baki.

Su wato idan mutum ba irin shigarsu yayi ba bai waye ba shi kenan ya zama abun kallo.
Wani guri na hango can ba kowa naja Baƙir dan idan har na cigaba da tafiyar nan faduwa zanyi, muna zuwa na zauna.

"Kai Allah wadai! Sai mutum yayi shirgarsu ne zai waye tir kuma ni wallahi ba zan taɓa canjawa ba kun dade baku kalle ni ba," kamar da wani nake yi yadda na bararraje ina sakin faɗa abuna hankali kwance.
"Shiyasa nake sonki shiyasa nake ƘAUNARki MEENAL".
Rass naji gaba yayi wani irin mugun faduwa taya zan iya mantawa da wannan muryar ɗago kai na nayi domin kallonshi naƙara tabbatarwa ido cikin ido muka yi wanda hakan ya ƙara faɗarmin da gaba. Murmushi ya sakarmin ya zauna akan kujerar da ke fuskarta ta.
Rintse ido nayi, "Ya isa haka dole na fuskance shi ko shi waye".
"MEENAL ina ƘAUNAR ki MEENAL komai naki burgeni yake yi".
"Kai waye? meye matsalarka da ni, Meyasa kake son ka tsoro ni?? Malam bari ka ji ni MEENAL magana ɗaya nake yi ba biyu ba bana ƘAUNARka kuma bazan taɓa ƘAUNAR ka ba, dan haka kabar wahalar da kanka bana son na ƙara ganin fuskarka, idan ba haka ba zaka sha mamakin abunda zan yima ko aljani ne kai wllh nafi ƙarfinka dan haka ma ka gama gabanka, "cikin tsiwa nake gayamashi magana ba tsoro ba shakka balle fargaba.
" MEENAL ki fahimta ƘAUNAR ki fa kawai nake yi ba komai ba, karki ce haka nasan zaki so ne nima zaki so ni kamar yadda nake miki", cikin sanyin murya yake maganar cikin harshen hausa.
Rintse ido tayi, tana jin wani irin zafi me raɗaɗi a ranta har gwara da kalamar ƙiyayya yake gayamata da wannan kalmar ta yana ƘAUNARta.
"Kai wai baka da hankali ne jakin ina ne kai bana ƘAUNAR ka kuma bazan so ka ba, kai infact ma na tsanake na tsaneka.
Cikin zafin nama irin na jaruman maza ya tashi tsaye tare da bugun teburin gurin da karfi wanda hakan yasa hankali jama'ar gurin ya dawo gurin.
Nima tashi nayi a zabure idan hauka yake ji nawa ya fi nashi idan dan bala'i ne shi to ni ƴar guguwa ce. Wani irin gurnani yake yi lokaci daya ya sauya daga me kyau zuwa me muni. Duk da na fahimci hakan amma na dake ɓacin rai nima ina ciki ai wa zai yi wa hauka dan mahaukaciya ne shi to nima haka.
Ido cikin ido muke kallon juna a inda yake wni irin gurnanin ɓacin rai me ban tsoro dan bai yi kama da irin na mutane ba, tsabar jarumta ce irin tawa yasa na dake da kuma nima din na harzuƙa.
Cikin wata irin murya wacce bana ce irin ta mutane ba ya ce, "INA ƘAUNARKI MEENAL," cikin ɗaga murya a kuma fusace.
Nima fusatar nayi zan nuna mishi hauka na, da nayi fatan kar na nunawa kowa shi na ce "I hite u," cikin daga murya a fusace da kakkausar murya,dan har ga Allah raina ya mugun ɓaci matuƙa.
"I LOVE U MEENAL".
"I HITE YOU!"

runtse ido naga yayi ya buɗe duk jarumta ta saida na ja baya dan a iya sani na da halittar Allah ta ɗan adam idan ranshi ya ɓace idanuwa ja  suke komawa ba green ba.
 "Dole ki so ni Minel dole ki zo ni".
   Duk da ina cikin halin tsoro amma sai da na iya cewa, "Vazan taɓa sonka ba na tsaneka kara na mutu da na so ka".
Dafa ni naji anyi ta baya, wani irin kududu naji ciki na yayi, a tsoro ce na juyo nannauyar ajiyar zuciya na sauke tare da lumshe ido ganin Aunty Sadiya ce.
Jiki a mace ta ce, "Meenal!
Jin yadda ta kira ni wani iri yasa na ƙara zuba mata ido.
" Ke da wa? ta faɗa a sanyaye.
Juyawa nayi me zan gani wayam ba mutum ba alamarshi, waige-waige na fara yi ina kalle-kalle. Ga mutane duk sun zuba min najiyamo.
Juyowa nayi baki na rawa ina son yin magana Yaya miftahu ya tare ni," MEENAL ke da wa kike?"
To na shiga abunda yafi uku ni Meenal me suke nufi, dakewa nayi murya can na ce, "shi ne shi ne ya zo".
Gargixa kai Aunty Sadiya ta fara yi dan tunda suka jiyo ƙara hankali su ya dawo gurin basu ga kowa ba, bayan ita kadai da ke ta zuba masifa da bala'i, wanda duk sauran mutane ma basu ga kowa ba.
Jiki na ya mutu to kar dai ace Aunty Sadiya basu ganshi ba ne.
"Baki ganshi b ne yanzun ya tafi", na fada can da raunanniyar muryata.
"Ba kowa Meenal ba kowa a nan Meenal tun dazun muke tsaye ke kawai muka gani kina faɗa".
 Rass naji gaba ya yanke ya faɗi kallon mutane nayi wanda duk hankali su yana kai na, "Kenan Aljanin ne", sha naji hawaye ya balle ba shiri suka antayo.

Yaya Miftahu ne yaja hannu na mukai waje, ita kuma Aunty ta dauko Bakir. Wani iri nake jina lamarin da bazan iya cewa gashi ba kawai dai naji ni kamar wata ƴar karamar zautacciya taya za'ayi haka kenan ni kadai nake ganinshi janye hannu na nayi daga riƙon da Yaya tayi min bayan mun fito wajen.
Baƙir na janyo dukawa nayi gurin har kasa ina hawaye na ce da shi, "gayamin Bakir baka ga kowa ba dazun da nake mgn?“na tambaye shi ne don son ƙara tabbatarwa amma ina zullumin jin amsar da zai bayar.
Kallon iyayenshi yayi a inda su ma suka zuba mishi ido don jin amsar da zai basu.
Saida ya dawo da dubunshi gare ni kana ce cikin harshen turanci dan da turancin nima nayi mishi magana.
"banga kowa ba amma naji kina magana ke".

Rass naji gaba na ya yanke ya fadi saura ƙiris na zube ƙasa Yaya ya tarbo ni, alert message ne ya shigo wayata wanda duk ya razana mu.
Wayar Aunty ta amsa ta bude sakon.

" _MEENAL KIN KASA FAHIMTA NE KAUNAR KI FA KAWAI NAKE YI ZAI FI MIKI KI SO NI MA, DAN NI KULLUM KARA SONKI NAKE YI, KARKI MANTA DA WANNAN BAZAN TAƁA

BARIN KI BA HAR SAI KIN SO NI TUN KAFIN HADUWAR MU TA GABA KI FARA SO NA ZAI FI MIKI DOMIN HADUWAR BA ZATA TAƁA YI MIKI DADI BA, YA KUMA ZAKI TAFI BAN GA FUSKARKI BA BAKI GA TAWA BA JUYO KI KALLE FUSKAR ABUN ƘAUNAR KI KI KUMA AJIYE FUSKAR CIKIN KWAKWALWARKI DA TUNANINKI"._

Da ƙarfi Aunty ta karanta sakon dago kai na nayi domin na kalle Aunty wai cikin rashin sa'a ko na ce aljanan ce ya kai idona can bayan motar ta mu.

"Waaa... innnahuuu... Sulaimanu..... ".

Diff maganar ta yanke, wanda daman ba fitowa tayi ba iyakarta maƙogaro.
Jiki na ne ya hau rawa yana karkarwa fiye da shekaranjiya,  sanyi kawai naji ta ƙasa na wanda hakan ya tabbatar min na kuma.  kafafuwan nawa ma karkarwa suke yi, duk ilahirin jiki na ma rawa yake yi.
Na kuma kasa dauke idona daga gareshi a inda shi kuma yake sakar min wani irin kyakkyawan murmushi amma a gareshi.

Ganin halin da nake ciki ne yasa suka juyo dan ganin abunda nake gani amma wayam basu ga kowa ba, gashi dai ni suna ganin alama ina ganin wani abu.

Janyo ni Yaya yayi ya tura ni cikin motar Aunty,  tayi saurin shiga bayan ita da bakir jan motar yayi da gudun tsiya ya bar gurin. A inda ni kuma har yanzun hotonshi bai ɓacewa gani na ba idona fuskar shi kawai yake hasko min yana sakar min murmushi.

Duk jijjigar da Aunty ke yimin a banza ban ma san tana yi ma.
Sai can har mun isa gida ban ma san mun kai ba sai da muka isa tsakiyar falon sannan na farga a tsorace.

"Aljani ne Aunty Wllh aljnai ne na shiga uku na mutu!".

Aunty n ita kanta ta ruɗe ta gigice ta ma rasa abun da zata yi kawai dai riƙe ni take yi.

Muna nan tsaye a rude bamu ma san da fitar Yaya ba sai jin da muka yi an kwala sallama sannan yasa muka kai duban mu.

"Ruƙiyya za'ayi miki MEENAL idan ma aljanni ne zai rabo da ke".

Har maganar tawa tana hardewa gurin faɗin, "To to!'
".

Gaban malamin naje da sauri na tsugunna jiki na sai faman rawa yake yimin".

" Ayi min rukkiyar!".

da rawar naki na ce.

Murmushi Malamin yayi shi da wanda suke tare dan ta basu dariya ma wai ayi mata rukiyyar, zama suka yi akan kujerar daga can.
Ganin sun yi nisa da ni yass na tashi ina rawar jiki na matsa kusa da su gaff na tsugunna.

Murmushi suka yi a karo na biyu, cikin dattako malamin ya ce, "To MEENAL za'ayi miki ki kwantar da hankalinki yau zai bar jikinki gaba daya".

Naji sanyi a rai na, amma dai na ƙagara ayi na huta ya fita daga jiki na na huta.
Kallon su Yaya yayi yace, "Ku zauna".
Alama Aunty tayi wa ƴar aikin gidan ta ta janye Bakir su bar gurin. Zama suka yi su ma jiki a mace musamman ma Aunty Sadiya.

Wata gorar ruwa malamin ya ciro a yar jakarshi har ganin nawarshi nayi gurin bude gorar na ƙagara ya watso min ruwan na fashe da ihun da naga ana yi.

Basmala yayi bayan yayi yan tufe-tufenshi cikin ruwan ya watso min dauke numfashi nayi jin sanyin ruwan nai shiru ina jiran sakamako na kuma runtse idon gama yadda duk abunda zai faru ma ba zan gani ba.

"MEENAL Meenal! malamin ya kira ni".
Ban san lokacin da nace na'am ba sai jin sautin da nayi ya fito dan bude ido nayi naga ko wani abun ne.

" Meenal ke ce?".

"Eh ni ce Meenal".

Na bashi amsa a takaice.
Kallon wanda suke tare yayi yai mishi alama, naga ya fito da littafin Allah littafin me girma da

daraja kariya waraka magani ga duk wani abu a duniya, kogin azava a gurin shaidanun aljanai........

~_Mrsbalarabe_~✍🏼

*ƘAUNAR ƁOYE!!!*
_(THE SECRET LOVE!🖤)_

*Fatima Batula✍🏼*

_Wattpad:mrsbalarabe._

*Dedicated to my Anup(my happines) Allah ne kawai yasan irin son da nake yi miki, ke abun so ce dole duk wanda ya raɓeki ya soki, baki na bashi da kalaman godiya da nuna irin matsayinki a gurina sai dai kawai na ce ke ta musamman ce a cikin rayuwa ta, Allah yabaki Ify ya baki miji na gari. Amin thumma Amin.*

_Page_

_7-8_

✍ *✍ Ġ̓Ȯ̓Ŀ̓Ḋ̓Ė̓Ṅ̓ Ṗ̓Ė̓Ṅ̓ Ẇ̓Ṙ̓İ̓Ṫ̓Ė̓Ṙ̓Ṡ̓ Ȧ̓Ṡ̓Ṡ̓Ȯ̓Ċ̓İ̓Ȧ̓Ṫ̓İ̓Ȯ̓Ṅ̓* ✍✍

*wє αrє вєαrєr's σf sσ gσldєn pєn*
*wє wrítє αssídíσuslч pєrcєívє nσ pαín,*
*sσ mαgícαl σur crєαtívє gσldєn pєn* ✍ *,вєhσld σur wσrds.α prσduct σf σur pєn* *,sαvσur σur wσrds, fσr ít wíll* *cαusє чσu nσ pαín.*

*Yadda Annabi, Tsira Da Amincin Allah Su Tabbata A gareshi, Yake Kirga Tasbihinsa.*

Daga Abdullahi bn Amr, Allah ya yarda da shi, yace; Na ga Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, yana kirga tasbihi da (yatsun) hannun damansa.

*INA MASOYAN LITATTAFAN KUNGIYAR GOLDEN PEN?*

*NESA TA ZO KUSA, TUNANIN RASHIN SAMUN NEXT PAGE YA ƘARE!.*

Kasance mutum na farko da zai fara karanta sabbin littattafan marubutan mu, a duk lokacin da muka yi typing. Kina/Kana iya samu, ta wannan damar ce kawai idan ka bi wannan links tare danna *LIKE* a shafin mu na Facebook zaka/zaki iya samun cigaba ko kuma ki samu duk littafin da kike buƙata namu daga farko.

https://www.facebook.com/Golden-Pen-Writers-Association-102095951667849/

Sai kun zo, kar ku manta a koda yaushe comments da sharhin ku yana ƙara mana ƙarfin gwiwa a wajen rubutu mai yawa.

_*Bismillahir~rahamanir~rahim*_

Duk wata ayar ruƙiyya dake cikin alƙur'ani ba wacce basu karanto min ita ba, ni kuwa nai lamo sakon baya sakon yace MEENAL ke ce nace eh ni ce.
Yace da Aunty ta kawo burner za'a kunna hayaƙi sannan ta kawo bargo.
Rufe ni aka yi da bargon bayan an zuba hayaƙn ya tashi, dayake nima ina so shiyasa nayi lamo a ciki duk yadda yace nayi, nayi wai ni Aljannai.
Na fi minti uku sannan aka buɗe ni, na fito duk nayi zufa, bayan wata lafiya da naji inaji ba abunda nake ji a jiki na.
"MEENAL baki ji komai ba".
 Kallon shi nayi murya zaun nace, "Banji komai ba".
"Ko ciwon kai?"
"Eh!
Lumfasawa yayi sannan yakai dubanshi gurin su Aunty Sadiya," To a zahirin gaskiya yarinya nan bata tare da wani aljanni sannan kuma ba aljannin da yake biyayyarta dan daya kawo kanshi, duk wani abu nayi amma sam ba ko alamar aljannai a tattare da ita".

Ni wllh zai fimin ma da yace aljannin ne, to yanzun da bashi ba ne waye? ina kawai dai bai gano ba ne shi  kuma ba zai iya cewa bai gano ba kar mu raina iyawarshi abunda na barwa raina kenan.
Ita kuma Aunty Sadiya da sai jinjina kai kawai take yi, daman tasan abunda zai faru kenan dan zu gaba daya zuri'ar su aljanni bazai iya shiga jikin wanin su ba, to amma abun da ruɗarwa.

Ina jinsu suna  firar cewa ba aljanni b ne mutum ne kawai yana son tsorata ni ne ta tashi nabar gurin nai ɗaki na, jiki na a jiƙe da fitsarin da nai tayi bayi na shiga na sakarwa kai na shayaaa.
Ina tunanin taya zai kasance mutum anya kuwa ina gaskiya bazai taɓa kasancewa mutum ba ina?? dole na je gurin malamin gaskiya daman yan Lagos akwai wani malamin arziki ne me ilimi.... tunani dai iri-iri nai ta kawo wa a rai na har na fito daga bayin nazo na shirya ina cikin

shirin ne Aunty Sadiya ta shigo zama tayi kan kujera har na shirya sannan nazo nima na zauna.
"Me kike tunani? ta jefomin tambayar ban kalle inda take ba na ce," malamin ƙarya ne bai iya komai ba kawai zan koma gida naje na samu musu ruƙiyar gaskiya".
Dariya Aunty Sadiya ta fashe da shi, kallon ta nayi rai a ɓace.
Yaya Miftahu ya shigo, "Honey yadai meye faru?"
"Honey kaji abunda MEENAL ta ce kuwa?"
Tashi nayi a fusace," Idan na bar muku gidan sai kuyi ta dariyarku daman ai saida Maama ta ce min bazan ji dadi ba nace zan zo a haka... "Nai ta mita duk na sauke musu guntun haushin da nake ji.
Da ƙyar suka iya shawo kai na na fasa, ni daman haka nake saurin hawa saurin sauka.
Da lallami da ban baki suka ban hakuri akan idan har wani abu ya kara faruwa sai a nemi wani malamin, jinsu kawai nayi dan na saka wa raina ƙara ganinshi zanyi.

Haka muka wuni ranar a gida muna ta fira ganin abun nasu yayi yawa bazan iya cigaba da gani ba dan zai su suka na rasa kunyata yasa naja Bakir mukai daki na.

Na dade sosai a falon ina kallo dan su suna da nasu a daki kuma Yaya baya barinta da dukan alama maye ne, sai can na tashi na koma ɗaki.
Tun asubar fari na tashi lumi hankali kwance naje nayi sallah ban koma barci ba alqur'anin wayata na bude na fara bita.
Da yake yau ta kasance Monday ranar aiki. Gurin bakwai saura na tashi zan koma Aunty na ta shigo cikin shigar gayan aikin ta. "Amma Aunty wannan bai dace ba wllh kalli fa shigarki yanzun kuma a hakan zaki fita gaskiya da sake".
"To ya zanyi MEENAL dokar gurin aikin kenan ba yadda zanyi ne".
"To ba sai kibar aikin ba ba wani ne sai shi".
"Hmm MEENAL kenan ba zaki gane ba, bari naje Honey na jira na sai mun dawo daga nan zamu sauke bakir a makaranta," tana idasa faɗa ta fita da sauri karewa shigar nayi kallo matsatsen wando ne a jikinta da ƙaramar riga sai hula da tarkacen kayan aikin.
Wani uban tsaki naja wani irin bala'i ne wannan mace yar musulma da shigar arna kai, duk sai naji na ƙara tsanar garin da duk mutanen da ke ciki ma.
Komawa nayi na kwanta naita barci gurin goma na tashi na fito gidan wayam ba kowa sai naji wani iri kenan haka zan dunga zama ni kadai kamar maiya, ga me aikin arniya ni kuma na tsane Arna wari ma suke min vazan iya sakewa da ita ba balle ta shafamin ƙazanta.
Haka na wuni ranar zungur ba dadi bani daki bani falo nayi barci na tashi nayi na tashi.

Sai dare suka dawo lokacin har bakir yayi barci ma, a tsatsaye muka gaisa suka wucewarsu daki, ta nan kuma suna burge nidaki daya suke kwana abunsu.
Haka ma washegari.

Tare suka leko harda bakir sukai min sallama suka wuce. Kullum haka nake wuni ni kadai zungur a gida gashi ina jin tsoron fita duk sai naji na gaji gashi ni ba saurayi ba, ba abun kuma na kira mama ba, abu duk ya hademin goma da ashirin.
Haka kullum nake wuni a gida, yau dai na gaji nace duk abunda zai faru ya dade bai faru ba sai

na fita abuna, na ko shirya na sa direba yaja ni cikin gari. Abun har ya ban mmk dan ban taɓa dauka  har naje na dawo ban ga aljani na ba.

Haka har yau sati na biyu a garin Lagos wanda na zo dominsu basu takai na dan wata rana ma ko salamar basu yimin ranar da suka yi latti da dukan alama dai gurin aikin nasu suna da zafi duk da basu gayamin ba amma nasan cewa me kamfanin ƙasurgumin  arne ne, kuma kamfani daya ne ita Aunty a ƙaramin kamfanin take aiki shi kuma Yaya a Babban yake aiki a duk da ni ras'ayina irin nawa na hausawa ne amma hakan bai hana naji suna burgeni ba.

Ni da aljani na kuwa har yanzun shiru, nakan karanta sakon shi nayi dariya abu na kuma sai naji ina fatan kara haduwa da shi, gashi shiru kike ji dan yanzun kullum sai na fita da idan na fita bana sauka ko ina har na gaji da yawon nace a dawo gida amma yanzun kam sauka nake yi naita yawo guri guri yau tsabar karan bani na cewa nayi yakai ni shoprite din na muka hadu har gurin naje amma shiru bashi va lamarinshi.

Ni har na fara mantawa da shi ma, hutu kuwa nayishi har na gaji da yinshi sai kuma naji garin ya fita rai na dan bani da me tayani fira bani da ɗan fira, ina jiran ranar Lahadi tayi ranar suna gida nace musu ni gida zan tafi, dan yanzun har ranar sati fita suke yi saidai bada wuri ba kuma su dawo da guri.
Kasancewar a babban famfani ne dan duk Lagos kowa yasan da kamfanin me kamfanin hamsin me kudi ne, dan yana da kamfani iri daban-daban.

Yau ta kasance ranar ladi da wuri na fito ban bi takan su ba nai gurin Bakir na shiryashi da kai na bayan mun gama lokacin gurin goma saura sannan muka fito.

"Aunty tsiwa fitsari wai ina aljaninki yake ne? naga kwana biyu bai kawo miki ziyara ba".
Yi nayi kamar ban san da wacce yake mgnr ba, nai zama na na fara bawa Bakir abinci.
"Zan koma gida na gaji da zama tunda ku rayuwarku haka take bazan iya ba gurin Maama zan koma".
"Haba Auta kiyi hakuri daman jiya da daddare muka yi mgn da Honey akan haka zaman gidan zai miki yawa to gurin aiki na za'a ɗibi'i ma'aikata to na tura application letter jiyan".
Zaro ido nayi, "Me gurin aikin ku na ce ina so ne, ki janye ma tun wuri dan bana so".
  "Haba MEENAL ya zaki ce haka dabara ce fa kinga kullum sai ku dunga fita tare ku dawo tare hakan zai fi da zaman gidan da kike yi".

"Hm nidai Yaya gaskiya bazan iya ba," abunda yafi ban haushi shi ne wato duk na rasa inda zan fara aiki sai a nan na baro arewata na zo nan idan aikin nake so na zauna acan mana, ni sam bana wani sha'awar fita aiki kamar wata namiji.
Da kyar da ya Allahu suka shawo kai na na yarda shi ma da sharaɗin na wata biyu kawai zanyi na ajiye na koma gida, na kuma yardan ne dan idan na cigaba da zama cikin kaɗaici gajiya zanyi n koma gida Maama kuma dariya zata yimin daman tace bazan iya yin ko wata ba, shiyasa kawai na aminci har ga Allah badan na so ba.

Washegari ranar Monday duk suka wuce kamar yadda suka saba haka nai ta faman xama ni kaɗai abun takaici nai wata irin qiba ta hutun bala'i.
Yau laraba ina zaune gurin karfe tara na dare ina kallo a falo sai ga su nan.
"Sannun ku da zuwa yau kun dawo da guri".
Washe baki Aunty tayi, "Eh yau shugaban mu ya sallame mu da wuri ne, amma MEENAL gaskiya ke me sa'ar gaske ce", tana kare mgnr ta kai ga zama kusa da ni.
"Na me kuma?"
"Wllh MEENAL ba wanda ya taɓa zama matsayin Sakatariya a kamfanin mu ba tare da yayi wani abun ba ko cin hanci ko yai asiri kuma ba ma kai tsaye haka ba, amma ke *MR DANIEL* da kanshi ya baki wannan matsayin wllh da na gani sai da naji wani irin luu zan faɗa tsabar mamaki na rasa dalili ikon Allah ne kawai yasa amma abun da mamiki shi da sam baya son m.... "
Ban bari ta ƙarasa ba na katse ta," Hm ni bar gayamin meye nawa wllh ina ganin ba zan iya va zan guduwa garin mu zanyi".

"Gaskiya MEENAL sa'arki tayi yawa farko dai ga masoyi ya rako ki har nan, sannan kuna ga babban matsayi a gurin aiki ina ji a jiki na akwai wani abu".
"Gaya mata dai Honey abun da mugun mamaki wllh".
"Sai da safe! ina faɗa na tashi nabar gurin sai naji kamar na ce na fasa, dan ban hango alkairi a cikin wannan aikin sam ni dan ƴar uwata kawai yasa na amince amma da ko kusa, gashi abun jin ma gurin duk arna ne ni da ban son mu'amala da su.

Dariya suka yi sannan suka wuce dakin su.
Asubar fari naji aunty tana tashi na, "MEENAL dan Allah ta ki shirya kinga yau zaki fara zuwa karki makara".
Bata barni ba saida ta tabbatar na tashi, na shiga bayi sannan ta fita ita ma ta je ta shirya.
Tunda na tashi nake jin ƙirjina na bugawa kamar zai fashe na kuma rasa dalili da kyar na fito na tada sallah bayan na idar nazo gaban mirrow tunanin kayan da zan saka na fara yi, nasan idan na saka riga da siket abun kallo zan zama kuma ni su ne kayana. Tashi nayi na janyo wata duguwar riga navy blue ithopian abaya ce me kyawun gaske tasha adon stone na zura ta, kamar yadda na saba yiwa fuskata Light makeup yanzun ma shi nayi, ni kaina nasan nayi kyau na dauko farin kyale nayi rolling din kai na da shi da farar jakata na saka takalmi na fari me dan tudo.
Tashi nayi tsare ina karewa jiki na kallo ba laifi shape dina bai fito sosai ba, turare na fesa bayan na mulke humra a jiki na.
Ina tsayen Aunty ta shiga.
"Waw MEENAL kin hadu zaki kwashi ƴan kallo yau a office kuwa".
Ni daman akwai ni da basarwa na ce, "Naje mu je", nai gaba abuna kamar wata wacce ta kware gashi ina jin gaba na faduwa.
Ina isa harabar gidan motar su Yaya na fita.
Gaban motar ta na shiga, ita ma ta shigo ita zata ja motor, bude mana get me gadi yayi muka fice daga cikin gidan gabana na kara tsananta faɗuwa.
"MEENAL! Aunty Sadiya ta kira ta cikin kulawa.

Yadda naji ta kiran yasa na amsa nima cikin kulawa domin irin wannan kiran tana yimin shi ne idan zata gayanin mgn me muhimmanci.
" MEENAL ki kula sosai nasan zaki ga bambanci sosai  amma ki kula sosai cikin arna zaki shiga tsamo-tsamo kuma yare, ki kama kanki abun jin ma ina fatan Allah yasa Sir *DANIEL* ya barki ki shigaba da saka irin kayan nan, me kamfanin baya son musulunci baya son musulmai, ban ce ki juya ki nuna ke ba musulma va ce no ko baki ce ba an ganshi a fuskarki amma ki kula ki kama kanki".
Tashin Hankali tabb aiki ja, "To me yasa Aunty Meyasa sai nan baya son musulunci baya son musulmai kan me to? wani irin kamawaye kike nufi nayi? Aunty kin san ni kuma kin san abunda zan iya?.
" Ohh more no taya zan saka ki fahimta MEENAL".
"Bana jin zan fahimta Aunty wllh idan har sai na koma yin shigarsu arna sai nayi basajar ni wacece sannan zan cigaba da aikin wllh a shirye nake na juya tun yanzun bazan iya b sannan kuma....
Ƙii naji alamar tsayuwar moto kai duba na nayi a inda naji wani irin rass saida murfin zuciyata ya rufta ciki, ambaton Allah na fara yi a zuciyata ya tsare ni ya kuma kare ni.
Sauka tayi, ganin hakan yasa nima na fito.
*REAL FUTURE HOPE IND. LTD.*
FUGULE ESTATE, ISHERI IJEGUN LAGOS NIGERIA.
nai tuzali ta sunan a can saman kamfanin me bene kusan shidda.
Dauke kai na nayi na cigaba da kallon gurin to nidai ba maƙiyiya Allah bace da sai nayi ƙarya nace gurin bai yi kyau ba, amma da yake bashi a rai na sai naji be min kyawun ba.
"Muje! Aunty Sadiya ta ce min da yarensu da turanci binta nayi a baya ina kallon ikon me sama. Wllh idan ba kasan hasken musulunci da ke baiyana a fuskar musulmai ba, bazaka taba cewa Aunty Sadiya musulma ba ce.
Jiki na naji ya mutu libis ga shi sai famam kallo na ake yi, kamar a hadiye ne left hawa na biyar muka hau.
Waiyo ni MEENAL ina zan saka raina kallo ne ya dawo gare ni ita kuwa Aunty Sadiya sai gaisawa take da mutane cikin sakin fuska dan ta saba da su sosai shekara biyar tana aiki a kamfanin.

Da yake akwai kama sosai a tsakani na da Sadiya shiyasa mutanen duk suka gane ni, gashi duk sun san ni ce yanzun sabuwa sakatariyar Sir Daniel, kallon mamaki suke yimin a inda wasu ke raya ma ransu tafiyar tamu tare baza ta yuwa ba domin baya son musulmai kuma ni daga ganin alama musulmace ta kwarai wacce ke kishin addininta, wasu kuwa suna raya tafiyar zata so daya dan ina da kyau ga sura shi kuwa mutum ne mayen me kyau mayen mata ne na karshe karshe,wasu kuwa su ce idan na bada kai zan zauna Ify naci riba nida yayata duk da kasantuwar ni musulma ce, idan kuwa naƙi na ja mana wahala.

Bin bayan ta nayi zuwa cikin office din da naga ta kunna kai ina shiga na tura kufar jiki na mace , zama taje tayi akan kujerarta ni mamaki ma take ban.
"Aunty bazan iya yin wannan aikin ba".

"Zaki iya ya zama dole ma, MEENAL kenan taya zan fahimtar da ke sa'ar da kika yi a gurin nan ki daure zKi iya ba ina nan ba".
 Shiru nayi bayan na zauna naji duk rayuwata ta jagule na rasa abunda ke min dadin ina zan saka kai na ni MEENAL.
Dafa ni Aunty Sadiya tayi cikin sanyin murya da sigar ban baki ta ce, "MEENAL karki ji komai zaki saba nima haka naji da farko ba kuma abunda zai faru ba ina nan ba, kuma ki kula dan canji zaki ga canji zaki ga mutane iri daban daban masu halaiya daban daban sai kin lura kin kula sannan".
Daga mata kai kawai nayi.
"Good my sister u are smart girl u know how act".

Nidai lamo nayi ina jin wani iri taya zan saba cikin mutanen da ba ƙabilata ba ba kuma addini na va, anya kuwa zan iya irin wannan sabawar kuwa??

Waya naga ta kira tana ajiye wayar wata ƙasurgumar arniya ta kunno kai cikin offiice din kallo daya zaka mata ka tabbatar wannan ko a arnan ma ita ƙasurguma ce.
 Wani irin kallo naga tayi min mara kai, ban san lokacin da na maida mata raddinshi ba, dan ni ban da hakurin wannan.

Da turanci sukai mgn akan ta tunamin yadda aikin yake da office dina da komai da komai na kamfanin.
To tace da ita kawai ta kalle tace na biyo ta tare da, tashi nayi jiki a mace na bi bayanta har na kulle kofar aunty ta tsayar da ni wai muje tare.
Naji dadi kuwa ina ma da a office daya ne zamu yi aikin nasan da na rage jin wani abun.
Yawo sosai muka yi duk idan muka je suna sunanin yadda komai yake da yadda ake amfani da shi da komai da komai ina fahimta dan ba ƙarya ni gorowace by nature not by son a iya, duk inda muka gifta naji ana ta mgnata akan sa'ar da nayi wasu naji suna cewa anya da akwai wata a ƙasa ba yadda za'ayi Sir. Daniel ya dauke ni aiki, ohoo dai ni duk wannan maganganun basu gaba na hakan yasa ban basu muhimmanci ba, daga su har ogan na su.
Duk mun zagaya ko'ina yanzun guri daya ya ragemin offiice dina wanda sai naje gurin oga sannan zan shiga nawa office din, tunda muka nufa office din naji faduwar gaba na ya tsananta na jure na cigaba da tafiya ina ambaton ubangiji na.

Tiny suna da naji Aunty ta kirata da shi kenan ita ce ta fara knocking din kofar a hankali tun tayi sau daya ta tsaya gashi dai ba'a bamu izinin shiga ba, a rai na nace bai ma ji ba, gashi dai naga sai tsayuwa muke yi ni har na fara gajiya da tsayuwar ma har na bude baki zanyi mgn taji ance, "u can come".
Ban wani ji ba illa dai kawai nace naji anyi mgn amma banji abunda aka ce ba, na gane cewa yayi a shigo ganin ta murɗa kofar ta shiga.
Bin bayan ta nayi dan Aunty ta koma gurin aikinta office dinta.

Dan taɓe bakin nan nayi da na saba, ganin yadda ya bawa kofa baya kenan mu ma bayan ya

basu. bayani tayi mishi na kan cewa ni ce sabuwar sakatiyar na zo, tana gama faɗa ta juya.
To ni me zan tsaya yi juyawar nayi, har nayi taku ɗaya na tsaya cikk tare da yin nazarin kamar fuskar aljani na na gani, a zabure na juyo.
Ni MEENAL taya zan iya mantawa da wannan fuskar ai har abada bazan taɓa mantawa da ita ba.
"Aljani na! na furta can ƙasan maƙogaro.....

~Mrsbalarabe~✍🏼

*ƘAUNAR ƁOYE!!!*
_(THE SECRET LOVE!🖤)_

*Fatima Batula✍🏼*

_Wattpad:mrsbalarabe._

*Dedicated to my Anup(my happines) Allah ne kawai yasan irin son da nake yi miki, ke abun so ce dole duk wanda ya raɓeki ya soki, baki na bashi da kalaman godiya da nuna irin matsayinki a gurina sai dai kawai na ce ke ta musamman ce a cikin rayuwa ta, Allah yabaki Ify ya baki miji na gari. Amin thumma Amin.*

_Page_

_9-10_

✍ *✍ Ǵ́ŐĹĎÉŃ ṔÉŃ ẂŔÍŤÉŔŚ ÁŚŚŐĆÍÁŤÍŐŃ* ✍✍

*wє αrє вєαrєr's σf sσ  gσldєn pєn*
*wє wrítє αssídíσuslч pєrcєívє nσ pαín,*
*sσ mαgícαl σur crєαtívє gσldєn pєn* ✍ *,вєhσld σur wσrds.α prσduct σf σur pєn* *,sαvσur σur wσrds, fσr ít wíll* *cαusє чσu nσ pαín.*

*Yadda Annabi, Tsira Da Amincin Allah Su Tabbata A gareshi, Yake Kirga Tasbihinsa.*

Daga Abdullahi bn Amr, Allah ya yarda da shi, yace; Na ga Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, yana kirga tasbihi da (yatsun) hannun damansa.

*INA MASOYAN LITATTAFAN KUNGIYAR GOLDEN PEN?*

*NESA TA ZO KUSA, TUNANIN RASHIN SAMUN NEXT PAGE YA ƘARE!.*

Kasance mutum na farko da zai fara karanta sabbin littattafan marubutan mu, a duk lokacin da muka yi typing. Kina/Kana iya samu, ta wannan damar ce kawai idan ka bi wannan links tare danna *LIKE* a shafin mu na Facebook zaka/zaki iya samun cigaba ko kuma ki samu duk littafin da kike buƙata namu daga farko.

https://www.facebook.com/Golden-Pen-Writers-Association-102095951667849/

Sai kun zo, kar ku manta a koda yaushe comments da sharhin ku yana ƙara mana ƙarfin gwiwa a wajen rubutu mai yawa.

_*Bismillahir~rahamanir~rahim*_

Komai nisan shuɗewar lokaci banjin zan iya mantawa da wannan halittar wacce ta kafa tarihi a kundun rayuwata,hotonta ya shiga kwanyata ya zauna tamkar rubutu akan dutse,ai faɗa ma ɓatawa ni *MEENAL* taya zan manta da shi wanda ban sanshi ba sai dai kawai na iya kiranshi da *ALJANINA* zuba mishi milky eyes ɗina nayi tunda nake haɗuwa da shi ɓan taɓa ganin yayimin kyau da cikar haiba ba irin yau ban wani damu ba sanin iya surkulen aljani.
Kaɗan- kaɗan nake jin zuciyata na bugawa a inda tunani na ya shiga karantomin abubuwa iri iri,cigaba da kalle shi nayi tsaf ƙiff na kafe idanu na akan zarɓeɓiyar saƙar kurus ɗin dake maƙale a wunyanshi.
Nufarshi nayi a fusace cikin ɗaga murya da masifa irin tawa nahau faɗin,"Yau kuma da wannan aka zo?ohoo ma zuwanka kafiri ko musulmi bai dame ni ba,kawai yau ina son insan kai waye dan na gaji da barazanar da kake yimin ayita ta ƙare soyayya dai nace bana yi kuma ko kai ne sarkin aljannan kafirai bazan soka ba,dan haka ayita ta ƙare kawai....."cike da tsiwa nake mgnr murya kuma a ɗage.

Tundaga halittar yatsun kafafuwanta Daniel ke binta da kallo karo na farko ga baƙuwar fuska a gareshi yaji yana son kallonta bai taɓa ganin ko da me kama da ita ba a duniyarshi,tunda suka haɗa ido yaji ya kasa ɗauke idonshi akanta,shiruu yayi tare da zubawa bakinta ido yana kallon yadda take sarrafa su duk da baya jin abunda take faɗa amma ya fahimci faɗa take yi,murmushi kawai yake saki a fakaice Yadda ta ke faɗa ko da me meye confidence ɗinta ya matuƙar burge shi yasan shi me kwarjini ne ya yarda da wannan ba duk mace ba,kunsan duk matan da yake

hulɗa da su basu iya kallon cikin idonshi su gayamishi ko da kalmar soyayya balle kuma ita da yake ganin kamar faɗa take yi mishi,ta burgeshi for the first time yaji takai inda mata da yawa ba su ko nufar gurin balle su burgeshi .
Ganin yadda yake ta sakin mata murmushi yake yi ya ƙara ƙular da ita.
"Dariya ma nake baka dole zan baka dariya tunda ka maida ni mahaukaciya yau sai na tuna maka asiri",daa ƙarfin zaxxaƙar muryata ta ce,"ihhhhu jama'a help!help me!!!
Runtse ido yayi a yayin da yaji wani irin abu chuuu ya duki dodon kunnuwanshi shi mutum ne mara son hayaniya a rayuwarshi duk wanda yasanshi yasan hakan gashi yana da matslar kunne baya son ayi mgn da ƙarfi sam yana jin kamar laudspeak ake zuwa daidai kunnuwanshi ana yin mgnr da ita Kasancewar ba wani nisa a tsakanin mu da ofisoshi ne yasa duk suka jiyo ihu na,karo na farko kenan da suka taɓa jin irin haka ta faru duk abunda yayiwa macce bata mishi ihu balle ta nemi taimako shiyasa duk suka ruɗe jin irin ihun da take yi.
Aunty Sadiya kuwa da sai da ta ƴarta wayarta dake hannuwanta a zabure ta fito da gudu ta nufi office ɗin ganin hakan yasa ssuran ma'aikatan biyo bayanta dan ganin abunda ke faruwa.
Shi kuwa Sir Dany tunda ya rufe dukan kunnuwanshi da hannunshi ya kuma runtse ido amma ina hannunwanshi sun kasa tsaida muryata ga shiga cikin kunnuwanshi suna dukanshi.
Ni kuwa ban tsaida yin ihuu na ba saida naga mutane sun shiga office ɗin dam sanan na tsaya.

Juyowa nayi na kalle mutanen da ke ciki Aunty Sadiya kawai nafi buƙata na gani dan ta shaida yau dai asiri ya tuno yau kowa ya ganshi,juyowa nayi domin na kuma kallonshi naga yana nan ko yabi iska ya gudu.Tasss kake ji.
Tagaga naji tare da jin wani irin shuuuu cikin kunnuwana,wani irin wawan mari yabi kyakyawar fuskarta da shi,ba wanda bai ji marin ba jin yadda sautin ya fita da ƙarfi gashi murjajjen namiji.Aunty Sadiya kuwa da tana saka ƙafa yana sauke marin taji wani irin raɗaɗin zafi ya saki ta runtse ido tayi.
Ni kuwa da faɗar azabar zafin marin daya kwasamin ɓata lokaci ne ma domin ɓoyaƴƴen abu ake baiyanawa baiyanne kuwa ba ta yadda za'a baiyana shi,kowa yaga irin yadda na tafi tagaga zan faɗi har russunawa nayi amman ban kai ƙasa ba tsabar azaba harda jiri naji ya ɗibeni yuuu gashi marin ta gurin kunnuwa na ya ssukemin su yasa naji shuuu xan iya cewa dodon kunne na ya samu matsala bani ba kara jin mgna a duniya.

Kama gurin nayi ina jina wata iriii na kuma kai duba na gareshi dan son tabbatar da abunda nake ji kamar a mafarki.
"How dare u! u rascal wacce irin banza ce ke dabba mara hankali mahaukaciya wawiyace waya kawomin ke mahaukaciya?"yadda yake mgnr cikin ɗan ɗaga murya ya tabbatar musu daya fusata dan sun san baya ɗaga murya haka.

Wani irin kallo yayi musu kafin cikar saƙon duk sun watse banda Aunty da take cikin kwatankwacin halin da nake ciki.
Runtse idona nayi da tuni sun ɓalle da ambaliyan wasu irin ruwa masu azabaɓen zafi nayi,zuciyata naji tayimin wani irin ɗaci wanda nake jinshi har maƙogaro na,jin waɗan nan munannan kalamai wanda basu da na biyu yasa na tabbatar da cewa ban rasa ji na ba,saida kuma yanxun kai na ya kulle kwanyata ta tsaya cik tayama zan iya ɗaukar wannan baƙon lamari

daga Meenal ina ƙaunarki ki so ni,komai naki burgeni yake yi Meenal wllh ƙaunar gaske nake yi miki wanda ba wanda ya taɓa yimiki irin ta,sai kuma wani azabaɓɓen mari me matukar zafi mahaukaciya,dabba,hajila wawaiya,runtse ido nayi a daidai nan a tunani na wasu irin hawayen azaba suka kwaranyomin suna rangaji suna wanke min fuska tausayin kai na ne ya mugun kamani.
Cikin sanyin murya da yin ƙasa da kai Aunty sadiya ta ce,"Sorry sir!
Ta jani muka bar office ɗin binta kawai nake yi,su kuwa mutane sai gulmar mu suke yi,gurin parking muka je ta ja motor bata ce min komai har muka isa gida nan ma ita ce ta fito da ni daga cikin motor ni kuwa da har lokacin hawaye nake yi,riƙe ni tayi muka isa tsakiyar falon kana ta rungumeni ta fashe da kuka,sautin kukan ta ne ya dawo da ni daga duniyar dana faɗa,nima fashewa da kukan nayi me ban tausayi na ƙara ƙanƙameta a jiki na.
"Shi ne fa shi nefa!cikin shashsheƙar kuka nayi mgnr.
Zaunar da ni tayi akan kujera ta tashi taje ta ɗaukomin gorar ruwa me sanyi ta kawomin,amsa nayi tasha dan ina da buƙatar sha ko naji ɗan sanyi-sanyi.
"Shi ne wa Meenal,"ta faɗa bayan ta zauna kusa da ni,ita ma idanuwan na ta sunyi jajir.
Ni da har lokacin hawayena basu ƙafe ba,gashi ina jin fuskata tayimin nauyi ina jin ta kumbura ne to ai dole dan ma ni jaruma ce da wata ce sai ta suma ga kukan da na sha.
"kin ganshi ne?"Na faɗa ina hawaye.
"Wake kike nufi Meenal Sir Daniel kike nufi wai".
"A'a aljani na baki ga marin da yayi min ba,"sai na fashe da kuka wannan halittar tsakani na da ita sai Allah ya isa ban yafe ba,domin duk ramuwar da zanyi bazan taɓa iya raba abunda tayimin ba.
Cikin rashin fahimtar zance na Aunty sadiya ta ce,"sir daniel ne fa ya mareki Meenal".
Girxiza mata kai nayi ina kuka abuna wato sai ya fito mita a matsayin oganta Allah ya haɗani da sheɗani.
Waya ta zo dubawa dan ta nunamin hotonshi bada gani ba,sai yanzun ne ma ta tuna da yadda tayi da wayar.
Tashi tayi taje ɗakin ta ban kula da abunda ta ɗauko ba inacan ina kuka na."Meenal kalli wannnan ne".
Tashi nayi daga zaunan da nake a tsorace nace ,"eh shi ne shi ne aljanin a ina kika sanshi".
Wata irin raguwar ajiyar zuciya Aunty Sadiya ta sauke zama tayi tare da kama kanta abun da ɗaurewar kai.
Nima zama nayi kusa da ita na dafa kafaɗunta ban iya cewa da ita komai ba.
Ɗagowa tayi muka kalli juna sosai,"Meenal wanan shi ne *DANIEL KRISTEN*  yaron attajirin ɗan kasuwar da lagos ke ji da shi bayarabe ne sanan kuma manyan kafirai maƙiya Allah,taya Daniel zai kasance aljanin dake bibiyarki ko mutum dai ma,bayan baya jin hausa ko kaɗan sanan kuma bai iya fadin ko zo na kashe ka ba da hausa,ke bai ma taɓa xuwa arewa ba,taya taya?sam baya son hulɗa da musulmai kamar mahaifinshi bazai taɓa kasancewa shi ba Meenal kowa yasan wanan irin wannan sanin d na gayamiki,"ta faɗa tana nuna shi a hoton da ke haɗe da mujalla.

Ban wani bawa kwanyata wanan damar ba balle ta buga haka ma zuciyata na samar musu hutu dan yin wannan tunain a daidai wannan lokacin daidai yake da tarwatsamin kai yahaifar min da

hawan jini.
Hawaye ne kawai suke ta faman safa da marwa a fuskats,na shiga uku ni Meenal wani irin lamari ne wannan Allah ka ɗauramin abinda yafi ƙarfina Allah,abunda nai ta rayawa kai na kenan a zuciya.
Rungume ni Aunty tayi na matukar bata tausayi xata iya cewa tun ƙuruciya rabonda ta ga kuka na,balle wannan yanayin Meenal jarumce me juriya da jan hali duk lamarin da ya sakata a wannan yanayin to tabbas da wani ne abun bazai kwatantu ba.
"Kiyi shiru Meenal ɗan Allah kiyi hakuri kin ji".
Abun kuka ya sameka ace kayi shiru to ya ake so kayi da ranka fitinar cikin ranka da ɓoye kuka ko me,kalamanta na nayi shiru tinzira ni ma suka ƙara yi na sake fashewa da kuka me cin rai da ban tausayi kukan da zan iya cewa duk tsawon rayuwata ban taɓa yin irin shi ba.
Na daɗe sosai ina kukan cikin haka naji wani irin barcin wahala na fusgata ganin hakan yasa aunty ta taimaka min na shiga ɗaki na,na kwanta ina kwanciya barci ɓarawo yai awan gaba da ni.

Aunty sadiya ta daɗe xaune tana kallonta daga bisani ta tashi bayan ta rufeta da bargo,office ɗin da ita ma bata koma ba kenan.
Sai gurin ƙarfe biyu da rabi na tashi da ƙyar na iya buɗe idanuwana tsabar nauyin kumburin da suka yi,ita kanta fuskata ta kumbura tai him da ita.jiki n ma ciwo yake yimin da ƙyar na samu na lallaɓa na faɗa bayin  ganin lokacin sallah ya wuce,wai tamkar bani ba dana kalli fuskata a madubi ta kumbra  nai wani irin muni yatsunshi biyar kuwa gasu nan a fuskata shafa gurin nayi wasu ƴan tsiraran hawaye suka gangaromin na takaici ba wanda ya taɓa yimin abunda wannan halittar tayimin a rayuwa,gasa jiki na na fara ina kuka ban yarda da abunda Aunty sadiya ke son gayamin ba na wannan ba shi ba ne wancan mutum biyu ne ko aljannai biyu anya kuwa,da gaske wannan baya jin hausa kuma bai taɓa zuwa arewa ba??shi kuwa wancan a kano na fara ganinshi da hausa raɗam a bakinshi kai ina dole da wani abu,to ko dan nace bana sonshi shi ne zai ɓullomin ta wata sigar.
Da wannan zancen na gamsu wato dan na ce bana sonshi shi ne ya bijiromin ta wannan hanyar tuno kalamanshi na ƙarshe nayi inda yske tabbatar da cewa kwara na fara sonshi kafin haɗuwar mu ta gaba idan ba haka ba abun bazai min daɗi ba Jinjina kai nayi,"ohho shi ne zaka birijomin ta haka to xamu ƙara haɗuwa ne,zaka gayamin kuma sai na rama marin da kayimin,"da ƙarfi nayi mgnr kamar yana gaba na.
Na daɗe sosai ina gasa jiki na,sannan na fito wata duguwar rigar na saka sannan na tada salla ina cikin yi Auntyna ta shigo zama tayi har na idar.
"Kin tashi Meenal ga abinci n kawo miki ki ci,ga magani ki sha nasanki da saurin zaxzaɓi".
Kusa da ita na zo na zauna na ɗauka ta koma gurin aiki gaskiya aunty sadiya tana so na so mugun so nafi komai muhimmanci a gareta nasan yadda take mugun son aikinta.
"Baki koma ba",n faɗa ina kallon fuskarta.
Buɗe robar man zafin tayi ta lakato ta shafamin a gurin daya barmin taɓon yatsunshi ni ba fara ba amma gurin yayi jajir.
"Oshhhh!
"Sannu!sai gobe zanje naji yadda ake ciki Meenal Sir Daniel bashi da mutuncin yin yafiya ga kowa,ina jin ƙarshen aiki na a kamfanin ne ya xo ƙarshe nima na huta".

Zuba mata ido nayi ina ganin yanayin da tayi mgnr da shi yanzon shikenan zanyi silar barinta gurin aiki,raurau nayi da ido xanyi kuka ta caraf ta ce,"No dont carry is all  my fault saida kika ce baki xo ba zaki iyaba na takura ki..."shiru tayi tare da sauke nannauyar ajiyar zuciya,flet ɗin abincin ta buɗe ta miƙa mata,"ki ci".
Ba musu na amsa naci kaɗan na miƙa mata ta miƙomin magani da ruwa na sha.
"Ki samu ki kwanta zaki ji daɗin jikin ki,"ta faɗa bayan ta gyaramin kwanciyar ta lullubɓe ni da bargo,rufe ido nayi badan ina jin barcin ba.
Ina son Auntina ina ma tana so na,bazan taɓa bari ta dalilina ta rasa aikinta ba.......

*#Comment*
*#Share*
*#Vote and like*
👏 *Please*

~Mrsbalarabe✍️~

Follow this link   https://chat.whatsapp.com/FUiDhNPMi2W2AKSovmsstj

*ƘAUNAR ƁOYE!!!*
_(THE SECRET LOVE!🖤)_

*Fatima Batula✍🏼*

_Wattpad:mrsbalarabe._

*Dedicated to my Anup(my happines) Allah ne kawai yasan irin son da nake yi miki, ke abun so ce dole duk wanda ya raɓeki ya soki, baki na bashi da kalaman godiya da nuna irin matsayinki a gurina sai dai kawai na ce ke ta musamman ce a cikin rayuwa ta, Allah yabaki Ify ya baki miji na gari. Amin thumma Amin.*

_Page_

_11-12_

✍ *✍ ĠŐĹĎĔŃ ṔĔŃ ŴŔĨŤĔŔŜ ÁŜŜŐĊĨÁŤĨŐŃ* ✍✍

*wє αrє вєαrєr's σf sσ gσldєn pєn*
*wє wrítє αssídíσuslч pєrcєívє nσ pαín,*
*sσ mαgícαl σur crєαtívє gσldєn pєn* ✍ *,вєhσld σur wσrds.α prσduct σf σur pєn* *,sαvσur σur wσrds, fσr ít wíll* *cαusє чσu nσ pαín.*

*Yadda Annabi, Tsira Da Amincin Allah Su Tabbata A gareshi, Yake Kirga Tasbihinsa.*

Daga Abdullahi bn Amr, Allah ya yarda da shi, yace; Na ga Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, yana kirga tasbihi da (yatsun) hannun damansa.

*INA MASOYAN LITATTAFAN ƘUNGIYAR GOLDEN PEN?*

*NESA TA ZO KUSA, TUNANIN RASHIN SAMUN NEXT PAGE YA ƘARE!.*

Kasance mutum na farko da zai fara karanta sabbin littattafan marubutan mu, a duk lokacin da muka yi typing. Kina/Kana iya samu, ta wannan damar ce kawai idan ka bi wannan links tare danna *LIKE* a shafin mu na Facebook zaka/zaki iya samun cigaba ko kuma ki samu duk littafin da kike buƙata namu daga farko.

https://www.facebook.com/Golden-Pen-Writers-Association-102095951667849/

Sai kun zo, kar ku manta a koda yaushe comments da sharhin ku yana ƙara mana ƙarfin gwiwa a wajen rubutu mai yawa.

_*Bismillahir~rahamanir~rahim*_

Daman barcin ba isata yayi shiyasa ina kwanciyar ya tafi da ni bayan na gama ƴan tunani na. Ita kanta Aunty Sadiya jikinta duk ya mutu,dan a zahirin gaskiya ba wani aljani dake jikinta ko yake bibiyarta,mutum ne dai to kuma idan mutum ne sai ya zamto Dany kai ina bazai taɓa kasancewa shi ne ba ta hakan zata kasance,mutumin da ko hausa baya ji bai kuma taɓa zuwa

arewa ba,hulɗa da musulmai ma baya yi,to taya zai kasance shi?
Binciko wannan amsar daidai yake da binciko halittun cikin ruwa,da yawansu wanda kuma yin hakan badai bawa ba sai ubangijin da yayi su a ciki,dan haka wannan zancen ma bashi da amfani Allah ne kawai masanin gaibu.

⚜⚜⚜⚜⚜

Idan ka kalleshi zaka ɗauka barci yake yi,yadda ya rufe ido luff yana kuma sauke ajiyar zuciya irin ne barci,amma a zahiri ita yake tunowa murmushi kawai yake saki tuno yadda take kallon cikin idonshi tana gayamishi magana ƙara lumshe ido yayi a inda kwanyarshi ke ƙara haskomishi hoton ta,bazai iya dakatar da kanshi yabo da begen halittar da ta kasance jaruma a cikin mata  ba,duk kuwa ta kasancewar ita ba ƙabilarshi ba ce,lokaci n farko yaji wani abu akanta yana son macce mara shakka da tsoro da tsiwa,ɗan ɓata rai yayi ba tare da ya sani ba tare da jin wani irin abu wanda zai iyacewa zafi a ranshi tuno yadda yaga hawaye na zirya akan fusksrta sai kuma ya sake sakin wani irin murmushin ko na meye??

Cikin salo ta fara shafa shi salon da tasan yana jan hankalinshi,"Aure fa xamu yi amma na rasa dalilin dayasa nake ganin kamar u are not interested,Dany u know i lov u morethan anythings ,we have to get a baby before we marriged,baka son k..."
"Shiii!
Ya faɗa ba tare daya buɗe idonshi ba,baya tare da ita hasalima ba jin abunda take faɗa yake yi ba.
"Am not in dt mod",ya faɗa can ƙasan maƙogaro ,"leave me alone pls".
Duk da yarbanci suke maganar. "Momy ce ta aiko ne fah,"ta faɗa kamar zata yi kuka.
Shiru yayi mata baya son yawan magana tafi kowa sani.Naci ne ma da ita kamar maiya tasan idan yana yanayin buƙata tana zuwa yake biye mata.
Cigaba da shafa shi tayi cikin salon karuwanci,ɓalle mishi buturen riga ta shiga yi.
Buɗe idanuwanshi yayi tare da riƙe hannayenta duk biyu,wani irin wawan kallo ya bita da shi,tashi tsaye yayi daga zaunan da yake kamota yayi har wajen ɗakin ya turata ya janyo ƙofar ya rufe.
Kuka ta fashe da shi,bata son ta rasa shi,shi ne burinta shi ne mafarkinta.
"Taye meye faru?"
Juyowa tayi ganin momyn yasa ta faɗa kan jikinta,"Momy Dany baya so na,baya son aure na".Ta faɗa cikin kuka
Lumfasawa  Momyn tayi,"Ba haka ba ne Taye,Dany naki ne ki saka a ranki bashi da wata matar bayanke dole zai so ki ne ma,u are my only inlaw Taye ki share hawayenki kibarni da shi muje ki kwanta tunda ya rufe ɗakin shi,"cikin sigar lallashi take yi mata mgnr tare da kulawa da nuna soyayya.
Goyan bayan Momyn akanta shi ke ƙara mata gwarin gwiwa,akan duk rintse ita ce zata zamto tashi.
Janta Momyn tayi suka bar gurin.

⚜⚜⚜⚜⚜

Ko da yaya ya dawo Aunty Sadiya tayi mishi bayanin abunda ya faru yasha mamaki sosai,shi kanshi abun ya ɗaure mishi kai matuƙa,kwantar mata da hankali yayi akan karta ji komai tayi hkr insha Allhu ba zata bar aikin ba,bazai kore ta ba,duk da shi kanshi ya faɗa ne kawai amma baya tunanin Sir Daniel yana da mutuncin da zai iya barinta.
Juyi kawai nake yi akan gadon na rasa wacce irin kaddace haka ke bibiyata,ba abunda yanxun yafi damu na illa aikin Aunty sadiya bana so nayi silar rabuwarta da aikin da take mugun so,ya xamar min dole nayi wani abu,dole zan kuma haɗuwa da shi zan roƙeshi a madadin naci mutumcin shi akan barazanar da yai tawa rayuwata a madadin nayi ramuwa zan bashi hakuri dole na ɗuka domin Aunty na,da wanan tunanin barci yai awan gaba da ni.

⚜⚜⚜⚜⚜

A ƙa'idarshi ƙarfe takwas yake tashi ya shirya zuwa tara ya gama shiri sai ya tafi gurin aiki,saɓanin yau da ta kasance ranar farko a gareshi daya tashi ƙarfe bakwai saura,shi kanshi ya rasa dalilin daya kawai yaji yana son zuwa office da wuri,duk da wata zuciyar shi tana tsokalarshi akan dan yana son ganinta ne,amma yaƙi yarda da hakan.cigaba da shirin shi yayi cikin navy blue da farar suit ya shirya yana matuƙar son farin abu.
Kallon kanshi yayi a madubi,ko ba'a faɗa ba shi kanshi yasan shi classic guy ne yana kyau na gaban kwatance ga haiba da ƙwarjini,zubin jaruman maza gareshi masu faɗin ƙirji,bai tsaya ƙarewa kyawunshi kallo ba ya zura farin glas ɗin shi wanda ke ƙarawa kyawunshi kyau.
Ita kawai take faɗu mishi a rai,yana son ganinta fiye da tunaninshi ita ce yaji ya kasa samun natsuwa tun daran jiya  feel somtings strong about her,breifcase ɗinshi ya ɗauka ya fita daga cikin ɗakin wanda zan ce aljannar duniya.

Bai haɗu da kowa ba,tunda ya fito,wata hanya yabi wacce ta sada shi da steps kaɗan yana kai ƙarshen ya ci karo da wani ɗaki,nufar ɗakin yayi ba tare da shakkar komai ba.
"Goodmorning Swt heart,"can ƙasa yayi maganar.
Kasancewar ta saba da jin mgnrshi yasa taji abunda ya ce,juyowa tayi daga gurin da take zaune.

Murmushi tayi wanda ke nuni da tsantsar ƙaunar da take yi mishi,tashi tayi ta nufe shi,"Morning my Dear har ka shiga fita haka da wuri?yauwa Dany meyesa jiya ba kabar Taye ta kwanta a ɗakin ka ba,ita ce matar da zaka aura nan da wani ɗan lokaci ya kamata ta samu ciki....."
"Ina sauri ne Momy idan na dawo kinyi maganar,"ya faɗa tare da xame jikinshi daga rungumar da tayi mishi,bai ko tsaya ya waiwayeta ba,ya fita ,"Sai na dawo Momy".
Kallon mamaki ta bishi da shi,ganin yadda yake sauri haka tasan ko wani abun gaggawan ne ya taso ai akwai secretary,to ko saurin me yake haka ohho???

Tun asuba na tashi jiki a macce duk jina nake yi kamar ba niba,shiryawa na fara yi,ina cikin shirin Anty Sadida da Yaya suka shigo,ta ce bari ita taje taji abunda zai faru,jiki na ya ƙara mutuwa domin ƙwaroƙwaro naga ƙaraya a cikin idanun su.

"Ya ubangiji ka ɗaura ni akan wata dama wacce xanyi ramuwar gaiyya ga wannan halittar ta ka,Allah kasan ban iya jure abun da ban ɗau fansa ba akanshi,wannan halittar taka in ma dai mutum ce ko aljanna Allah ka bani ikon yin galaba akan shi Allah ba ruwan Auntyna  Allah kasa kar abun ya shafeta,"hawaye nake yi masu zafin gaske a inda maganar ke fitowa daga can ƙasan zuciyata,kallon ƙofar nayi wacce suka barta a buɗe bayan fitarsu,ina kudurtawa kai na duk rintse bazan taɓa bari ta rasa aikin ta ba.
Ga tsanar wannan halittar da ke ruruwa a cikin raina har wani ɗaci nake ji ai ko masoyina nasan zai ya tayani tsanarshi,shi babban maƙiyi na a duniya har wani ji nake kamar na kashe shi na huta.

Duk da kasancewar mutane sun yi ɗan mamakin ganinshi,amma basu wani ji ko kawo wani abu a ranshi dan shi ɗin kamar hanwawa yake me zanja kala da launi.
Yana zuwa Office ya zauna zaman isa da gadara dan yana da fariya da gadara,rufe ido yayi yana jin wani iri a ranshi baƙon lamari dai kawai idanuwanshi yake so suyi toxali da ita.
Ɗanna wata ƴar ƙararrawa yayi wacce kai tsaye take aikowa office satariya saƙon kiran shi.
Shiru yaji har gurin minti ishirin ba ita ba alamarta.
Ita kuwa Aunty Sadiya da tunda ta shigo jikinta a macce har ta isa office ɗinta ta zauna shiru bata ga wata alamar sallama ba,dan idan har aka sallami mutum to ko da zai xo gobe zai dai yaga wani kan kujerarshi.
Kuma bata ji wani labari makamancin hakan ba,hasalima lura da tayi ba wanda ya shiga office ɗin tun jiyan.
Office ɗin P.A ya ɗanna kira bai kai ga sauke hannunwanshi ba yaji knocking.
"Come in",ya faɗa ƙasa.
Jiyowa tayi,"Goodmornig Sir".
Kallonta yayi sama da ƙasa ya daɗe yana jin sha'awarta saidai shi abu ɗaya ne baya so rai ni,bazai taɓa iya neman ma'aikaciyarshi ba,bada kai kenan wanda baya jin xai iya bada kanshi ga kowa,ko matan waje su ke bada kansu gareshi.
Ɗaure rai yayi daman ba ma'abocin fara'a ba ne,"where is secretary?"
"Bata zo ba tun jiyan nan,saidai naga accounter (Aunty Sadiya)ita ta zo yau".
Tana kai aya yace,"call her".
Ta juya ta fita ita kanta tana mugun sonshi,da biyu ma tayi yadda tayi tazo kamfanin aiki dominshi amma har yau ta kasa samun ko wacce irin dama.
Rass gaban Anty Sadiya ya faɗi jin wanda ke kiranta,haɗiye wani daskararren miyau tayi ta fito daga office ɗin na ta jiki a mace,tana zuwa tayi knocking ya bata izinin shigowa.
"Where she is?"
"Amm..am she is at home..we thng dt ..thatt".
"Call her bata san dokar ƙin zuwa office ba ne?"
Wani irin sanyi taji a ranta har saida tayi wani irin deepbreath na jin daɗi,"Ok sir thank u Sir",ta faɗa jiki na rawa bata taɓa tunanin ita kanta xata cigaba da aiki ba,balle kuma Meenal.
Fita tayi cikin jin daɗi jiki na rawa ta shiga kiran Meenal ɗin ringin ɗaya biyu ta ɗauka.
"Meenal wllh ke me sa'a ce,Allah na sonki Meenal".

"Allah na son kuwa ai Aunty Sadiya".
"Eh haka ne amma ke me sa'a ce,kinyi abunda ba wanda ta taɓa yi ya xauna".
"Ya aka yi gayamin tsinannen ya koreki ne,bari na zo na bashi hakuri dan Allah yayi hakuri ni ya hukunta ni,"a gaggauce nake yin mgnr kamar ta kusa ƙarewa.
Dariya Anty Sadiya tayi,"A'a Meenal be kore niba kuma ke ma yace ki dawo bakin aiki,ki shirya yanxun ki fito",ƙil ta katse wayar. Wani irin sagaga nayi,"meye manufar mutumin nan akai na?idan bashi aljanin ba ai kurata zaiyi kamar yadda suka faɗa",hura hanci nayi cikin ɗaga murya nahau faɗin,"Yau kuwa dole ayi ta ƙare zai ka gayamin manufarka akai na...."tamkar ina gabanshi yadda nake maganar "Ai daman nasan duk kai ne,kana son ka saka ni a cikin ruɗani ne dan ka ga ko xan so ka, soyayya dai banyi duk kuwa tsiyarka..."ina faɗan ina shiri.Daman tun safe nayi wanka na shirya,cikin duguwar riga baka da ratsin fari,gyalen rigaar babba ne na yafa abu na,na saɓa jaka..
Na fito fuska a murtuke,ina zuwa na je direba yaja ni gurin,kansutuwar ba wani nisa yasa muka isa da wur,na fito duk da naji gabana yana faɗuwa amma ban yarda hakan yayi min tasiri ba,na fito ban ko biye ta mutanen da naji suna saƙin ƙananun maganganu ba,ko Office ɗin Aunty Sadiya ban waiwaya ba,kai tsaye office ɗinshi na nufa,knocking nayi.
"Come in,ban ji abunda yace sosai ba amma nasan umarnin shigowa zai bani hakan yasa na faɗa,"Ai ko baka faɗa ba shigowa zanyi,"na faɗa da ɗan ƙarfi tsakiyar office ɗin naja na tsaya ina hura hanci da baki.
Dany kuwa da tunda ta shigo ya bita da wani irin kallo wanda shi kanshi bai san na meye.
"Kai malam ya isa haka,ka fito muyita gaba da gaba,idan mutum mutum idan aljann aljanna".
Bai san lokacin da ya sake wani irin murmushi ba,"such an idiot girl".
"Idiot!na furta da ɗan ƙarfi na haɗe da zare ido.
Kalaman daya xuburbuɗamin jiya ne suka dawo kwanyata tare da haifarmin da wata irin muguwar tsanarshi.
"am not an idiot u are ,idan hauka nake yi ka fini,jahila dabba kuwa wllh duk kai ne su,ni ko a jikin hajilar ban taɓa jin larabin takkuli irin ka ba,dan na ce bana sonka,ka mare ni ka tsorata ka kuma xage ni,for wht?i have never see person like u in my life,i say it and i will say it again i hite u r......
Tasss wani lafiyayyan sauti ya duki kunnuwana ban an ƙare ba sai gani na nayi a zuƙunne a kasa,ɗagowa nayi a razane a kuma tsora ce,raɗaɗin da naji a kunci ne ya tabbatar min da mari na yayi,hawaye shaaa kuka na fashe da shi,"Who do u think u are? da zaka mare ni haka Allah ya isa ban yafe ba wuta ballal kuma sai na rama,i hite u wllh bazan taɓa sonka ba,ko kashe ni xaka yi tsinnan ɗan a bura uba. Ɗan balaja'u ɗan batsula..,"cikin tsantsar kuka nake xagin nashi da.

Runtse ido yayi,a kaff duniya ba wanda ya taɓa kiranshi da mahaukaci,wacece ita da xata kalli cikin idonshi ta kira shi mahaukaci,wani irin zafi yaji har cikin ranshi.
"Mahaukaci kawai wawa dabba jahili....ta uwa ta uba nake zaginshi zagin da ni kai na ban san na iya ba..
Duk da baya jin take cewa amma yadda take mishi mgnr cikin ɗaga murya ya ƙara kai shi ƙarshe wacce irin yarinyace wannan mara hankali,buɗe ido yayi wanda har sun sauya kalla tsabar bacin rai ya ƙara shatata mata wani uban marin.

Wata irin gigitacciyar ƙara na sake da dukkan ƙarfin muryata......

*Hmm...this is just d begining...yanzun wasan zai fara,sai ku gyara zama.*

*Mu tashi Ify fans*

*#Comment*
*#Share*
*#Vote and like*
👏 *Please*

~Mrsbalarabe✍️~

*KAUNAR ƁOYE!!!*
_(THE SECRET LOVE!🖤)_

*Fatima Batula✍🏼*

_Wattpad:mrsbalarabe._

*I Dash d whole page to u MASOYIYAR Marubuta😍haƙika kin nuna mana ƙauna kin yabe mu,kin saka munji cewa mu ƴan baiwa ne,kin mana yabon da mutane basu yi mana,mun gode bai isa zama tuƙici gareki ba saida muyi miki addu'a Allah ya cika miki burikan ki na duniya ya baki sa'a akan duk abunda kika saka a gaba,ya yiwa rayuwa albarka ya kuma haɗamu a firdausi kamar yadda kika yi fata,Batula ƴah ga Umar mata gurin Yaya Balarabenta,ta gaidake tare da jinjina miki Dear yabonki agare mu ya saka ni jin daɗi har raina,fatan Alkairi Mosiyiyar mu,Allah yabar ƙauna.*

*Dedicated to my Anup(my happines) Allah ne kawai yasan irin son da nake yi miki, ke abun so ce dole duk wanda ya raɓeki ya soki, baki na bashi da kalaman godiya da nuna irin matsayinki a gurina sai dai kawai na ce ke ta musamman ce a cikin rayuwa ta, Allah yabaki Ify ya baki miji na

gari. Amin thumma Amin.*

_Page_

_13-14_

✍ *✍ ĠÓĹĎĖŃ ṔĖŃ ẂŔÍŤĖŔŚ ÁŚŚÓĊÍÁŤÍÓŃ* ✍✍

*wє αrє вєαrєr's σf sσ gσldєn pєn*
*wє wrítє αssídíσuslч pєrcєívє nσ pαín,*
*sσ mαgícαl σur crєαtívє gσldєn pєn* ✍ *,вєhσld σur wσrds.α prσduct σf σur pєn* *,sαvσur σur wσrds, fσr ít wíll* *cαusє чσu nσ pαín.*

*Yadda Annabi, Tsira Da Amincin Allah Su Tabbata A gareshi, Yake Kirga Tasbihinsa.*

Daga Abdullahi bn Amr, Allah ya yarda da shi, yace; Na ga Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, yana kirga tasbihi da (yatsun) hannun damansa.

*INA MASOYAN LITATTAFAN ƘUNGIYAR GOLDEN PEN?*

*NESA TA ZO KUSA, TUNANIN RASHIN SAMUN NEXT PAGE YA ƘARE!.*

Kasance mutum na farko da zai fara karanta sabbin littattafan marubutan mu, a duk lokacin da muka yi typing. Kina/Kana iya samu, ta wannan damar ce kawai idan ka bi wannan links tare danna *LIKE* a shafin mu na Facebook zaka/zaki iya samun cigaba ko kuma ki samu duk littafin da kike buƙata namu daga farko.

https://www.facebook.com/Golden-Pen-Writers-Association-102095951667849/

Sai kun zo, kar ku manta a koda yaushe comments da sharhin ku yana ƙara mana ƙarfin gwiwa a wajen rubutu mai yawa.

_*Bismillahir~rahamanir~rahim*_

Rufe kunnuwanshi yayi da hannayenshi duk biyu,amma hakan bai hana ƙarar ihunta shiga cikin kunnuwan shi ba.
Kafin cikar saƙon Office ɗin ya cika dam da mutane ihun da suka ji,a ruɗe Aunty Sadiya ta nufo ni,"Meenal..Meenal.."Abunda ta iya faɗa kenan duk ta ruɗe.
Security ne suka kamo ni,nan Aunty Sadiya ta ruɗe ta shiga yi musu magiya tureta suka yi,suka

ja ni,ni kuwa da gaba ɗaya bana tare da wannan duniyar ma,nadai ji alamun rike ne aka yi irin riƙon ɓara yin nan.
Fituwa yayi daga office ɗin kallo ɗaya zaka mishi kasan yana cikin wani hali me wuyar kwatantuwa,huci yake yi kamar mafaraucin zaki.

Kai tsaye gurin motorshi ya nufa,daman shi ke tuƙin motor da kanshi,yaja ta da ƙarfin tsiya,bazai taɓa iya misalta ɓacin ran da yake ciki ba,idanuwanshi sam basu gani tsabar ɓacin rai.
Wani irin sautii yaji ƙiiiii sannan yaji kanshi na juyawa yana hajijiya wanda hakan ya tabbatar mishi da cewa haɗari yayi.

Kuka Aunty Sadiya ke yi muraran tana basu hakuri su ƙyale ni,amma ina basu ji basu gani,inda ake kulle masu laifi kafin a yanke musu hukunci suka kai ne,jefa ni suka yi sannan suka saka key suka ƙulle ƙofar.
Kallon gurin nayi ina zubda wasu irin hawaye masu zafin gaske  na kasa gane yadda zan kira wannan lamarin da shi,illa kawai nace ina cikin goma sha tara,ina cikin hau ina cikin iftila'i wanda wannan halittar ne ya jefa ni a ciki,xama naje nayi kan wata ƴar duguwar kureja,har lokacin ina dafe da kunci na.
Ina jiyo kukan Aunty Sadiya to bani da baki balle nayi magana.

******* *** *******

Shi kuwa cikin gaggawa akai asibiti da shi,tare da yi mishi taimakon gaggawa.
Kiran Momy aka yi,a ruɗe ta zo tana kuka kamar  zata mutu shi ne kawai ɗan ta duniya tana yi mishi wani irin mugun so lallashinta likitocin suka yi suka kuma tabbatar mata da abun yaxo da sauƙi bai ji ciwo ba,zai kuma farka lafiya zasu iya tafiya gida ma,sannan taji ɗan sauƙi a ranta.
Taye ma kuka take yi sosai.
Ƙarfe huɗu ya farka,meyeasa yake jin wani iri a ranshi a madaɗin yaji yana jin haushinta sai ma jin da yayi be ƙyauta ba,meye laifinta bata san yana da matsalar kunne ba ne,ya tsinci kanshi da bata uzuri.
"Ka tashi ba abunda ke ma ciwo ko?",a ruɗe Momy take tambar nashi.
"meye ya faru?na hanaka tuƙi amma ka ƙi ji,kana tunanin idan wani abu ya faru da kai xan yafewa kai na ne?siraran hawaye suka hau zirya akan fuskarta.
Murmushi yayi kaɗan tare da yunƙurin tashi zaune,maida shi tayi.
"Ai ba abunda ya farun?ba abunda zai faru da ni Momy,muje gida".
Ya faɗa can ƙasa.
Tashi yayi yana jin kanshi na wani irin sara mishi amma ya jure baya so hankalin ta ya tashi,kama shi tayi suka fito har harabar asibitin suka shiga moto direba yaja su.
Suna isa ta kawoshi har ɗakinshi,"bari n kira Taye na gayamata mun dawo gida ta zo nan".
Ɗaga mata kai kawai yayi,ya tashi ya shiga toilet ya daɗi yana watsawa jikinshi ruwa,duk wani tunanin da xaiyi da ita,ko taye da yace yana so sam baya tunaninta haka.
Yana fitowa wayarshi na ringin daman tun ɗazun yaji tana ta yi,da kamar karya ɗauka sai kuma yakai hannu ya ɗauka.

"Hello sir ga yarinyar nan an kamata me kake so ayi mata".
Shiruu yayi yana saurar zuciyarshi yaji ko zata raya mishi wani abun amma yaji ba abunda take raya mishi illa a saketa taje gida ta huta.
"hello Sir!
Maganar ta dawo dashi daga duniyar daya faɗa.
"A sake ta",yana faɗa ya katse wayar  faɗawa kan kafitar yayi tare da yin wani irin deepbreath.
Yasan shi dai ba me sauƙi ne haka ba,amma kawai yaji yana sauƙaƙa mata ai tun jiya ya kamata a hukunta ta,meke faruwa ne haka tun kallon farko yaji yana jin wani abu akan ta.
Murɗa ƙofar dayaji anyi ne yasa ya juya,tun kan ya ɗauke idanshi akanta ta iso gareshi ta rungumeshi a zaune.
"Ba abunda ya sameka naji dadi,bazan iya jurar wani abu ya sameka".
Lumshe ido yayi yana jin kalamanta har ranshi musamman sigar da tayi mgnr da shi.Ganin jikinshi ya mutu yasa ta ƙara samun damar manne mishi tana shafa kwantaccen gashin ƙarjinshi wanda ya jiƙe da ruwa.
Kiss takai mishi akan ƙirjin yirr yaji tsigar jikinshi ta tashi,kwantar da shi taye akan gadon ta haye jikinshi.
"I lv u to,i wnt to u in my life with u,u are my heartbeat".
"i lv u too taye",y tsinci kanshi da faɗin hakan duk da dai ba yau ne na farko ba ,amma sai yaji wani iri kamar bata cancanci ya so ta ba.
Cikin shauƙin so da sha'awar juna suka hau jiyar da juna dadi,Taye ta ƙware gurin iya sex shiyasa yake mugun jin daɗinta.

*****

Gaba ɗaya cikin su ba wanda ya iya cewa da kowa komai,kuka Aunty Sadiya take yi ƙasa-ƙasa.
Ni kuwa da nake kwance rufi cikin bargo ina ta rawar sanyi , wani irin mugun zaxzaɓi ke tambaliya da ina son nayi mgn amma ba hali.
Ɗafata yayi,"ya isa haka Dear saidai kawai mu godewa Allah da komai ke zuwa cikin sauƙi,abunda za'ayi gobe kawai ku ajiye aikin da kanku sanan bayan kwana biyu ku shirya ku tafi kano".Cikin sigar ban baki yayi maganar.
Share hawaye Aunty sadiyar tayi wannan ita ce mafita su ajiye aikin kawai ba zata iya jure duk wani abu da xai faru da Meenal ba.
"to zan kwanta a nan,sai da safe".
kiss yai mata,"to ku tashi lafiya Meenal sannu zaki ji sauƙi kinji",yana faɗa ya juya ya fita.
Kwanciya tayi kusa da Meenal ɗin wacce har yanzun bata daina rawar sanyi ba.

Su kuwa barci ne yai gaba da shi bayan sun gama jiyar da juna dadi,sai bakwai ya tashi duk da ba wankan tsarki yake yiba,amma duk ya gama saduwa da macce sai yayi wanka,bai tashe ta ba,ko da ya fito ya shirya cikin gajeren wando da riga ya fito,ɗakin hutawar momy ya nufa yana zuwa ya sameta zaune,tana ganinshi ta taso.
"Ka tashi ya kake jin jikin ka?"
100% normal".

Ya faɗa yana maida mata martanin murmushin da tai mishi zaunar da shi tayi,ba musu ya zauna.
"Taye bata tashi ba ko?"
"Eh!
"Taye na sonka da yawa".
" i know".
"ina so na ganta da ciki ne sai a ɗaura auran ku,ina son ganin jika na,ka dunga kulata yadda za'a samu cikin ".

"Okk!ya faɗa a fakaici shi kanshi yana son yaro fiye da komai.
"Dany meye ya faru ne a office?" ta jefo mishi tmbyar.
Shiru yayi me zai ce to.
"Naji kuma ance a sababbin ma'aikatan daka ɗauka musulmai sunfi yawa,u know very well bana son musulmai bana kuma son kana hulɗa da su, kuma ka san waye mahaifinki fiye da kowa?

Ita ce ta faɗo mishi a rai,"musulma ce,"ya faɗa a ranshi,yana jin wani irin connection me ƙarfi game da ita,wanda kuma yake jin bazai iya nisanta kanshi gareta ba,yasan iyayenshi basu son musulmai sam,kuma shi ma haka,duk da cewa saka mishi ƙiyayyar aka yi....

"naji ance secratary ka musulma ce ka kureta".
"What ya furta a ɗan zabure.
"Ka cire ta na ce".
Wani irin abu ya haɗiye kutt duk yaji ya dabure bazai iya kurarta yana son ganinta kusa kamar wata ɓari a gareshi.
"tunanin me kake yi?
"Nothing zan cire ta..but for wht reason kike son na kureta me too i hite muslim kina tunanin zan kulata ne ko me?ƙazamace fah im just hiting her ma,tunda na fara ganin yanzun haka ma na saka an kulle ta,i wnt to make her life misrable cos ita ta kasance musulma ina jin daɗin ganin ta kuntaka,I wnt her to realized yadda musulmai suke gurin mu,yadda zata ji ciwon kasancewarta musulma...." shiru yayi yana jin wani sabon lamari,shi dai ba wani ma'abocin ƙarya ba ne,amma ji yadda ya sake baki yana faɗin mayaudariyar ƙarya to,sam waɗannan kalaman nashi na ƙarya ne shi kanshi ya shaida hakan,ko ɗis baya jin ƙiyayyarta a ranshi sai ma wani irin feelling da yske ji akan ta wanda bai san ko na meye ba,and kuma bazai iya ganinta kuntaka ba,tuno yadda yake jin zafin ganin hawayenta,duk taya ya iya shirya wannan mayaudariyar ƙarya?tambyar da yake yiwa kanshi kenan,duk domin me?.
"good ka wulaƙantata kaci mutuncinta,kayi mata ƙazafi ka nuna mata ƙiyayya",Momyn ta faɗa cikin jin daɗi.
Yaƙe yayi wanda ko fuskarshi bata gamsu da shi ba,balle zuciyarshi..
Fira suka shiga yi suna nan Taye ta zo,kan cinyarshi ta ɗare,sai wani shafashi take yi,ai ba maganar kunya ga fariki.
Shi ma yana biyeta cikinta ya shafo har gurin ƙirjinta,lumshe ido yayi a duniya ba abunda suka fi ɗaukar hankalinshi zama da nonowan macce,ita kuwa Momy washar baki kawai take yi.

Jan shi Tayen tayi suka bar gurin dan sun fara fita haiyacinsu,ɗakin suka koma romance sosai suke yiwa juna cikin tsananin ƙwarewa take sarrafashi da abunda yafi so,haka shi ma yana mugun nishaɗantu da soyayyar Taye me mantar da shi komai da komai ta kai shi duniyar dadi. Murzar juna suka yi iya iyawarsu ita kanta ta yarda da jarumtarshi har gajiya take yi ta fara neman guduwa duk maitar ta kuwa yana bata jikin ta....

***** **** *****

Da zaxzaɓe sosai na kwana a jikina,sai gurin asuba muka samu barci ni ta Aunty Sadiya,ina jin sallah amma na kasa tashi dan jiki na ciwo yake yimin ga wani irin ciwon kai na azabar hawayen da nai tayi.

Ina jin Anty Sadiya ta tashi tayi sallah ta idar.

"Meenal ɗaure ki tashi na haɗa miki ruwan zafi,ki watsa sai ki fito kiyi sallah ki koma barcin".

Bata barni ba saida ta tabbatar na tashi da ƙyar sannan.

Fita tayi taje gurin mijinta suka gaisa ya rakata kicin ta ɗafa indomi da ƙwai ta suya dankalin turawa,ɗaki ta kawomin nawa tare suka shigo harda Baƙir muka gaisa.

Ina son wannan ahalin so me lafiya ma,zan so cigaba da zama da su amma ina bazan iyaba lagos tafi ƙarfina.

Saida suka sa naci sosai,na kuma shan magani sanan yaya yace a barni na huta.

Ban ce su tsaya ba,dan ni kaina ina buƙatar hutu ina buƙatar kaɗaici ko na samu na dawo da tunani na da kwakwalwa ta aiki,dan tun shekaran jiya suka tsaya da aiki.

Lamo nayi na zurfafa tunani na can iyakar shekarun da na fara ajiye abubuwa a memory na.

*MEENAL MANSUR MANGA* shi ne dai asalin tunana,ban san tarihi da asalin mu ba,nidai kawai na buɗe ido na gamu a garin kano,na kuma gan mu a cikin ƙabilar hausawa sanan kuma cikin addinin tsira da aminci addinin musulunci,mu uku kawai na buɗe ido na gamu mama mahaifiya masoyiya a gare mu kuma ƙawa,Mama bata magana haka muka buɗe ido muka ganta amma muna mgnr mu ta kurame da ita,tana ma ji raɗau saidai bata mgn,ba muga wani uba a gaban mu,kuma har yau bamu san yadda lamarin yake ba,yana raye ne ko ya mutu,waye shi ɗan ina ne,duk wannan amsoshin bamu san su ba,ba kuma mu taɓa tambayar mama su ba. Abu ɗaya ne dai wanda muka saka a ran mu,shi ne mu ƴaƴa ne,dan maa tana mugun son mu,a bata aikin komai to aikin me zata yi ma bata gani,ba kuma mu san ko tun haihuwa b ne rashin ganin.

Cikin tarbiyar islama muka ta so dan ni hafiza ce,na haddace littafin Allah kuma nasan tafsirin kwata daga cikinshi,haka ma Aunty Sadiya zan iya cewa ma ban taɓa ganin me son addini irin na Maama ban taɓa ba,har mamaki nake yi,kuɗi kuwa bamu san inda take samo su ba,mundai san ta fi mu sanin meye halal meye haram shiyasa bamu damu ba,balle mu nemi ba'asi,haka muka ta rayuwa cikin jin daɗi da ƙaunar juna bamu wani damuwa da rashin dangin da muka ga bamu da su ba,dan Maa cikin tarbiyyar tauhidi da ihisani ta raine mu.

Lokaci yana ja muna girma yadda muke amfani da kuɗi ya ragu wanda hakan ya tabbar ta mana da cewa kuɗin sun yi ƙasa kenan ƙuɗin da take ɗiba.

Bata da wata kalma a gare mu kullum bayan cewa,mun yarda da ita,mu kuwa mu bita da amsar eh ke yardaddiyace Maa.
Nifa tun ƙuruciya nake jarabbiya ƴar bala'i ina da tsiwa ta fitina,ga rashin hakuri dan ban san cewa na yafe ba,ina kayimin nayi maka shiyasa ban fiye shiga sha'anin mutane ba,duk wanda ya taɓani ya taɓowa kanshi.
Ban iya shanye abu sam,daman Maa bata bamu damar yin ƙawaye ba,hakan yasa ba ruwan mu tun ƴan unguwa na tsegumi har sun gaji sun daina.Ana haka Yaya ya shigo rayuwar mu,mutumin arzƙe ne sosai ya jure kawaicin Maa har ya shiga ran mu ya zamar mana ɗan uwa tun Maa bata so ya fara yi mana hidima har ta hakura,tundaga nan shi ya cigaba da ɗawainya da mu har yanzun kuwa,shi masoyine na gaske duk ya jure tsagumin mutane akan mu na cewar mu shegu ne,nidai ya zamemin yaya.
Haka fa har Aurensu shekara shidda da rabi kenan,wanda bayan bikin basu yi shekara ba suka dawo wannan garin,na lura da Maa bata son lagos sosai amma haka nan ta haƙura,nima zuwana wannan saida muka sha fama da magiyar da bamu taɓa yi mata ba,ta barmu muka zo badan ta so ba.
Wannan kenan taƙaitaccen tarihin rayuwata.
Juyawa nayi tare da sauke wata irin ajiyar zuciya wannnan tunanin ya dawomin da abunda na rasa,tun zuwa na legos ya kuma haskomin wani abu,sannan kuma ya tunatar da ni ni wacece,ya kuma kunnamin injin kai na daya mutu.
*** *** ***
Yau ma haka ya tashi yana son ganinta har wani ji yake yi kamar ya shekara,dariya ma yake ba kanshi da kuma mamaki yaushe ya santa kwana biyu kawai amma ji yadda yake missing ɗinta ko Taye baya jin haka,tana nan kwance ya shirya tsaff abunshi ya fito.
Bai yi niyyar zuwa gurin Momynshi ba dan yasan zata hanashi zuwa ne,shiyasa ya waske sai cin karo suka yi a falo.
"Dany!ina kuma zaka ne?muje ka cire kaya yau ba zuwa office",cikin nuna kulawa tayi maganar.
Shi daman abunda yake gudu kenan,kafin ya ƙwaƙwulo ƙaryar d zai gayamata yaji ta ja shi,"Muje ba inda zaka wai yaushe ka fara son aiki haka da nasan baka son aiki ko kaɗan sai sa'a".
"ina son ganin wa...shiru yayi jin abunda ya faɗa wanda shi kanshi jin maganar kawai yayi ta fito.
Tsayawa tayi,"Wa zaka gani?"
"Eh Momy akwai su costomer ne sun sha zuwa basu samu na".
"To meye amfanin ma'aikatan?"
"Ehm ..amm eh suna nan amma nayi musu alƙawari ne zamu haɗu da su ne".
"Ina sakatariya ta sanar da su baka da lafiya ko a soke meeting ɗin sai nextweek"...

Shiru yayi tunanin yadda zai ɓuluwa Momy ta barshi ya fita ,yana son ganinta har wani ji yake kamar shikenan bazai ƙara ganinta ba.....

*#Comment*
*#Share*
*#Vote and like*
👏 *Please*

~Mrsbalarabe✍️~

*ƘAUNAR ƁOYE!!!*
_(THE SECRET LOVE!🖤)_

*Fatima Batula✍🏼*

_Wattpad:mrsbalarabe._

*Dedicated to my Anup(my happines) Allah ne kawai yasan irin son da nake yi miki, ke abun so ce dole duk wanda ya raɓeki ya soki, baki na bashi da kalaman godiya da nuna irin matsayinki a gurina sai dai kawai na ce ke ta musamman ce a cikin rayuwa ta, Allah yabaki Ify ya baki miji na gari. Amin thumma Amin.*

_Page_

_15-16_

✍ *✍ ǴÓĹĎÉŃ ṔÉŃ ẂŔÍŤÉŔŚ ÁŚŚÓĆÍÁŤÍÓŃ* ✍✍

*ωє αrє вєαrєr's σf sσ  gσldєn pєn*
*ωє wrítє αssídíσuslч pєrcєívє nσ pαín,*
*sσ mαgícαl σur crєαtívє gσldєn pєn* ✍ *,вєhσld σur wσrds.α prσduct σf σur pєn* *,sαvσur σur wσrds, fσr ít wíll* *cαusє чσu nσ pαín.*

*Yadda Annabi, Tsira Da Amincin Allah Su Tabbata A gareshi, Yake Kirga Tasbihinsa.*

Daga Abdullahi bn Amr, Allah ya yarda da shi, yace; Na ga Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, yana kirga tasbihi da (yatsun) hannun damansa.

*INA MASOYAN LITATTAFAN KUNGIYAR GOLDEN PEN?*

*NESA TA ZO KUSA, TUNANIN RASHIN SAMUN NEXT PAGE YA ƘARE!.*

Kasance mutum na farko da zai fara karanta sabbin littattafan marubutan mu, a duk lokacin da muka yi typing. Kina/Kana iya samu, ta wannan damar ce kawai idan ka bi wannan links tare danna *LIKE* a shafin mu na Facebook zaka/zaki iya samun cigaba ko kuma ki samu duk littafin da kike buƙata namu daga farko.

https://www.facebook.com/Golden-Pen-Writers-Association-102095951667849/

Sai kun zo, kar ku manta a koda yaushe comments da sharhin ku yana ƙara mana ƙarfin gwiwa a wajen rubutu mai yawa.

_*Bismillahir~rahamanir~rahim*_

Kan ya ankare sai ganinsu yayi a ɗakin Momyn,"kin yarda da ɗakin ki?" . Ya faɗa yana kallon cikin idanunta cikin  tare da tattara dukkan tsanuwarshi a kanta.
Idonta cikin nashi ta ce,"na yarda da kai".
"To ki bari na fita zan dawo da guri abunda zanyi yana da muhammanci sosai".
Tana son naxartar wani abu daga cikin kalaman nashi tasan waye ɗanta kuma a sanin da tayi mishi sam bai ɗauki aikin shi da wannan muhammancin ba,kuma ta hango wani baƙon lamari a cikin idonshi naashi, wani abu ne me matuƙar muhammanci haka?.Katse mata gundun tunanin da ta faɗa yayi,"Yana da muhimmanci ",shi kanshi zuciyarshi yaji tana janshi ga hakan.
Ɗaga mishi kai kawai tare  tayi tare da faɗin,"Take care".
Kiss ya manna mata a goshi sannan ya fita yana sauri kamar wanda zashi bangon duniya.
Binshi kawai tayi da ido,ta kuma kasa yin tunanin komai.

****** **** *****

Ko da Aunty Sadiya ta isa office ɗin jiki a mace,gashi taji labarin har motor ta begeshi fitan da yayi,jikinta ya ƙara sanyi ,takardar barin aiki ta rubutu ta zauna tana da kallon takarda wani irin ƙunci take ji dan tana son aikinta bata shirya barinshi ba,amma kuma duk duniya bata da wani abu me muhimmanci sama da Meenal,dole zata yi domin Meenala,  wannan tunanin da tayi yasa ta tashi cikin ƙarfafawa kanta gwiwa akan abunda zata yi shi ne daidai,office ɗinshi ta nufa,daman ta san bai iso ba,hakan yasa ta shiga kai tsaye ta ajiyesu inda yana zuwa zaiyi tuzali da su ta fita,bata tsaya tabi takan kowa ba ta fito abunta taja motor,tana fita motorshi na shigowa,saida ya kalli motor duk da dai bai shaidi waye me itan ba.

Yana zuwa ya fito ya hau saman left ɗin wanda zai kai shi babban gurin ma'aikatan inda a nan office ɗinshi yake.
Ba ƙaramin mamaki mutane suka sha ba,gashi kuma sunga bandge a kanshi,abun ya basu mamaki haka nan ma dan hudu yaƙi zuwa office sai gashi abun ƙin zuwan ma ya kama ya zo,su dai na su kallo.
Suna gaidashi bai ko san suna yiba,daman kullum aikinsu kenan su gaida shi,shi kuma yayi banza da su,ba kowa ne ma ya taɓa jin maganarshi bs tsabar rashin son yin magana.
Yana isa office ɗin yaje ya zauna abunda ya faru jiya ya soma bijero mishi,"i wnt to see her,"ya furta can ƙasan maƙogaro,tare da kai dubanshi kan tebur ɗin,tozali yayi da dakardun inda ya gane cewa na barin aiki ne,bai wani damu daya duba ya gani ba,dan basu ne a gabanshi ba,duk da cewa yana wuya mutum ya ajiye aiki da kanshi.
Computer ya buɗe camarar tsaro ya shiga,wacce ke ɗaukar komai na office ɗin shi da ma sauran opisoshin.ganinta yayi ta shigo office ɗin nashi,ta ajiye takardun,cikin sauri ya janyo su ya fara dubawa,bai ma san lokacin daya miƙe tsaye ba,saidai ganinshi a tsayen yayi.
"Wht?
Ya faɗa da ɗan ƙarfe,sun ajiye aiki kenan shikenan,bai gaji da ganinta ba yana son kasancewarshi a tare da ita.
Komawa yayi ya zauna cibir,tare da ɗan runtse ido,duk abunda suka yi mishi bai kore su ba,sai su ne zasu ajiye aiki da kan su,wyar tafi d gidanka ya yanjo kai tsaye office ɗin PA,yana ɗauƙo ya kira ta zo bai jira ta bakinta ba ya katse wayar.
Ko da Aunty Sadiya ta koma gida ina zaune a falo na rangaɗa wanka ne hankali kwance rai fess.
"Kin dawo ya hanya",na faɗa hankali kwance domin na dawo Meenal ɗita.
"Zauna kinga muyi kallo the evil eye suke yi,film ɗin mu".
Zama tayi ita ma ba tare da ce da ni komai ba,ajiyar zuciya ta sauke kamar zata ce da ni wani abun dan har na juyo naji.
"kawomin ruwa me sanyi da abun taɓawa ko cake ne,yau ina so mu fita".
To kawai nace na tashi ita ma tashin tayi tayi ɗakinta ta canja kaya ko kan na dawo har ta canja,murmushi nayi har raina ganin aunty Sadiya cikin shigar riga da siket na atamfa kayan gida yau an tuna gida kenan.
Zama nayi bayan na miƙa mata,"Wai daman kina da atamfa a kayanki".
Dariya ta ɗan yi kaɗan ita kanta sai ta tsinci kanta cikin jin daɗi da farinciki.
"Har kamfala da shadda duk ina da su".
"Au shi ne baki sakawa".
A madadin ta bi zance na sai ta yanke da faɗin,"Meenal yau zamu gurin Yayar Abban Baƙir" .
Tana kai aya ta shiga kiran wata number wacce nake ganin kamar ta wacce tayi mgnr akan ta ne.
Ringin biyu ta ɗauka.
"Baban Baƙir kenan yau an tuna da mu?" daga can ɓarin ta ce haka.
"A'a ba haka ba ne Aunty Rabi'a,kin san abubuwan ne sai a hankali bamu samun time sai sunday,ita kadaice ranar da muke samu,amma yanzun komai ya daidaita ina nan zuwa ma ni da ƙanwata Meenal",takai maganar tana kallo na.

"Kai amma naji daɗi to shikenan sai kun zon".
" yauwa mun gode sai mun zo",ta katse wayar.

"Tashi ki shirya muje,"ta faɗa tana kallo na.
Nima kallonta nayi na kasa fahimtar yanayin da take ciki,dan nasan tunda naga ta dawo ta ajiye aikin ne.
To kawai na iya  ce mata na tashi nabar falon mayafi kawai zan yafa dan a shirye nake,ina fituwa itama ta fito yafe da babban gyale.
Murmushi nayi,"Kinyi kyau maman Baƙir.
Dariya ita ma tayi ita fuska ta ce,"ke ma haka antyn baƙir muje.
Tana rufe baki kira na shigowa wayarta,banga wanda ya kiran ba,amma naga duk tayi sanyi.
Saƙale tayi tana saurarar abunda ake ce mata wanda jinsu ya sauya mata yanayi.
Har na kagara ta gama naji ko meye.
Ana katse wayar ta zauna kan kujerar jiki a sanyaye.
"Lafiya anty?waye?meye ya faru? Ajere nai ta yi mata tambayoyin.

"Shi ne! ta furta a takaice
Tsaye na tashi daga tsugunnen da nake.
Bana mukatar ƙarin bayani da zasu tabbatar min da wanda take nufi.
Wanan mutumin na rantse da sarkin daya busa min lumfashi sai na saka rayuwarshi cikin kwalekwale,zai na saka yayi hawaye sai na saka yayi kukan da ba sauti sai na hanashi rintsawa sai na ɓata mishi lissafi sai na tsoratar da rayuwarshi kamar yadda ya jefani cikin tsoro,duk da hakan ma nasan bazan huce va.
Cikin dakewa nace ,"Muje!na faɗa ba tare da na kalli inda take ba,nasan daman dole abu ɗaya zai faru cikin biyu,idan har shi ne ki maƙaryacin aljani dole bazai bari mubar aiki ba,domin ai bai cin ma burinshi akai na ba.
"Je ki maida kayan aikin,bari nima na canja,"ina faɗa na juya.
Sagaga anty Sadiyar tayi,ya akai tasan akan ƙin amincewarshi ga barin aikin sukai maganar??meye kuma nufinta da su shirya su je?ta amince zata cigaba da aiki a ƙarƙashin ne ko kuwa?.
Tana nan zaune har naje na dawo,tsaye anty sadiya ta miƙe baki a sake tundaga sama har kasa ta tsaya kallo na.
Cikin baƙar riga duguwa iya gwiwa da pinki ɗin wandoa,sai rolling ɗin kai na da nayi da pink ɗin mayafi,na rufe idanuwana da bakin glass ga dugun bakin takalmi da na saka.
Ban tsaya jiran ta gama yimin kallon mamaki ba,nai gaba abu na,"Ina jiranki kiyi sauri pls",na faɗa cikin wata irin murya wacce ke nuni da ina sauri.
Me hakan ke nufi?ta shiryawa aikin kenan ta shiryawa zama a ƙarƙashin shi kenan ko me?Anty sadiya ke jerowa kanta waɗan nan tambayoyin.
Ni kuwa da tuni har na shege motor abuna,a shirye nake?waye shi da bazan fuskance shi ba?dole zamu fuskanci juna gaba da gaba domin sanin manufofin juna,dole zan ɗau fansar fitsarin da yasa nayi dole zan rama marukan da yai ta min,dole na rama disgen da yayi min,dole na tsorata shi,wannan shi ne ƙalubali na akanshi,i will take my revegen.
Nida zuciyata muke wannan zancen,ganin shiru yasa na yi hon da ƙarfi wanda nasan zata jiyo.

Ita kuma da ta faɗa duniyar tunani jin hon ɗina yasa ta dawo daga inda taje.
Ɗaki ta koma a gurguje ta shirya cikin kayan aikin ta fito,a gaban motor ta zame ni,bata ce min komai ba taja motor muka bar gidan.
Tuƙin kawai take yi amma hankalinta baya tare da ita,"wani irin abu ne haka,taya zai ce ba zasu ajiye aiki ba,sannan kuma harda barazanar faɗa musu suna yadda kenan ba zasu taɓa samun wani aikin ba,tsabar mugunta anya bashi da wata manufa kuwa akn Meenal,"takai ƙarshe mgnr tana sauke dubanta a gare ni.
Murmushi nayi mai aminci na ce,"Yadai ?"
Girziza min kai kawai tayi,ban damu ba duk da nasan cewa da wani abun a ranta,cigaba da latsa wayata nayi hankali kwance.

Kafin cikar minti sha biyar mun isa cikin kamfanin,ni na fara fitowa ban ma wani tsaya jiranta ba nai gaba abu na,cikin natsuwa da ƙasaita nake tafiyata.
Ita kuwa Anty Sadee binta kawai take yi da kallo,yadda take ƙwonbo kamar wacce ta shekera tana aikin.
Mutane sai faman bin mu da kallo suke yi,ni kuwa tsaɓanin yadda na saba, naji duk na tsargu ina ɗariɗari, amma yanzun kuwa ko a jiki na,banda ma ji nayi kamar zuga ni suke yi,suna ƙaramin ƙarfin gwiwa,hakan yasa ma na ƙara wani larkewa ina zuba isa da ƙasaita kamar wata matar me kamfanin,ni na fara kunna kai banyi wani abu wai knocking ba.
Jin an buɗe kofa kai tsaye yasa ya ɗago da sauri,idanuwanshi suka harɗe cikin nata,wani irin baƙon yanayi ya fara kaiwa zuciyarshi ziyara,ita kuma zuciya ta kaiwa ƙwanya domin tantancewa saidai wannan lamarin yasha gaban tunaninshi,zuciyarshi ta kasa fahimtar yanayin balle ta tsaidar mishi da gurbi.
Wataa uwar harara na balla mishi bayan na sauke kai na kasa,idan da yanxun za'a bani makami a yarjemin nayi kisa ba shakka wannan shi ne gawar farko da zan raba shi da duniya.

Lumshe ido kawai yake yi,duk da bai san yanayin ko na meye ba,amma yasan yana jin daɗin shi,kamar lokaci ya tsaya a haka.
"Sir plsease forgive us we come to apologized don't ..."
Daga mata hannu yayi alamar tayi shiru.
Ita kuwa anty sadiya daman cikin tsoro take maganar yasa ta ja baki tai shiru.

"go to ur office",y faɗa cikin sanyin harshe kamar wanda ake mishi dole a maganar.
Kallo na tayi,nima na kalleta alama nai mata da ido da ta tafi ba komai zan kula.
Fita tayi jiki a macce,duk da wata zuciyarta na gayamata meenal zata ji da komai domin ta shirya,amma ta kasa samun natsuwa tuno waye shi ma mutunci ba imani balle tausayi zai iya binta da wani marin.

Shiru nayi dan yau ba jiya ba,taɓe baki nayi bayan na ɗago mun haɗa ido,a rai na nace,"Munafiki sai na fara sanin kai waye?meyesa kake bibiyar rayuwata sanan zan ji da kai".
Juyawa nayi zan fita har na kusa naji ya ce,"Wait!"
Kalmar da kawai yaji ta tunguɗu kanta ta fito,ya kan rasa meyesa akanta sai yaji ya kasa control ɗin kanshi sai yadda zuciyarshi kawai tayi da shi,yanzun daya tsayar da ita me zai ce mata?

Juyowa nayi,ba tare da na ce mishi komai ba gani nayi ko kallo na ma bai yima kusan minti biyu hakan yasa na juya,aiki kawai nake yi bazan juri cin mutunci ba.
"I say stop",ya ƙara furtawa can ƙasan maƙogaro.
Juyowa nayi,"na tsaya au so kake ka kuma marin nawa ne kamar yadda ka saba,wannan fuskar tafi ƙarfin ka mareta wancan ma rabon ayi ne da tsautsayi shi ma kuma na baka bashi",da hausa nayi mgnr,na kafe shi da mayun idano na,so kawai nake naji amsar da zai bani....

*#Comment*
*#Share*
*#Vote and like*
👏 *Please*

~Mrsbalarabe✍️~

*ƘAUNAR ƁOYE!!!*
_(THE SECRET LOVE!🖤)_

*Fatima Batula✍🏼*

_Wattpad:mrsbalarabe._

*Dedicated to my Anup(my happines) Allah ne kawai yasan irin son da nake yi miki, ke abun so ce dole duk wanda ya raɓeki ya soki, baki na bashi da kalaman godiya da nuna irin matsayinki a gurina sai dai kawai na ce ke ta musamman ce a cikin rayuwa ta, Allah yabaki Ify ya baki miji na gari. Amin thumma Amin.*

_Page_

_17-18_

✍ *✍ ǴǑĹĎĚŃ ṔĚŃ ŴŔĬŤĚŔŜ ÁŜŜǑĆĬÁŤĬǑŃ* ✍✍

*wɛ αrɛ вɛαrɛr's σf sσ  gσldєn pєn*
*wɛ wrítɛ αssídíσuslч pɛrcєívє nσ pαín,*
*sσ mαgícαl σur crєαtívє gσldєn pєn* ✍ *,вєhσld σur wσrds.α prσduct σf σur pєn* *,sαvσur σur wσrds, fσr ít wíll* *cαusє чσu nσ pαín.*

*Yadda Annabi, Tsira Da Amincin Allah Su Tabbata A gareshi, Yake Kirga Tasbihinsa.*

Daga Abdullahi bn Amr, Allah ya yarda da shi, yace; Na ga Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, yana kirga tasbihi da (yatsun) hannun damansa.

*INA MASOYAN LITATTAFAN KUNGIYAR GOLDEN PEN?*

*NESA TA ZO KUSA, TUNANIN RASHIN SAMUN NEXT PAGE YA ƘARE!.*

Kasance mutum na farko da zai fara karanta sabbin littattafan marubutan mu, a duk lokacin da muka yi typing. Kina/Kana iya samu, ta wannan damar ce kawai idan ka bi wannan links tare danna *LIKE* a shafin mu na Facebook zaka/zaki iya samun cigaba ko kuma ki samu duk littafin da kike buƙata namu daga farko.

https://www.facebook.com/Golden-Pen-Writers-Association-102095951667849/

Sai kun zo, kar ku manta a koda yaushe comments da sharhin ku yana ƙara mana ƙarfin gwiwa a wajen rubutu mai yawa.

_*Bismillahir~rahamanir~rahim*_

Wasu takardu ya miƙomin ba tare da ce komai ba,zuwa nayi na amsa,naso ya ce da ni wani abun,har na amsa na juya sai kuma na ja na tsaya,ina so na kure tantama ta,shi ne aljanin ko kuwa shi wani ne daban?hakan yasa na juyo,carab ido na cikin nashi,kamar dai yadda aljani na yake kafe ni da mayun idanuwanshi,ban yi ƙasa a gwiwa ba naje har gaban shi .
Shi kuwa ƙura mata ido kawai yake yi,yana jin wani irin abu akanta ,wanda shi kanshi ya gamsu da hakan,zuciyarshi yaji ta shaƙu da ita,ta amince da ita tamkar ita ce masosiyar shi,tamkar yayi shekarun rayuwarshi da ita ,ba zai iya raudarar kanshi akan yadda yake ji akanta ba,samethings secret,either lv or reletionship whch ya kasa ganewa wanne a ciki but zuciyarshi ta shaƙu da ita ruhi da rai sun shaƙu da ita,ido ya lamunce ma,tunani ya yarda da yin tunaninta,wht all means?
Tambayar kanshi ya shiga yi,yana son sanin amsar tambayar,tunda shi dai ba yaro ba ne 34yrs yasan abunda yake yi,kuma yasan meye so meye sha'awa meye burgewa,meye ƴan uwantaka,kuma duk yasan yadda ake ji,to amma ita ya kasa gane lamarin domin ji yake ta

shiga kowanni matsayi daga ciki.

"Na amince ina sonka zan rayu da kai,kamar yadda ka yi fata,zan so ka so na amana,zan ƙauna ce ka,ƙauna me daraja da muƙami,zan kuma sallama kai na gareka,zan bika duk inda ka ja ni,zan kuma zaunar da kai a can cikin zuciyata na baka sarauta a faɗar zuciyata kayi mulki yadda ka so",cikin wata irin siga wacce ni kaina ban ɗauka zanyi har haka ba,ni kaina naji daɗin kalaman musamman muryar da nayi mgnr da su me sanyin da ni kaina ta taɓamin zuciya balle mai sauraro,lumshe fararan idanuwa na nayi bayan na sauke hannu na daga ƙirjina,tare da sakar mishi wani irin mayaudarin kallo,kai ka rantse da Allah soyayyarce yadda na narke na bararraje tamkar wacce ta nutse kogin so da ƙauna.
Wani irin murmushi na kuma sakewa ganin tarko na ya faɗa,ta tabbata shi ɗin ne kenan??

Karo na farko a rayuwarshi da yaji nadamar jin hausa ta kamashi,ina ma daya jin hausa?ina ma ina ma?da yaji maganganun da suka fi komai daɗi,duk da hakan ma yaji cewa wannan jin wannan yaren wannan kalamomin sunfi komai zamtowa magana mafi daɗi daya taɓa ji a rayuwarshi,duk da baya ji amma yaji zuciyarshi ta rungumesu,har ta sanyaya da jinsu.
Cikin wani irin salo yake lumshe idanuwanshi murmushi ya sakar mata wanda yafi to daga can ƙasan zuciyarshi mai tattare da saƙon naji na yava kuma na amince.
Nima dariyar murmushin na maida mishi da martani.
Knocking ake yi ina ji kamar yadda nasan shi ma yana ji,amma ba mu iya bada umarnin shigowa ba,nidai badan nayi nisan da yayi ba,kawai dan na ƙara ɗana tarko na ya ɗano,yadda zanji daɗin yin aiki na.
Shigowar da muka ji anyi ne yasa duk muka juyo ga kallon mu gurin wanda y shigo ɗin .
PA ce,ganin irin yadda muke kallon juna wanda ba wanda zai ce mu ba masoya ba ne,yasa ta ɓata rai wani irin kishi ya turnuko mata kamar ta haɗiye kanta, ta ma kasa faɗin abunda ya kawota sai wani ƙuramin ido take yi,ni kuwa da ba ganwar lasa ba na maida mata da raddi.
Tare da faɗin,"Meke tafe da ke?
Da turanci nayi maganar ba ƙarya ni kaina nasan ni gwana ce,dan bana yi ne sosai bai dame ni ba,ko su anty sadiya da turanci suke min mgn amma ni da hausa nake maida musu,ina kishin yare na,shiyasa yafi zama raɗan a baki na,daman shi turanci nan ne gurinshi inda zai yi nashi bajintar.
Bai kalli niba,saidai kawai ya lumshe ido almar na taimaki bakinshi da yin tambayar.
Ɗafa hannayena nayi kan dex ɗin,kallonta nake yi ina jiran amsarta,nifa sakatariyace wannan aiki na ne,cikin nuna gwanancewa ga aikin na kuma cewa,"ba zaki yi magana ba ne?"
Mamaki kam ta gama yinshi yarinyar da ko jiya saida tasha mari a gurin shi,bayan disge da zagin da ta sha,yanzun kuma ita ce,ta ma rasa me zata kira ta da shi.
"An haɗu a gurin meeting ɗin ku kaɗai ake jira",tana faɗa ta juya.
Har ta murɗa kofa na tsayar da ita,juyowa ta kuma yi saida na gama ƙare mata kallo cikin izza da taƙama kana na ce,"karki kuma shigowa ba tare da an baki umarni ba,ya zama lastwarning".
Harda ɗan zare ido Pa tayi nashan mamaki,lallai ma yarinyar nan yaushe ta zo?
"u can go",na ce da ita ina ƙara karya murya.
Fita tayi jiki a sanyaye,juyowa gareshi nayi ,"Zamu iya tafiya?".
Na faɗa ina kallonshi,shi ma yana kallo na,na so yace wani abu,amma hanzari ba gudu ba.

Bai ce da ita komai ba,ya tashi,ni na fara gaba shi kuma ya biyo bayana.
Idan ka ga yadda muke tafiar abun burgewa shi ma sanyin jiki ne da shi,haka nima abun gwanin burgewa.
Ko da muka isa ni,na fara shiga,gurin zaman mu yana kusa da juna,naja mishi kujera cikin nuna kulawa shi kuwa ya zauna,nima zaman nayi.
Carab muka haɗa ido da Anty sadiya,ban san lokacin da na sake wani irin murmushi ba,ganin yadda ta sake baki da ido da hanci tana kallo na.

Tiryan-tiryan aka gabatar da Meeting ɗin akan wani sabon abu da kamfanin ke shirin yi,kasantuwar na sakawa rai na yin aiki kuma,am gurowa ba nature not by nashi,yasa duk naji na iya,nima na tashi na bada tawa shawarar da gudunmuwa,kuma abunda yafi min daɗi shi ne ƴan arewa na amfana da kayan,kamar dan su ake so ayi ma,dan sun fi amfani da shi,wannan yasa naji daɗi,duk da kafirshin su mun ƙaro da su,kuma su ma sun ƙaro damu.
Taɓi akai ta yimin dan na burge Allah yayi min hikimar yin magana me tattare da fa'idoji,duk nai mgn tana zuwa da cikakken nazari,shiyasa nan da nan na kwanta musu rai,wanda suka kawo manhajar kuwa sai yabo na suke.
Ogawa kuwa da tunda ta fara mgnr yake jin wani irin abu,bai taɓa samun sakatariya me hazaƙa irinta ba,dan shi bai ce komai ba,yana nan zaune yana bin duk wani motsinta da kallo.
Lumshe ido kawai yake yi,komai na ta abun burgewa faɗa tsiwa ga kuma sanyi.a faƙaice yake sakin murmushi,duk sai yaji ya canja ya,wani irin canji na daban.
Anty Sadiya kuwa da tsabar mamaki ta ma kasa cewa komai ido kawai ita ma ta zuva,wani irin daɗi ne ke ratsa ta har kwanya.
Meenal ɗinta ce haka ko kuwa?.

Bayan meeting ya watse duk sun tafi bayan sun gama jinjina min,saidai abu ɗaya sam naƙi yarda su taɓa ni,wasu ma basu yi gigin nan ba,wasu kuwa sunyi ko hannu ban basu,van yarda da wannan zancen ba.
Ban bi ta kanshi ba,nai gurin ƴar uwata domin ƙanƙare mata tantamar da take yi.
"Oum Baƙir yadai ya kika ga aikin Anty Baƙir,"cikin zolaya nayi mgnr na riƙo hannunta muka fito,hanyar office ɗinta muka nufa.
Tsayawa tayi,"Meenal!
"Yes i am Meenal ɗin Maama".
"Meenal!rungume ni tayi ni kuwa dariya nayi ni kaina naji mmki dan wai ina speach a mkaranta bashi zai bani confidence ɗin abunda nayi yanzun ba,ni kaina sai naji na ƙara yarda da kaina,na kuma godewa Allah ,magana cikin mutane masu basira da fasaha da kaifin kwakwalawa a matsayina me ƙaramin ilimi da mamaki,sannan kuma mgnr da duk aka amincemin da ita.
Wannan wata nasara ce,dana samu.
Janta nayi muka ƙarasa cikin office ɗin na zaunar da ita akan kujerarta.
"Meenal ɗinki tafi haka karki yi mamaki".

"Am proud of u Meenal".
"Am alwys dare for u My Anty".

Jin jina min kai kawai tayi tare da share ƴar kwallar da ta fito mata.
"Bari naje office akwai abunda zan duba,"na ina kallonta ina murmushi ban san irin son da nake yiwa Anty Sadiya ba,to ita na buɗe ido na gani.
Ɗagamin kai itama tayi.
Na juya na fita,ina tafiya ina tunani,"ya kamata ya fito fili ai tunda yanzun dai na amice da abunda yake so ɗin?amma bai ce komai ba,duk da naga alamar cewa yaji daɗin amincewar tawa,to me zai saka yayi shiru?ina ce abunda yake son ji kenan??
Bangazar da naji anyimin wacce har saida yasa wayar da ke hannuwana faɗuwa ƙasa,yasa na tsaida tunanin da nake yi,runtse ido nayi ina jin ƙuno wacce irin bangaza ce haka,ga zafin da naji ƙirjina yana yimin.
"Baki gani ne?"
A zabure na buɗe ido na juyo,wani ma'aikaci ne kana ganinshi ka ga arne koɗaɗɗe.
"Kai ne baka gani taya zaka bangaje ni da gangar",cikin ƙunar rai nace haka dan wannan da biyu,bangazar juna cikin rashin sani kafaɗu ke haɗewa ba ƙarjiba.
"Da gangar kuma?"
"Eh idan ba haka ba,taya zaka bigeni a..."
Ba zata iya ƙarasa kalmar hakan yasa tayi shiru.
"A ina?daman ai ku musulmai baku....
"enought don't ever dare u,say dt word",cikin zafin zuciya da nayi maganar,rai a ɓace.
Tsaki naji na duƙa na ɗau wayata nabar gurin,office ɗina na koma,zama nayi kan kujerata.
Xan iya kuwa sam  zan iya zama cikin mutanen da basu san ƙima da darajar musulunci ba kuwa?
Nasan dole zan fuskanci waɗan nan ƙalubelen,but  i have to fulfilled my job I have to take my revenge, nannauyar ajiyar zuciya na sauke,i can't wait anylonger ina son sanin shi waye,shi ne ma ko ba shi ba ne??raguwar ajiyar zuciya na sauke,bana so ya kasance ba shi ne aljani na ba?girgiza kai nayi,taya zai kasance ba shi ba,ganin kai na ya fara zafi yasa na washe idanuwana tare da janyo takardun dake gurin na buɗe computer da ke gurin ita ma ƙirar iphone.

Kwantar da kanshi yayi saman lallausar kujerarshi yana ɗan juyata da jikinshi,tana wainashi kaɗan-kaɗan.
Ji yake ya matuƙar canjawa wani irin canji wanda bai san irinshi,ya kuma so emotion,kuma kuma a da ba haka yake ba.
A ɓari gudu kuwa na zuciarshi hasko min ita kawai take yi,lumshe ido ya hau yi a inda kunnuwanshi suka hau tariyo mishi kalamanta tiryan tiryan.
_Na amince ina sonka zan ƙaunace ka,kamar yadda kayi fata zan soka so na amana,zan ƙaunace ka ƙauna me daraja da muƙami xan sallama kai na gareka,zan bika duk ina ka ja ni,zan baka zan baka guri a cikin zuciyata,na baka sarauta a faɗar zuciyata kayi mulki yadda ka so"_

Kamar waƙa haka kalaman nata ke bijerowa cikin kunnuwanshi sai faman sakin murmushi yake yi,xai so sanin ma'anonin waɗan nan kalman masu daɗin gaske na faranta rai.
Ya lokaci ɗaya yake jin kamar tana ƙokarin sace shi kamar tana son mallakar komai nashi,ko yace shi ke son mallaka mata da kanshi,yaji yana son bata wani guri wanda baya tunanin kowa

ya taɓa gurin rayuwarshi kenan.
Ta ko ina a cikin zuciyarshi ita yake ji,a ko wani saƙo,meye wannan?meye wannan?yake tambayar zuciyarshi,ganin da yayi mata a haɗuwarsu ta farko shi ke dawo mishi.
Yadda ta sake jiki tana tsiwa murmushi yayi tuno ranar da ya watsa mata mari amma bakinta yaƙi mutuwa.
"Idiot!
Ya furta can ƙasan maƙogaro.

Ringin ɗin wayarshi yaji wanda hakan yasa ya dawo daga fegen daya faɗa,tunda yaji ringin ɗin wayar ya shaida waye me kiran.
"My love",sunan daya baiyana a kan wayar kenan,zubawa wayar ido yayi,yana jin ringin ɗin dake tashi ƙasa-ƙasa na wayar starboy,har kiran ya katse bai ɗauka ba,saida ya kuma shigowa sanan ya ɗauka.

"Hello dear kana ina?ka zo yanzun muna asibiti jikin momy ya tashi".
"What?"
Ya faɗa tare da tashi tsaye zumbur,"am coming". Kitt ya katse wayar,bai koma ya zauna ba ya fito daga office ɗin cikin hanzari da sarsarfa ya isa fita daga office ɗin.
Su dai ma'aikata nasu ido.
 Cikin hanzari yaja motor da guduu ƙiii yabar famfanin,kai tsaye asibitin ya nufa dan yasan can ne inda suke kwanciya,asibitin na ƙanwar Momyn ne ma,mahaifiyar Taye na familly ne dai asibitin,yana haɗe da gidansu tayen ne.
Tunda naisa ya dunga buga horn getman yana ji ya wangle katafaren get ɗin.
Bai kai ma inda ake farking ɗin ba ya tsaida motor,ya fito. Jikinshi har rawa yake yi ɗakin ya nufa inda yasan nan ne ake ajiyeta duk sanda hawan jininta ya  tashi.
Tsaye ya tsaya tuɓuss.
 "Hmm yaron Momynshi kenan kin ganshi kamar a sama ya tawo",suna kama da Momyn sosai.
Tashi tayi taje har bakin ƙofar ta rungumeshi,"My son,kuma inlow ɗina  ƙaraso ciki mana",ta janyo hannuwanshi har gurin kujerar da Tayen ke zaune ita da Momyn,zama yayi a tsakiyarsu,tare da kallon Momyn tashi wacce sai washan baki take yi.
"Idan ba haka aka ce ba,ba zuwan zaka yi ba".
"But u know how worry i.."
  "am sorry nothing happen to me am fine,kai ne ai very stuborn".
Ɗan faɗa rai yayi dan sun ruɗar dashi matuƙa.
Saƙwalo hannuwanta tayi ta gafenshi ta ɗan ƙwantar da jikinta kan kaɗarshi,"Sorry Dear i don't mean to hot u,Momy ce tace nace ma haka".
Shiru yayi ba tare da yace mata komai ba.
Kallon maman tayen yayi,"Ya gida Momy?ya aiki?"

"yanzun an manta da ni,ba'a zuwa guri na".

"is not like dt,aiki ne suka min yawa a office shiyasa".

"I see,jiya an gayamin ka faɗi a motor,naje yau da safe wai ka tafi aiki,nace meyesa bata hanaka ba,shi ne na haɗa wannan plan ɗin cox i wont to see u".
Ɗan murmushi  yayi yasan shi ɗan gata ne,yana samun soyayya daga garesu sosai.

Fira suka yi sosai yana ɗan jefa tashi kaɗan-kaɗan ba ma ma'abocin son magana ba ne shi,bayan sun gama firar a inda firar duk ta fi ta labarin bikinsu da taye,duk sun ƙosa a wayi gari ta samu ciki,ba zasu bari ya wani girma ba zasu saka ranar bikin,son yara a jininsu yake duk su ɗin,ba Tayen ba ita da Momynt ba shi ba ba tashi uwar ba.
Duk sun fishi so ma,duk da shi ma yana so.
Fita suka yi wai zasu siyayya suka bar su,su kaɗai ɗakinta Taye ta ja shi.
Dan kafin shigowarshi sun bata wani magani wanda aka tabbar musu yana kwanciya da ita a lokacin to ba makawa zata ɗau ciki.
Daman da biyu suka kirashi ɗin.
Shi kuma da daman yana cikin yanayin kasala da mutuwar jiki,hakan yasa ya amshi tayinta da hannu bibbiyu..
Nan suka hau jiyar da juna daɗin rayuwa,saita taye ta tabbar da ta mantar dashi komai ya fita haiyacinshi,dan duk jarumtarshi wannan faninin susucewa yake yi.
"I love u Taye zan yi rayuwa da ke kaɗai ne,nayi miki alƙawari bazan taɓa bawa wata kai na ba bayan ke
....u are d only one who have right akai na,am  your's  har abada,Taye ba wata maccen da zata kai ki .... Ke ba irin su ba ce...kin fi su...."
Shi dai yaji yana suburbuɗo zance,amma bai san kansu ba.
Ko da ta soma ƴanke ƙauna ga  samun nagartaciyyar soyayyar  Dany,a wannan fanin take samun gamsuwar yana son ta,kawai dai shi haka yake baya yin abu da zafi-zafi,domin  sosai take yarda da amincewa da kalamanci,musamman idan ta tuno shi mutum ne me magana ɗaya da kuma cika alƙawari,shiyasa ta ƙore ta huro take kuma gyara kanta,shiyasa kullum yake jinta savuwa kuma daban,daɗinta kullum sabonta yake mishi.

*** **** ***

Ban tsaya ba saida na tabbar da nayi duk abunda ya kamata nayi,sannan na tsaya lumshe ido nayi na gaji ga wata uwar zufa da takw ketomin,"gaskiya aiki da wuya".
Ban tabbatar ba,saida nayi tuzali da agogon dake office ɗin.Zaro ido nayi ƙarfe uku da rabi banyi sallah ba..
Tsaye na tashi,ina tunanin lokacin da muka fito daga meeting ƙarfe sha ɗaya da hamsin da wani abu,haka na ɗau lokaci gurin wannan aikin.
Tsaki naja  na takaicin rashin jin kiran Sallar da ba'ayi,ai dole kuwa a shafawa gurin yi inba wanda yaɗau sallah kaya ba,ji dai yanzun ina zaune ina aiki har lokaci yayi haka,irin haka ai sai ga buɗe ido ka ga ma anyi sallar maqrib.
Ina wannan tunanin ne,ina alwala a vayin da ke office ɗin.
Fitowa nayi aiki ja,wato sallaya ina zan samota,ni kuma ban yarda da wannan gurin ba,abun haushi kuma ba hijjabi na saka ba,balle na cire ɗan kwalina na shimfiɗa,haka nan na samu nayi dabara nayi sallar ina idarwa na tadda la'asar.

Bayan na idar na zauna nayi azkar kamar yadda na saba,sanan na tashi naje na zauna ina jin gajiya.
Tunaninshi na fara yi  ya kamata yace wani abu ai,wannan kalaman idan har masoyi yaji su to dole zai ce wani abu.Azalzata xuciyata naji ta fara yi,dan a ɗabi'ance haka ne,ina son sanin shi ɗin ne?.
Deepbreath nayi bai ƙarfe .
"cool down Meenal!
Na faɗa da ɗan ƙarfina tare da furza isa daga bakina,zanca tunani nayi akan cewa to ko dai yana so yaja aji ne,ganinshi babban mutum ne ma matsayi da daraja.
"Mtsewww wani girma da daraja ga kafiri".
In badan ina son ɗaukar fansa ai ni da tuni na gama gaba ne,kan me zan zauna ɓata lokaci na da tunani ga kafira.
Wani tsakin na kuma ja tare da yin fatan Allah ya kawomin lokacin da zan bar garin ma gaba ɗaya.
"i have to do something",na faɗa bayan na tashi tsaye fita nayi office ɗinshi na nufa tunda banga ta zama ba.
  Banyi knocking ba na kunna kai wayam ba mutum ba alamarsu.
Tsaki na kuma ja iya laɓɓa na.
  "ina kuma yaje daman ai duk abunda aka haɗa da jaki sai ya ci kara",na faɗa bayan na juya na fita.
Securityn gurin na tambaya ko sun ganshi,suka ce min ya fita yana sauri da alama gida za shi wani abun ne na gaggawa ya tashi,taɓe baki nayi na koma office ɗina na zauna.
Wayata na ɗauko text na rubutawa Anty Sadiya.
"Besty ya aiki?
Murmushi nayi lokacin muna makaranta ita ce besty na,idan nun dawo gida Anty idan muna makaranta besty.

Daman ita ma ta gama abunda take yi,zama tayi tana ƴan dube-dubenta a wayar,tana jin shigowar saƙon ta duba,ita ma dariyan tayi .

"Alhmdllh Besty ya naki aikin?ah tunda ke expect ce ba wani gajiyar da zaki yi".

Murmushi Meenal tayi bayan ta karanta.

"Ban kai ki ba ai,gani nan a gajiye yau muna zuwa gida zan kwanta dan barci ma nake ji".
Sai yanzun na tuno da fitar da zamu yiba,muka fasa bayan kuma munce wa matar zamu zo,ya kamata muje gaskiya.
Kallon agogo nayi wanda ya nuna min ƙarfe shidda da rabi,lokaci naja.
Tunda oga baya nan yanzun ni ce zanyi sallama ta hanyar danna ƙararrawa.
"Zamu tashi da wuri yau,kafin muje gida sai mu biya inda kike ce zamu tunda mun sanar da ita,bai kamata kuma tashi shiru ba" .
Na turawa anty sadiya.

"Hmm manya aiki fa yazo gurin manya za a saka ya sallame mu kenan da wuri,"dan ita bata kawo baya nan ba ma.
Ni ban ma duba replay ɗinta ba,na tashi na faɗa bayi dan ɗauro alwala,ina aiyanawa rai na Sallar isha'i a gida zan yi ta.
Ina fitowa na tada dan lokacinta yayi.
Bayan na idar na gabatar da azkar ɗi na na yamma sannan na tashi.
Lokacin bakwai tayi shiri na fara yi duk da bazan tafi da komai gida ba,dan duk mafi yawan ma'aikatan da computer suke tafiya gida harda anty sadiya.
Na kimtsa tsab na fito kai tsaye office ɗin nashi na nufa,gurin madannin naje na danna ina dannawa nai fitowa ta.

Naga alamun mamaki ƙarara tun gurin security ɗin,ni kuwa nai murtsitsi abuna na taka cikin isa da ƙasaita har office ɗin Anty na.
Tunda taji ƙarar gabanta ya faɗi,ta tambayi wani ma'aikaci da yazo kawota wasu takardu meke faruwa,ya ce oga baya nan ya fita tun ɗazun sakatariya ce tayi sallamar.

Daman tasan haka Meenal take idan ta ce xata yi abu to fa zata yi shi ne,ba tsro balle fargaba,a tarihin ma'aikatar bai fi sau ɗaya aka taɓa sallama bakwai da wani abu ba,ana dai yi takwas tara.

"Ki fito muje,"na katse mata tunanin da ta faɗa.
Firgitt tayi tana cigaba da shan mamakin Meenal da ƙarfin hali.
Ƙarasa shigowa nayi,"bai kamata ace kina mamakin ƴar uwarki har yanzun,trust me kawai nasan abunda nake yi".

"gaskiya banga alama ba Meenal,baki tsoron abunda zai biyo baya idan yaji".

"Pair! ba ina son zama gwana ba ce,da yasa bana jin tsoro akan abunda zanyi,haka nake i do wht ever a want to do,me zai faru is my job nifa sakatariya ce,i have right to do my job,ban karya doka ba,kawai nayi yadda nake so ne",cikin karfin gwiwa nake zaro kalaman da nake sarrafasu haɗe da hannuwana wanda nake nuna da kai na,da kuma matsayina.

Duk da gaskiya ta faɗa amma ita dai har yanzun jikinta a sanyaye yake,dan tasan lallai sai an kira an gayamishi tun yanzun.

Jan ta nayi muka fito,"ni muje".

Bayan mun shiga motor ta ja ,"ina so na iya tuƙi ba,ko zaki bani na koya".

Zaro ido anty sadiyar tayi,"wuu rufa ma Ɓakir asiri tausaya mishi yayi ko da wayau ne da iyayenshi".

Dariya na fashe da ita sosai wacce na manta rabon da nayi irinta.

Ita ma dariyar tayi,muna tafe muna fira,da yake gidan na ɗan nisa hakan yasa muka ɗau lokaci kafin mu isa,a tanƙamemen get ɗin na alfarma muka tsaya muna hon,saida security ya fito zuge glss ɗin Anty sadiya tayi.
Murmushi,"Tun ɗazun aka sanar mana da zuwan ku,barka kun zo lafiya",yai mgnr cikin raha.
Anty Sadiya ce ta amsa mishi ni kuwa ko kallo bai ishe ni ba.

Get ɗin aka buɗe mana,wai yadda kasan rana tsabar hasken tsagar gidan wanda ya haska ƙyayataccen gidan.

A tare muka sauka bayan mun tsaida motor,kallonta nayi muka yiwa juna ɗan murmushi kafin muka nufi kofar da zata sada mu da falon.

Turuss muka kusa cin karo da juna,ja yayi ya tsaya.
Kyakykyawa ne ajin farko gashi fari tasss zubin fulanin asali,ga hutu da boko zun ratsa shi,ɗan gaye na na ƙarshe,sakin wannan kyakyawar fuskar yayi wacce daman me annurin ce,murmushi yayi wanda ya bawa fararen haƙuranshi damar baiyana.

"Munyi fushi tunda sai yanzun kuka zo",da harshen hausa yayi maganar.

Hakan da naji yasa na ɗago mukai two eye da shi,hausa kai yaushe rabon da naji hausa irin haka.

Wani lafiyayyan murmushi ya sakar mata,ita ma ta maida mishi martani,ya burgeta dubi da yadda yake ya ga dama yace shi bai taɓa jin hausa ba ma,kuma ta zauna,dan yadda yake mugun yanayi da indiyawa harda sirintar ma,amma ji hausa raɗam a bakinshi.

"Maraba ku shigo,"ya faɗa bayan yayi gaba,yai mana jagora har tsakiyan tankamemen falon.

"Anty rabi'ah kin gansu wai sai yanzun,"cike da zazzaƙar muryarshi yake kiran na ta".

Juyowa yayi gare mu,"ku xauna dan Allah".

Ni da har lokacin murmushi nake saki dan jin hausa a bakinshi yasa naji ya burge ni ƙwarai.
Zaman muka yi muna zama ta fito.
Babbar macce me jini a jika,ita ma fara ce sol zubin fulanin,fuskarta ɗauke da annuri.

" *Khaleed* su waye kake maga....." bata iya ƙarasawa ba,ganin mu da tayi,da murna ta isa gurin Anty sadiyar rungumar juna suka yi.

"Haba oum Ɓakir tun ɗazun,muna ta jira ai da kin gayamin sai kun taso daga gurin aiki".

"Kyi hakuri wllh da ba aikin zamu ba,har mun fito sai aka kira mu shiyasa".

Sakin Anty Sadiya tayi tayo kai na,rungume ni tayi,naji wani irin banbara kwai.

"Meenal muna ta jiranki tun ɗazun,Khaleed daga jin nace zaku zo,ke daga arewa kike yaƙi fita shi dole zai ya jira ki ya ganki,ya samu abokiya ƴar arewa,wacce zasu na hausa, daman baya son hausarshi ta gudu....."

Kallonshi nayi,wanda shi ma daman idonshi na kai na,murmushi na sakar mishi......

_Kai wai ya naji sai typing nake yi,ba gajiya,hmm ban gaji ba haka zan dai barku idan naji ruwan comment na dawo.Amm gaskiya duk grp ɗin da nake tura muku da kaina baku yin comment yasin dainawa zanyi,dan lada ake sallah a to._

*I do love u my people,ƙaunar ɓoye fans,ku huta ku saki ranku kuna raina,ina mugun jin daɗin addu'o'inku gare ni.*

*#Comment*
*#Share*
*#Vote and like*
👏 *Please*

~Mrsbalarabe✍️~

*ƘAUNAR ƁOYE!!!*
_(THE SECRET LOVE!🖤)_

*Fatima Batula✍🏻*

_Wattpad:mrsbalarabe._

*Telegram*👇

https://t.me/joinchat/GxqDXvsOyg0Xr4s8

 *  Dedicated to my Anup(my happines) Allah ne kawai yasan irin son da nake yi miki, ke abun so ce dole duk wanda ya raɓeki ya soki, baki na bashi da kalaman godiya da nuna irin matsayinki a gurina sai dai kawai na ce ke ta musamman ce a cikin rayuwa ta, Allah yabaki Ify ya baki miji na gari. Amin thumma Amin.*

_Page_

_19-20_

✍ *✍ ǴÓĹD́ÉŃ ṔÉŃ ẂŔÍT́ÉŔŚ ÁŚŚÓĆÍÁT́ÍÓŃ* ✍✍

*wє αrє вєαrєr's σf sσ  gσldєn pєn*
*wє wrítє αssídíσuslч pєrcєívє nσ pαín,*
*sσ mαgícαl σur crєαtívє gσldєn pєn* ✍ *,вєhσld σur wσrds.α prσduct σf σur pєn* *,sαvσur σur wσrds, fσr ít wíll* *cαusє чσu nσ pαín.*

*INA MASOYAN LITATTAFAN KUNGIYAR GOLDEN PEN?*

*NESA TA ZO KUSA, TUNANIN RASHIN SAMUN NEXT PAGE YA ƘARE!.*

Kasance mutum na farko da zai fara karanta sabbin littattafan marubutan mu, a duk lokacin da muka yi typing. Kina/Kana iya samu, ta wannan damar ce kawai idan ka bi wannan links tare danna *LIKE* a shafin mu na Facebook zaka/zaki iya samun cigaba ko kuma ki samu duk littafin da kike buƙata namu daga farko.

https://www.facebook.com/Golden-Pen-Writers-Association-102095951667849/

Sai kun zo, kar ku manta a koda yaushe comments da sharhin ku yana ƙara mana ƙarfin gwiwa a wajen rubutu mai yawa.

*Addu'ar  Nema Wa 'Ya'ya Tsari.*

Manzon Allah, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya kasance yana nema wa Hassan

da Husain tsari da wannan addu'ar:

أُعِيذُكُمَا بِكَلِمَاتِ اللهِ التَّامَّة، مِنْ كُلِّ شَيْطَانٍ وَهَامَّةٍ، وَمِنْ كُلِّ عَيْنٍ لاَمَّةٍ.

O'eezukuma bikalimatil-lahit-tammah, min kulli shaytanin wahammah, wamin kulli 'aynin lammah.

Ina neman muku tsari da kalmomin Allah cikakku daga dukkan shaidan da wata dabba mai dafi, da kuma dukkan wani mai kambun baka, mai cutarwa.

_*Bismillahir~rahamanir~rahim*_

_Previously_

Kallonshi nayi,wanda shi ma daman idonshi na kai na,murmushi na sakar mishi.....

_Continueosly_

Shima Khaleed d'in wani k'ayataccen murmushi ya sakarmin mai d'auke da wasu sak'onnin da suka rikitamin dukkan lissafi nah.

Lumshe idona nayi tare da sake bud'e su a hankali na d'ora su akan kyakkyawar fuskarsa mai cike da haiba tare da kwarjini.

“Barka da zuwa”.

Na jiyo saukar sihirtacciyar muryarsa a cikin dodon kunnenah.

“Yawwa,Mun sameku lafiya?”.

Nima na fad'a cike da farin cikin jin hausarsa mai birgewa, kallon gefen da su Anty Sadiya suke nayi ashe wai harsun bar wurin sun wuce d'akin Anty Rabi'a,wata nannauyar ajiyar zuciya na sauke,ina jina normal.

“Bismillah, Ga ruwa kisha Meenal”.

Khaleed ya fad'a yana ajiye min tray mai d'auke da robar swan da cup d'aya.

Dariya nayi nace;

"Nagode da wannan karramawa".

Murmushi yayi min,

"Karki damu,kinsan ance baqonka Annabin ka,gaskiya naji dad'in had'uwa dake".

"Nima haka,Barin ma da naji ka iya Hausa sosai,tinda nazo banji Hausa irin taka ba".

Na k'arashe maganar ina d'aukar ruwan na b'alle murfin robar da zummar zubawa, da sauri Khaleed ya riqo hannu na wanda yin hakan yayi sanadiyar jin wani irin shock tare da wani bak'on yanayi,saurin janye hannun nayi ina kallonsa cike da mamaki.

Murmushi mai sauti yayi yace;

"Nine ya dace na zuba miki ba keba,karki wahalar da kanki".

Sai a lokacin na saki wata ajiyar zuciya,jin inda manufarsa ta dosa.

"Okey nagode".

Na fad'a ina karb'ar cup d'in da ya mik'o min wanda ya tsiyaya ruwan a ciki.

Ina qoqarin kai cup d'in bakina wayata ta hau ruri, dubanah nakai kan wayar naga number Anty Sadiya murmushi na saki sannan na d'aga wayar ina fad'in,

"Anty Sady yane?".

Dariya tayi tace;

"Lallai Meenal Sannunki,to Anty Rabi'a tace in tambaye ki wurin ta kikazo ko wurin Khaleed?".

Wata kunya naji ta kamani wacce bansan ma'anar ta ba, sannan naji wata irin fad'uwar gaba ta riskeni,da sauri nace;

"Wurinta nazo wallahi,kuna ta ina ne?".

"Ki shigo d'aki mai kallon ki muna ciki".

Aunty Sadiya ta fad’a sannan ta katse wayar.

Miqewa nayi ina gyara mayafina, ganin hakan Yasa Khaleed kallona yace;

“Ya haka kuma?,ina zakije gashi ko ruwan da na kawo miki baki sha ba”.

D’an murmushi nayi sannan na d’au ruwan nayi kurb’a biyu na ajiye tare da fad’in,

“Thanks, bara na samesu”.

Ban jira amsarsa ba na wuce hanyar da zata kaini cikin d’akin Anty Rabi’a,ina jin yanda idanunsa ke yawo a kaina.

Ina shiga Bak’ir yayo kaina ya rungume ni yayinda idon su Anty Sadiya yake a kaina wanda har saida naji na tsargu da kallon da suke min,d’aukar Bak’ir nayi muka zauna gefen Anty Sadiya,basu cemin komai ba sukaci gaba da firar su, nikuma naciro wayata na kamo muna game d’in Candy Crush nida Bak’ir,.

Saida suka sha firarsu mai isarsu, sannan Anty Rabi’ah tace muje dainy don cin abinci, dukan mu dainy muka nufa achan muka tarar da Khaleed zaune yana danna wayarsa da alama chart yake,Anty Rabi’a ce tayi sarving d’in mu kowa ya fara cin Abincin shi, inda suka dasa wata sabuwar fira kamar wasu ‘yan jarida, ni haushima suka fara ban jin duk yawancin firar tasu da turanci suke, kuma ba akan al’adar mu suke tattaunawa ba,haba gaskiya Lagos batayi ba,mutum d’an bahaushe amma kaga ya juye baki ya koma inyamurin k’arfi da yaji,haba me ake da qasar arna?marasa tsalki.

Jikinane ya bani ana kallona hakan yasa ni d’ago fuskata, idanuwanmu ne suka sark’e cikin na juna wanda ya haifar min da wata irin fad’uwar gaba,da sauri na janye idanuna na sadda kaina qasa ina mamakin wannan bak’on yanayin dake neman rikitamin lissafi.

“Meenal!,haka kike dama bakya fira?”.

Anty Rabi’a ta fad’a fuskarta d’auke da murmushi.

kamin inkai da magana Anty Sadiya tayi saurin fad’in,

“Chapp aikuwa Meenal gwana ce wurin surutu, bata dai ga damar yi ba”.

Murmushi kawai nayi bance komai ba,inda Anty Rabi’a tace;

“To maybe kunyata takeji shiyasa bata fira da ni”.

Dariyar da ban shirya ba nayi nace;

“Ke Anty nah ce,mezaisa naji kunyarki?,kamar yanda Anty Sady ta fad’a banajin yin firar ne”.

Dukan su dariya sukayi,Agogon dake manne jikin bangon d’akin na kalla naga lokacin sallah yayi.

Guntun tsaki nayi cike da jin haushi,ace ga lokacin sallah yayi amma baka jin kiran sallah,wannan wane irin bala’i ne haka?.

“Zanyi sallah Anty”.

Na fad’a ina kallon Mamallakiyar gidan,wato Anty Rabi’a.

“Au anyi sallar kenan?,bara muma muje muyi”.

Anty Rabi’a ta fad’a tana miqewa muma miqewa mukayi a tare, inda na kai kallona wurin Khaleed naga ko alamar motsi baida ballantana yayi zummar tashi zuwa sallar hasalima hankalinsa na kan wayarsa,tsayuwata na gyara nace;

“To Oga, kai bazakayi sallar ba ne”.

D’agowa yayi ya kalleni tare da sakar min murmushi yace;

“Zanyi,akwai abinda nakeyi ne”.

Zaro ido nayi a mamakance nace;

“Tofah!, har akwai wani abu da yafi sallah muhimmanci?,au kaima kace ka fara bin ak’idar arnan nan, nan gaba ma kila sallar ma bazakayi ba”.

Dafe kai yayi yana dariya yace;

“Kai Meenal, ni ba hakan nake nufi ba,Bara naje dai nayi sallar nan”.

Ya k’arashe maganar yana miqewa har lokacin fuskarsa d’auke da murmushi yana kallon Masifaffiya for real wato Meenal.

Ban ce komai ba nabi bayan su Anty Sadiya da suka bar wurin tin d’azun, yayin da Khaleed ya fice daga gidan.

Bayan mun qare sallar ne, Anty Sadiya tace zamu wuce gida,sosai Anty Rabi ta nuna bata son mu wuce, wai abar mata ni na kwana gidan, a raina nace taff a ina zan kwana?,Allah shi kiyaye

ai gidan Anty Sady kawai zan iya kwana injini a salkake, amma duk inda na kwana ji zanyi kamar na koma arniya nima.

“Meenal zaki kwana ko?”.

Murmushin yaqe nayi mata nace;

“Dayake Anty akwai wani aikin office da na bari a gida,ina so idan na koma in qarasa”.

Kallona Anty Sadiya tayi cike da mamaki, nikuwa na fuske na d’auke kaina kamar gaskene, inda Anty Rabi’a tace;

“To shikenan Meenal, idan kinyi free promise me zaki zo ki kwanar min”.

Sosa kai nayi don nasan wannan alqawalin bazai yiwuba sam,

“Insha Allah”.

Na fad’a ina miqewa ganin Anty Sadiya ma ta miqe alamar dai tafiya zamuyi, d’aukar Bak’ir nayi ganin yanata lumshe ido da alama ma bacci yake ji, wata leda Anty Rabi’a ta miqamin tace;

“Ga wannan Meenal, ba yawa”.

Karb’ar ledar nayi ba kunya nace;

“Nagode Anty,Allah saka da alkhairi”.

Da Ameen muka amsa sanna muka nufi hanyar da zata kaimu pallor ta fitar damu waje, banga Khaleed ba da alama bai dawo sallar ba.

Sallama mukayi ma Anty Rabi’a muka shige motar mu Anty Sadiya ta bata wuta muka fice daga gidan,saida Anty Sadiya ta biya wani Restaurant ta siya muna Burger da Ice cream sannan muka koma gida a gajiye.

Bayan Anty Sadiya nabi zuwa d’akin ta domin kwantar da Bak’ir da yayi bacci, ina fitowa na wuce d’akina, kayan jikina na cire na d’aura towel na shige bathroom domin watsa ruwa don inji dad’in bacci.

Koda na fito Cream kawai na shafa ma jikina, na zuba wata doguwar rigar bacci, wutar d’akin na kashe nayi kwanciyata don wani irin lafiyayyen bacci nakeji.

Asuba Ta Gari Meenal🥰

*#Comments*
*#Share*
*#Vote and like*

~Mrsbalarabe✍️~

*ƘAUNAR ƁOYE!!!*
_(THE SECRET LOVE!🖤)_

*Fatima Batula✍🏼*

_Wattpad:mrsbalarabe._

*Telegram*👇
https://t.me/joinchat/GxqDXvsOyg0Xr4s8

* Dedicated to my Anup(my happines) Allah ne kawai yasan irin son da nake yi miki, ke abun so ce dole duk wanda ya raɓeki ya soki, baki na bashi da kalaman godiya da nuna irin matsayinki a gurina sai dai kawai na ce ke ta musamman ce a cikin rayuwa ta, Allah yabaki Ify ya baki miji na gari. Amin thumma Amin.*

_Page_

_21-22_

✍ *✍ G̊O̊L̊D̊E̊N̊ P̊E̊N̊ W̊R̊I̊T̊E̊R̊S̊ ÅS̊S̊O̊C̊I̊ÅT̊I̊O̊N̊* ✍✍

*wɛ αrɛ вɛαrɛr's σf sσ gσldɛn pɛn*
*wɛ wrítɛ αssídíσuslч pɛrcɛívɛ nσ pαín,*
*sσ mαgícαl σur crɛαtívɛ gσldɛn pɛn* ✍ *,вɛhσld σur wσrds.α prσduct σf σur pɛn* *,sαvσur σur wσrds, fσr ít wíll* *cαusɛ чσu nσ pαín.*

*INA MASOYAN LITATTAFAN KUNGIYAR GOLDEN PEN?*

*NESA TA ZO KUSA, TUNANIN RASHIN SAMUN NEXT PAGE YA ƘARE!.*

Kasance mutum na farko da zai fara karanta sabbin littattafan marubutan mu, a duk lokacin da muka yi typing. Kina/Kana iya samu, ta wannan damar ce kawai idan ka bi wannan links tare danna *LIKE* a shafin mu na Facebook zaka/zaki iya samun cigaba ko kuma ki samu duk littafin da kike buƙata namu daga farko.

https://www.facebook.com/Golden-Pen-Writers-Association-102095951667849/

Sai kun zo, kar ku manta a koda yaushe comments da sharhin ku yana ƙara mana ƙarfin gwiwa a wajen rubutu mai yawa.

Addu'ar Korar Shaidan da Wasuwasinsa:

Ya nemi tsarin Allah daga shaidan.

أَعُوذُ بِاللهِ مِنَ الشَّيْطَانِ الرَّجِيمِ.

A'uzu billahi minash shaytanir rajeem (3)

Ya yi kiran sallah.

Yin zikiri (ambaton Allah) da karatun Alkur'ani.

_Bismillahir Rahmanir Rahim_

A B’angaren Sir Daniel shida Taye, sun kwana farantama junansu rai,daga baya bacci yayi awon gaba dasu k’arshe dai a wurin Taye ya kwana.

Da asuba Anty Sadiya ce ta tasheni kamar dai kullum dak’yar tasamu na tashi saboda baccin yayimin dad’i sosai, Ina kammala sallar Asuba, na nufi Kitchen don had’a muna abin kari, Arish da kwai na soya muna sannan na d’ora ruwan zafin tea, Ina dama ma Bak’ir custard Anty Sadiya ta shigo Kitchen d’in cikin riga da wando sun bala’in matseta, kawar da kai nayi ina jan tsaki a raina,nace;

“Ina kwana?”.

Saida ta zauna kan kujerar dake kitchen d’in tace;

“Lafiya Lau, kin tashi Ipy?”.

“Nima haka”.

Na bata amsa a tak’aice.

Murmushi tasaki tana fad’in,

“Yau me ake had’a muna ne?,naji gidan duk ya k’amsashe”.

Daidai lokacin Yaya ya shigo kitchen d’in shima.

“Tsiwa Baby Me ake dafa muna hakane??duk gidan ya cika da k’amshi”.

Shima ya jefomin kalar tambayar Anty Sadiya.

K’wafa nayi ina kallon shi fuskar nan tawa a tamke nace;

“Arish da Kwai”.

Yanda nayi maganar ne ya sanyasu dariya.

Anty Sadiya tace;

“To a gama lafiya,bara mutafi karmu dameki”.

Daga haka suka fice ita da Yaya suna maganar da bansan me suke cewa ba.

Kayan da na b’ata na shiga wankewa,na jero abinda na had’a a dainy,sannan na wuce d’akina don yin wanka.

Wani Sihirtaccen k’amshin turaren da nake jin kamar na tab’a jinsa ya doki hancina, amma na kasa tino inda na tab’a jinsa,chak na tsaya ina  k’arema ko ina na d’akin kallo don ba shakka k’amshin daga cikin d’akin yake fita, wani rass naji gabana ya bada da sauri na fice daga d’akin ban zarce ko ina ba sai d’akin Anty Sadiya ko sallama ban tsaya yiba na fad’a d’akin.

Mik’ewa tayi da sauri ganin yanda nashigo duk a hargitse.

“Meenal!,lafiya?”.

“Anty ke kika fesa turare a d’akina?”.

“Turare kuma?,Ni ban shiga d’akinki ba”.

“Me yake  faruwa ne?”.

Yaya da ya fito daga Bathroom ya tambaya yana kallon yanda mukayi cirko~cirko damu.

“K’amshin turare naji a d’akina,wallahi kamar anyi b’arin turare a ciki”.

Kallon juna sukayi Yaya yace;

“Muje d’akin inji”.

Dukan mu ficewa daga d’akin mukayi zuwa d’akina, ga baki d’aya jikina duk a sanyaye.

“Banji K’amshin komai ba Meenal”.

Cewar Anty Sadiya cike da mamaki.
Ganin yanda jikina yayi mugun sanyi yasanya Yaya yin shiru don naga bakinsa na motsi da alama dai shima baiji k’amshin ba, nikuwa ga k’amshi inaji kamar ana k’ara kosantoni da shi.

“Kaima Yaya bakaji ba?,Wai Anty Sadiya da gaske kike bakiji ba?”.

Hannuwana ta riqo tana fad’in,

“Eh Meenal, inaga kawai hancinkine ya baki amma mudai bamuji komai ba”.

Kai na gyad’a,Inajin wata irin jarumta tazo min,don nasan ba kowa bane sai aikin wannan d’an iskan,Yo d’an iska mana tinda dai ya hana rayuwata sukuni.

“Shikenan Anty bara nayi wanka”.

“Ki riqa addu’a kinji Sisy”.

Yaya ya fad’a yana min murmushi, nima murmushin na miyar masa ina fad’in,

“Insha Allah”.

Daga haka suka fice daga d’akin, bathroom na fad’a na watso ruwa

Ina fitowa daga wankan na nufi gaban Mirror na zauna,har lokacin kamshin baibar d’akin nawa ba, cream na shiga murzama jikina don banada lokacin shafa wasu tarkace a fuskata.

“Masoyiyatah!!!”.

Naji Saukar muryar da ko a cikin bacci zan iya sheda me ita a cikin dodon kunnena,kaina na dago da sauri karaf muka had’a ido dashi ta cikin Mirror zaune yake kan gadona yana min murmushi,cikin shigar k’ananan kaya,sak Oga Daniel,ni banga wani bambancin dake tsakanin su ba,hakan na nufin dai Oga Daniel ne ke rainamin hankali,Kenan tsafi yakeyi?,yana cikin Qungiyar matsafa?,Meyasa yake bibiyata?,Ko nima tsafin zaiyi dani?,na shiga jeroma kaina tambayoyi.

Rintse idona nayi tare da bud’e su na saukesu akansa,jikinane ya fara rawa kamar mazari don iya tsorata nayi ta ba kad’an ba.

Addu’oi na fara jerowa  a zuciya ta,sai naji wata nutsuwa ta ziyarceni,tsoron da ya mamaye zuciya ta ya gushe,cikin dakiya da kawar da duk wata hanyar da zata nuna tsoron sa nace;

“Me kazo yi a d’akina?”.

“Ziyara na kawo Masoyiyata abar qaunata”.

Ya fad’a idonsa a kaina,da sauri na juyo domin qara tabbatar da kodai gizo ne yake min, Mutumen da ko zo in kasheka da Hausa bai saniba?,saidai banga koda alamar mutum akan gadon nawa ba,sake jiyowa nayi akan madubin still yana zaune inda yake.

“Kidena jin tsorona, bazan tab’a cutar dake ba saboda ke abar sona ce”.

A mugun fusace kamar me shirin dambacewa na mik’e tsaye ina juyowa saitin gadon nace;

“Wallahi qarya kake, da kana sona da baka rik’a takurawa rayuwata ba,mugu azzalumi,Yau Asirinka ya tonu kana cikin qungiyar matsafa to wallahi Daniel nafi k’arfin ka, Arnen banza k’azami d’an iska,Sai na toni asirinka mushiriki kawai maras tsoron Allah”.

Sautin dariyarsa kawai nakeji amma bana ganin sa,Tinanin na farayi meyasa wannan mutumen zai takurawa rayuwa ta ne,’yar baiwar Allah dani mai na tare masa a duniyar nan,Tabbas dole na k’ara damara wurin ganin na kwato ‘yancin kaina, in kuma d’au fansar zaluncin da yayimin, saina zame masa masifa a rayuwarsa.

“Na barki lafiya masoyiyata”.

Najiyo Muryarsa yana fad’a,Mirror nayi saurin kallo sai naga wayam, wata nannauyar ajiyar

zuciya na sauke ina dafe kaina a hankali na furta,

“Ya Allah gani gareka, kayimin katangar k’arfe da wannan azzalumin”.

Jiki a sanyaye na shiga sanya kaya a jikina, agogo na kalla naga lokaci ya tafi kuma nasan Anty Sadiya nachan na jirana,duk abinda nake buqata na d’auka don bana marmarin dawowa d’akin,sannan na fice zuwa pallor.

Anty Sadiya kawai na hango a dainy Bak’ir na kan cinyarta, alamar Yaya har ya fita aiki da sauri ta d’ago tana kallona tace;

“Me ya tsayar dake Meenal,sai jiran ki nake tin d’azun”.

Murmushi nayi mata nace;

“Bakomai Anty”.

Na k’arashe maganar ina zama gefenta, a gurguje muka gama yin break d’in duk da nidai ba dad’in abincin nakeji ba,saida muka biya Inda Anty kekai Bak’ir sannan muka wuce wurin aiki lokacin har 8:00 ta buge.

Koda muka isa kowa office d’insa ya nufa, banbi ta kansa ba duk da banada tabbacin yazo ko bai zoba,na cigaba da ayukkan da ban k’arasa ba.

Sai 9:30 Sir Daniel ya shigo ma’aikatar,fuskarsa a sake bayada burin da ya wuce ya d’ora idonsa a kan k’yakkyawar fuskarta ta.

Koda ya shiga Office d’insa baiga alamar shigowar ta office d’in ba, kan kujerar sa ya zauna yana k’allon  saitin qofa ko zata shigo amma shiru,tinanin meya faru a jiya bayan yabar ma’aikatar ya fara,waya sallami ma’aikata?,Itace ko kuwa Pa sa?.

*#Comments*
*#Share*
*#Vote and like*

~Mrsbalarabe✍️~

*ƘAUNAR ƁOYE!!!*
_(THE SECRET LOVE!🖤)_

*Fatima Batula✍🏼*

_Wattpad:mrsbalarabe._

*Telegram*👇
https://t.me/joinchat/GxqDXvsOyg0Xr4s8

*Dedicated to my Anup(my happines) Allah ne kawai yasan irin son da nake yi miki, ke abun so ce dole duk wanda ya raɓeki ya soki, baki na bashi da kalaman godiya da nuna irin matsayinki a gurina sai dai kawai na ce ke ta musamman ce a cikin rayuwa ta, Allah yabaki Ify ya baki miji na gari. Amin thumma Amin.*

_Page_

_23-24_

✍ *✍ ǴỎĹĎĚŃ ṔĚŃ ŴŔÍŤĚŔŚ ÁŚŚÓĆÍÁŤÍÓŃ* ✍✍

*wє αrє вєαrєr's σf sσ gσldєn pєn*
*wє wrítє αssídíσuslч pєrcєívє nσ pαín,*
*sσ mαgícαl σur crєαtívє gσldєn pєn* ✍ *,вєhσld σur wσrds.α prσduct σf σur pєn* *,sαvσur σur wσrds, fσr ít wíll* *cαusє чσu nσ pαín.*

*INA MASOYAN LITATTAFAN ƘUNGIYAR GOLDEN PEN?*

*NESA TA ZO KUSA, TUNANIN RASHIN SAMUN NEXT PAGE YA ƘARE!.*

Kasance mutum na farko da zai fara karanta sabbin littattafan marubutan mu, a duk lokacin da muka yi typing. Kina/Kana iya samu, ta wannan damar ce kawai idan ka bi wannan links tare danna *LIKE* a shafin mu na Facebook zaka/zaki iya samun cigaba ko kuma ki samu duk littafin da kike buƙata namu daga farko.

https://www.facebook.com/Golden-Pen-Writers-Association-102095951667849/

Sai kun zo, kar ku manta a koda yaushe comments da sharhin ku yana ƙara mana ƙarfin gwiwa a wajen rubutu mai yawa.

```WANNAN PAGE KYAUTACE TA MUSAMMAN GA DUKKANIN MASOYA LITTAFIN K'AUNAR B'OYE,INA GODIYA SOSAI A GAREKU DA SOYAYYAR DA KUKE NUNAMA WANNAN LITTAFI NAWA,ALLAH YABAR K'AUNAR😍🙌🙏ALKHAIRIN ALLAH YA ISKEKU A DUK INDA KUKE MASOYAN AMANA🥰😘MRSBALARABE NA GODIYA DA JINJINA A GAREKU```

Yana cikin wannan tinanin ne yaji ana neman izinin shigowa office d'in nasa,baisan lokacin da ya saki wani k'ayataccen murmushi ba don yasan itace ba wani ba,mayun idanunsa ya zubama k'ofar na 'yan wasu seconds sannan yace;

"Come In".

Yana gama fad'in haka yayi juyi akan kujerar sa fuskarsa d'auke da murmushi.

Pa ce ta shigo cikin wata irin arniyar  shiga,matsatsun riga da wandone sanye a jikinta,fuskar nan tata anci uban makeup ga wani katafaren glass da tasa,kanta yasha kitson attach har gadon bayanta,burinta kawai Sir Daniel ya juyo ya kalleta don tasan dolene sai ya k'yasa.

Fuskarta d'auke da wani shu'umin murmushi  tace;

"Good Morning Sir".

Muryar Pa ta d'aki dodon kunnensa,wani irin bacin rai ya ziyarce shi nan take,a mugun hasale ya jiyo yana kallon ta baima tsaya tantance shigar dake jikinta ba yace;
```

“Hey who permits you to come in?”.

Jikinta na rawa ganin yanda yake kallonta ranshi b’ace tace;

“Am..ehm Sir You ar...”.

“Get out of my office!!!”.

Ya daka mata wata razanannar tsawa,wadda tasa hanjin cikinta hautsinewa,da sauri ta bud’e k’ofar ta fice daga Office d’in ta nufi nata office d’in.

Nidai naga Pa ta fito daga office d’insa da sauri saidai ban tsaya lura da yanayin ta ba don kuwa bata isheni kallo ba,nayi shigewata office d’ina don a lokacin na dawo daga office d’in Anty Sadiya ne.

Pa na shiga office d’inta ta rik’e qugunta tana fad’in,

“Jesus christ!!!,What’s wrong with him?,did i do something wrong to him?,No i didn’t,Sir Daniel he’s never do this to me”.

Zama tayi kan kujera tana fad’in,

“I will find out what caused this to me”.

Sir Daniel kuwa yana ganin Pa ta fita ya mik’e ransa a mugun b’ace,yafara zagaye tsakiyar Office d’insa,

“What she’s mean?,Tana nufin bazata shigo office d’insa ba ya ganta ko zai samu sassauci a cikin zuciyarsa”.

Turo K’ofar da akayine ya sanyashi d’ago kansa da sauri yana kallon wane isasshene ze shigo masa Office babu izininsa,Karaf idanunsu ya sark’e a cikin na juna,lumshe idanunsa yayi ya sake b’ud’esu a kanta yana cigaba da kallonta.

Nikuwa murmushi na sakarmasa a raina nace;

“Munafuki,zakaci ubankane”.

A zahiri kuwa cewa nayi,

“Good Morning Sir”.

Har lokacin ina tsaye a bakin k’ofar Office d’in kuma ban rufo k’ofar ba don nasan ba qaramin aikinsa bane yace na fita.

“Come in”.

Ya fad’a tare da komawa kujerar sa ya zauna yana cigaba da kallon Meenal dake k’ok’arin rufe k’ofar.

Bayan na rufe k’ofar na juyo cikin wani irin taku mai jan hankali nake tafowa wurinshi,file d’in dake hannuna na ajiye mishi a kan table d’insa, cikin wata fitinanniyar murya nace;

“Ina buqatar sa hannunka Sir”.

“Okey, have a seat”.

Ya fad’a yana nunamin kujerar dake ajiye tana kallon table d’in nashi tare da janyo files d’in zuwa gaban shi ya bud’e.

Ba musu na ja kujerar na zauna,duk da kuwa nayi mamakin hakan,naci gaba da kallon shi,wani tinani nayi a raina tare da sakin wani murmushi ina kara wayata a kunne nace;

“Hey darling I miss you”.

Da mugun sauri naga Sir Daniel ya d’ago yana kallo na,nikuwa na maze  na cigaba da fad’in,

“I love you too,i can’t imagine life without you..”.

“What the hell you are doing here?”.

Sir Daniel ya fad’a a mugun fusace yana buga table d’in dake gabansa.

Da sauri na cire wayar daga kunnena ina kallon sa,ina k’ok’arin gimtse dariyar dake son kub’uce min nace;

“I’m sorry sir”.

“Shut up!,and leave my office”.

“But Sir wh..”.

“Out!!”.

Ya katse ni da wata irin tsawa.

Miqewa nayi na nufi k’ofa har na d’ora hannu kan handle d’in k’ofar naji yace;

“Come back”.

D’an murmushi nayi sannan na juyo nadawo gabansa nayi tsaye, kallo d’aya yayimin ya d’auke kansa yana fad’in,

“Seat”.

Ba tare da na kalleshi ba na zauna,ina mamakin murd’ad’en halin wannan mutumen.

Tsawon 5 minutes ya d’auka yana singing d’in sannan ya turo min su gabana ba tare da ya kalle ni ba.

Nikuwa da sauri na d’au files d’in ina k’ok’arin miqewa yace;

“Excuse me”.

Kallon sa nayi, ba tare da nace komai ba.

“Wannan ya zamo miki na k’arshe da zakiyi waya a cikin office d’ina, Infact bana ma son na k’ara ganin kin shigo office d’in nan da waya okey?”.

Da sauri nace;

“Okay Sir”.

“You can go”.

Ya fad’a yana juyarda kujerar sa ya bani baya murmushi d’auke a fuskar sa,nikuwa miqewa nayi na sakar mishi gwalo aikuwa lokacin ya juyo ya kamani ina masa gwalo,zaro ido yayi cike da mamaki yayinda nayi saurin ficewa daga office d’in ina k’yalk’yala dariya na shige office d’ina.

Shima Sir Daniel dariya yayi sosai wacce bai sa ran ya tab’a yin irinta a rayuwar sa.

“She’s so funny”.

Ya fad’a yana jin wani farin ciki na ratsa shi,saitin zuciyar sa ya dafe yana fad’in,

“I’m in love with this idiot”.

Wasu yawu masu k’arfi Pa ta had’iye tana bin bayan Meenal da kallo,

“Is he the one that makes this idiot laugh,no no this will never happen,i know how Sir Daniel hate muslim,so what make her laugh?,i wan’t know”.

Tana gama fad’in haka ta nufi Office d’in Meenal.

*Idan naji ruwan comments zanyi wani page anjima*😎

*#Comments*
*#Share*
*#Vote and like*

~Mrsbalarabe✍️~

*ƘAUNAR ƁOYE!!!*
_(THE SECRET LOVE!🖤)_

*Fatima Batula✍🏼*

_Wattpad:mrsbalarabe._

*Telegram*👇
https://t.me/joinchat/GxqDXvsOyg0Xr4s8

*Dedicated to my Anup(my happines) Allah ne kawai yasan irin son da nake yi miki, ke abun so ce dole duk wanda ya raɓeki ya soki, baki na bashi da kalaman godiya da nuna irin matsayinki a gurina sai dai kawai na ce ke ta musamman ce a cikin rayuwa ta, Allah yabaki Ify ya baki miji na gari. Amin thumma Amin.*

_Page_

_25-26_

https://www.youtube.com/channel/UCcAjVQ74qod9_dL0e_AqkiQ

*DUNIYAR LITTAFAN HAUSA TV*

✍ *✍ G̾O̾L̾D̾E̾N̾ P̾E̾N̾ W̾R̾I̾T̾E̾R̾S̾ A̾S̾S̾O̾C̾I̾A̾T̾I̾O̾N̾* ✍✍

*wє αrє вєαrєr's σf sσ  gσldєn pєn*
*wє wrítє αssídíσuslч pєrcєívє nσ pαín,*
*sσ mαgícαl σur crєαtívє gσldєn pєn* ✍ *,вєhσld σur wσrds.α prσduct σf σur pєn* *,sαvσur σur wσrds, fσr ít wíll* *cαusє чσu nσ pαín.*

*INA MASOYAN LITATTAFAN KUNGIYAR GOLDEN PEN?*

*NESA TA ZO KUSA, TUNANIN RASHIN SAMUN NEXT PAGE YA ƘARE!.*

Kasance mutum na farko da zai fara karanta sabbin littattafan marubutan mu, a duk lokacin da muka yi typing. Kina/Kana iya samu, ta wannan damar ce kawai idan ka bi wannan links tare danna *LIKE* a shafin mu na Facebook zaka/zaki iya samun cigaba ko kuma ki samu duk littafin da kike buƙata namu daga farko.

https://www.facebook.com/Golden-Pen-Writers-Association-102095951667849/

Sai kun zo, kar ku manta a koda yaushe comments da sharhin ku yana ƙara mana ƙarfin gwiwa a wajen rubutu mai yawa.

Na duk'ufa sosai ina aiki a laptop ina shigar da wasu bayanai,naji an turo k'ofar office d'in an shigo ba tare da sallama ba,dayake na ba k'ofar baya shiyasa banga wanda ya shigo d'inba,sharewa nayi na cigaba da aikina don sonake in kammala shi a yau d'innan,duk da kuwa shigomin Office da akayi babu sallama ya batan rai.

"Hey Muslim girl, Excuse me".

Tiny ta fad'a tana tsaye daga bakin k'ofar.

Banjuyo ba saida na karasa shigar da wani guntun bayani sannan na juyo ina kallonta,tamke fuska nayi kamar an aikomin da sak'on mutuwa nace;

"What brought you here?,What do you want?".

Yarfe hannayenta tayi tana tab'e bakinta mai kama da na aladu tace;

"Nothing,I just wanted to ask you some questions".

"Which questions?,do you have any business with me?".

Na fad'a ina b'alla mata harara.

"Menene ya sanya ki dariya lokacin da kika fito office d'in Sir Daniel?".

Tiny ta fad'a tana cire glass d'in dake fuskarta,mamaki taban sosai don har nayi niyya zan mayar mata da maganar da zata iya sanyata kuka sai kuma na saki wani murmushi don dama ina lure da take-takenta tin ranar da tasan nice Secretary d'in Sir Daniel take min wani matsiyacin kallo, hakan ya tabbatar min da sonshi take ba ko shakka.

Juyi nayi akan kujerata kamar yanda naga Sir Daniel yayi nace;

"Do you want to know what make me laugh that time?".

Na k'arashe maganar ina juyowa saitin da take na zuba mata idanuna,cikin sauri ta gyad'a kai tace;

"Yes".

Gira na d'age mata,tare da nuna mata kujera ina fad'in,

"Okey well,have a seat".

Ba musu ta zauna cike da zumud'in son jin abinda ya sanyani dariya.

Miqewa nayi daga kan kujerar na nufo inda take zaune,fuskata d'auke da shu'umin murmushi nace;

"Can you believe that?".

"What?".

Ta fad'a tana min wani kallo marar ma'ana.

"Can you believe Sir Daniel falls in love with me?,So that's what makes me laugh".

Wata mahaukaciyar dariya Tiny ta saki tana nunani da yatsa tace;

"You are lier,Do you know how Sir Daniel hates your ditty religion?,he's..".

"Shut up!!!,and Watch your words".

Na daka mata wata tsawa mai firgitarwa wadda tasa Tiny yin shiru ba shiri.

"This should be the last time da zaki fad'i wata banzar kalma gameda da addinina,I don't care If you believe or not,you can leave my Office".

Na fad'a ina komawa kan kujerata na zauna,raina fess don nasan yau bacci ma sai ya gagareta.

Miqewa Tiny tayi da sauri ta fice daga office d'in,nikuwa na saki wats shak'iyiyar dariya,bag d'ita na bud'e na feffesa turare a office d'in don wani irin warinta naji ya mamaye office d'in,Kai Allah ya shiryeni ni Meenal, duk banji warin ba saida ta fice daga office d'in lol.

cigaba nayi da aikin da nake a laptop d'in,ban tashi ba sai k'arfe d'aya naje nayo alwala na gabatar da sallar azahar.

Wani k’ugi naji cikina yayi alamar ina jin yinwa,da sauri na fice daga office d’in na nufi hanyar da zata kaini Office d’in Anty Sadiya.

Dakatar da aikin da take yi tayi ta d’ago ta kalleni Fuskarta d’auke da murmushi tace;

“Harkin kammala aikin naki kenan?”.

“Wallahi Anty yunwa nakeji,zan d’an fita nasai ko Fresh yo nasamu nasha”.

“Okay,amma kije ki d’au Excuse wurin Boss don bakida ikon fita saida izininsa”.

Da sauri na zaro ido nace;

“Kai!,Yunwa fa nace miki ina ji,ai ba wani gu zanje ba nasan ko shi dole idan yaji yinwa ya fito neman abinda zaisama cikinsa”.

Girgiza kai tayi tana fad’in,

“Nasan da haka Meenal,bana son ku k’ara samun wata matsala ke da Sir Daniel,please kiyi yanda nace kinji my sis”.

Harga Allah raina baiso ba,amma ganin yanda Anty Sadiya ta dage yasa ni fad’in,

“Shikenan,bara naje”.

“Okey,ki dawo lafiya”.

Harna kai bakin k’ofa na juyo nace;

“To ke Anty me kike so na siyo miki?”.

“Bana jin yunwa Meenal,kema nasan don kawai bakiyi wani karin kirki bane yasaki jin yinwa da wuri haka”.

Ban tsaya jin k’arshen zancen ta ba na fice daga Office d’in kamar in fasa ihu nakeji,wai d’an fitar ma da zakayi saika nemi izinin wani shirgegen Arne,mushiriki,ina gunguni a raina har na iso k’ofar Office d’in nasa,tsaye nayi abunda ya faru a tsakanin mu d’azun ya dawo min a kai.

“yanzu fa idan na shiga zai iya zabga min mari”.

Na fad’a a raina.

“Hmm wallahi bazata sab’u ba,ina wannan daa ne yanzu kam saidai mu kwashi ‘yan kallo bazan yarda lafcecen arne yana zabgamin mari a banza da wofi ba”.

Na k’arashe maganar ina d’aure gele na a qugu na don yau na d’au alwashin duk ya bugeni wallahi saina rama,da wannan tinanin na fara nock d’in k’ofar Office d’in.

Shiru banji alamar yama san ina wurin ba,a hankali na murd’a k’ofar na tura kaina kad’an don ganin ko baya cikin Office d’in ne,fincikoni akayi da k’arfin tsiya wanda zan iya rantsewa da Allah banji hannun mutum a jikina ba saidai na ganni  zaune a tsakar Office d’in, kalle-kalle na fara banga kowa ba,take naji hanjin cikina sun hargitse,ba b’ata lokaci na fara jero addu’oin tsari a raina.

K’amshin turaren d’azun da safene naji gaf da hancina,da sauri na k’ara kallon ko ina na d’akin babu kowa a ciki bakajin komai sai k’arar Ac.

“Meenal dagaske zaki iya dambe da masoyin ki?”.

Na jiyo sautin muryar da dukkanin wani sashe na jikina ya gama haddaceta.

Miqewa nayi da sauri,ina fad’in,

“Meye zaka wani b’oye kanka,ka fito idan ba tsoroba,na rantse da girman Allah duk ka tab’ani sai na baka mamaki”.

Sir Daniel  da ya fito daga Toilet tsaye yayi yana kallonta,dawa take magana?,ya tambayi kansa yana cigaba da kallon yanda tayi d’amara,dayake ta bashi bayane shiyasa bata ganshi ba,takowa yayi zuwa gareta a hankali ya d’ora hannunsa a kafad’arta yace;

“Hey..”.

Juyowa tayi ta daka wani uban tsalle  tare da zabga mishi wani lafiyayyen mari a kunci, tana fad’in,

“Me na fad’a maka?,wallahi yau koni ko kai a Office d’innan”.

Ta k’arashe maganar tana ja da baya,hannuwanta dunk’ule tana shirin kai masa bugu.

Mamaki da al’ajabi suka taru suka cika Sir Daniel ya dafe kuncin da ta maresa yana kallon ta,anya wannan yarinyar tanada hankali?ni zata mara?,tambayoyin da yake ma kansa kenan.

“Zakiyi nadamar wannan marin Meenal”.

Naji saukar muryarsa a gefena,kallon Sir Daniel nayi naga yana nan tsaye a inda yake har lokacin hannunsa dafe da kuncinsa,sannan na juyo na kalli gefen da naji saukar maganar shi, Tsaye na ganshi cikin shiga irinta jikin Sir Daniel ranshi a matuk'ar b'ace wanda ganinsa cikin wannan yanayin ba k'aramin razanani yayi
ba,sake kallon Sir Daniel nayi still yana nan yanda yake,iya rud'ewa nayita wacce bansan yanda zan misiltata ba.

"Meke shirin faruwa dani ni Meenal?".

Wani irin jiri naji ya d'ebeni Shuuu na zube a k'asa sumamma ban k'ara sanin inda nake ba kuma.

Da mugun sauri Sir Daniel ya
nufota, hankalinsa tashe yana mamakin abinda ke damun wannan yarinyar,bai tsaya b'ata lokaci ba ya sunkuceta  yayi waje da sauri,ta Elavetor d'insa ya shiga ta saukesu a chan k'asan ma'aikatar, ganin yanda Ya fito d'auke da Meenal ya sanya ma'aikatan nufosa suna tambayar lafiya? babu wanda ya kula a cikinsu ya sanyata a motar shi ya shiga yaja motar ya fice daga ma'aikatar a tamanin,Bayansa Security's d'insa suka bi,yayinda duk jama'ar ma'aikatar sukayi cirko-cirko suna mamakin abinda ke faruwa?,inda akaita cecekuce har labari ya kaima Anty Sadiya.

A rud'e ta shige motar ta tabi bayan su Sir Daniel duk da ko alamar motarsa bata gani ba,haka ta yanki tikiti tabi hanyar da zuciyarta ke bata a chan ya nufa.

*#Comments*
*#Share*
*#Vote and like*

~Mrsbalarabe✍️~

*ƘAUNAR ƁOYE!!!*
_(THE SECRET LOVE!🖤)_

*Fatima Batula✍🏼*

_Wattpad:mrsbalarabe._

*Telegram*👇
https://t.me/joinchat/GxqDXvsOyg0Xr4s8

* Dedicated to my Anup(my happines) Allah ne kawai yasan irin son da nake yi miki, ke abun so ce dole duk wanda ya raɓeki ya soki, baki na bashi da kalaman godiya da nuna irin matsayinki a gurina sai dai kawai na ce ke ta musamman ce a cikin rayuwa ta, Allah yabaki Ify ya baki miji na gari. Amin thumma Amin.*

_Page_

_27-28_

*HAPPY BELATED BIRTHDAY MUHAMMAD KHAREEM🎂🥂🍾🍾WISHING YOU LONG LIFE AND PROSPERITY,MORE MONEY IN YOUR ACCOUNT AND MATA TA GARI I PRAY🤗🙏💃*

✍ *✍ Ǵ́ÓĹD́ÉŃ ṔÉŃ ẂŔÍT́ÉŔŚ ÁŚŚÓĆÍÁT́ÍÓŃ* ✍✍

*wє αrє вєαrєr's σf sσ gσldєn pєn*
*wє wrítє αssídíσuslч pєrcєívє nσ paín,*
*sσ mαgícαl σur crєαtívє gσldєn pєn* ✍ *,вєhσld σur wσrds.α prσduct σf σur pєn* *,sαvσur σur wσrds, fσr ít wíll* *cαusє чσu nσ pαín.*

*INA MASOYAN LITATTAFAN KUNGIYAR GOLDEN PEN?*

*NESA TA ZO KUSA, TUNANIN RASHIN SAMUN NEXT PAGE YA ƘARE!.*

Kasance mutum na farko da zai fara karanta sabbin littattafan marubutan mu, a duk lokacin da muka yi typing. Kina/Kana iya samu, ta wannan damar ce kawai idan ka bi wannan links tare danna *LIKE* a shafin mu na Facebook zaka/zaki iya samun cigaba ko kuma ki samu duk littafin da kike buƙata namu daga farko.

https://www.facebook.com/Golden-Pen-Writers-Association-102095951667849/

Sai kun zo, kar ku manta a koda yaushe comments da sharhin ku yana ƙara mana ƙarfin gwiwa a wajen rubutu mai yawa.

Wata tsadaddar Hospital Sir Daniel ya kai Meenal,yayin da Likitocin asibitin suka shiga tambayar abinda ya sameta amma ina bai rabasu da kalma d’aya ba,da yaga ma zasu raina mishi wayo su kuma b’ata mashi lokaci ya shaqo wuyan wani babban likita ya hau kifa masa mari cike da b’acin rai,dak’yar aka kwaceshi suka hau ba Sir Daniel hak’uri,inda nan take aka shiga bata taimakon gaugawa.

Tare dashi aka shiga d’akin da aka kaita,sam ya kasa zama sai kai kawo yake yana tinanin meke damun wannan yarinyar haka?,ga baki d’aya ya rasa duk wani sukuni nashi,wayarsa ce ta fara qara dak’yar ya iya cirota cikin aljihu,sunan Mom ya gani,ficewa yayi waje sannan ya d’aga wayar yana k’ok’arin saita muryarshi don baya son ta fahimci yanayin da yake ciki.

“Hey Mom”.

Ya fad’a cikin muryar nan tashi mai kama da an mishi dole.

“Where are you”.

D’an sosa kai yayi yace;

“Ina Office Mom,meya faru?”.

“Jikina be bani kana Office ba Son,Please kana ina?”.

“Mom meyasa zan miki qarya?,Ina Office”.

Ajiyar Numfashi ta sauke tana fad’in,

“Shikenan,zanzo ma’aikatar don in tabbatar”.

Daga haka ta katse wayar,Sam shi bema da damu da zuwan da tace zatayi ba,ya komawarsa d’akin da Meenal take kwance,har lokacin bata farfad’o ba.

Dak’yar Anty Sadiya ta gano Asibitin da ya kai Meenal d’in,koda ta iso bakin get d’in cike yake da matsara wanda hakan ze tabbatar maka da akwai wani hamshaqi a cikin Asibitin,fitowa tayi daga motar ta don batama ga fuskar tunkaraso da mota ba,neman izinin shiga asibitin tayi amma fafur suka k’i barinta,daga k’arshe suka ce saita nuna musu ID card d’inta sannan zasu bari ta shiga,da sauri ta koma mota ta d’auko ta nuna musu sai a lokacin suka bata izinin shiga,sauri-sauri gudu-gudu take had’awa sai kuka take zuciyarta na zafi, bata sha wahala ba ta gano d’akin da Meenal d’in take,daidai lokacin Sir Daniel ya fito shida wani Doctor suna tafe yana ma Sir Daniel bayani akan sufa basuga wani abun dake damunta ba,hasalima lafiyarta lau batada wani rashin lafiya.

D’agowar da zaiyi suka had’a ido da Anty Sadiya da keyi mashi wani mugun kallo,duk danniyar da take ma zuciyarta amma ina hakan yacitura saida ta tako gaban sa tana fad’in,

“Yanzu ma ka k’ara marin nata ko?,To wallahi bari kaji duk hakan yayi sanadin samun matsalar sister ta sai nayi k’arar ka, kai wane irin mugune?,Azzalumi wanda baisan darajar d’an Adam ba”.

Wani daga cikin Security’s d’inshi ne ya katsa mata tsawa,yana k’ok’arin jan hannunta ta d’auke shi da wani lafiyayyen mari tace;

“Karka k’ara kuskuren tab’ani,ni musulma ce kuma matar Aure”.

Security d’aga hannu yayi da nufin zabga mata marora Sir Daniel yayi saurin riqe hannunsa yace;

“Kar kayi wannan kuskuren,ku b’ace min da gani”.

Jikinsu na rawa suka bar wurin,dubonsa ya maido kan Anty Sadiya kamar bazaiyi magana ba sai kuma chan yace;

“Idan zaki iya ki biyoni zuwa office d’in likita”.

Da sauri tace;

“Bana buqatar jin komai daga garesa,Ina son ganin Sister na”.

Ta k’arashe maganar tana tinanin wane irin hali Meenal ke ciki,bata da burin da yawuce taga wane hali Meenal ke ciki.

Sai a lokacin Doctor d’in yayi magana.

“Sorry Madam,amma zuwanki yanada matuk’ar amfani,ki daure muje don kiji abinda zan fad’a”.

Da yake Anty Sadiya akwai saukin kai bata k’ara cewa komai ba tabi su zuwa Office d’in.

Zama sukayi akan kujerun office d’in suna kallon likitan da ya fara rubutu a takarda.

Lumshe ido Sir Daniel yayi ya sake bud’e su yace;

“Wannan itace Sister d’inta,zata tsaya anan har lokacin da zata dawo normal”.

“Wai meya faru da ita ne?”.

Anty Sadiya ta fad’a tana tsare shi da idanunta da sukayi jawur.

Gyaran Murya Doctor d’in yayi yace;

“Babu abinda ya faru da ita Madam illa shock da ta samu akan wani abun da tagani,Sakamakon binciken da mukai mata ya bada hakan,so amma yanzu dai mun yi iyakar yin mu mun gano lafiyarta qalau babu abinda ke damunta,ko wane lokaci muna sa ran zata iya farfad’owa”.

Sai a lokacin hankalin Anty Sadiya ya d’an kwanta,ta sauke ajiyar zuciya tace;

“Nagode Doctor,amma zan iya ganin ta yanzu?,hankali na bazai tab’a kwanciya ba idan banga Meenal ba”.

“Eh zaki iya ganinta”.

Ya k’arashe maganar yana mik’o mata wani green card yace;

“Ki nuna wannan za’a baki damar shiga d’akin”.

Da Sauri Anty ta karba ta mik’e tare da fad’in,

“Thanks You”.

Sannan ta fice daga d’akin,inda tabar Sir Daniel zaune suna cigaba da magana da Doctor d’in.

Koda ta shigo d’akin kwance ta hango Meenal idanunta a lumshe,da sauri ta k’araso wurin ta tana kallon ta cike da tausayawa,fuskarta ta shafa take k’wallah suka sake cika idonta.

“Meenal menene ya sameki?,Don Allah ki bud’e idanunki Meenal,Duk wani farin cikina yana tattare dake”.

Shigowar wata nurse ya sanyata yin shiru.

“Kiyi hak’uri kidena wannan kukan da kike,zata iya farfad’owa ko wane lokaci”.

Tana gama fad’in haka ta fara qoqarin cire drip d’in da aka sanya ma Meenal.

Sir Daniel kuwa Kiran Mom d’insa ya addabesa don harta isa ma’aikatar ta tarar baya nan,yana d’agawa ta balbale shi da masifa,tare da bashi umurnin duk inda yake ya baro yazo ma’aikata tana son ganin shi, ba shiri ya fice daga Asibitin bayan ya gama tsara komai akan Meenal,don duk wani abu da zata buqata saida ya bada kud’i a k’asa.

Yana shigowa Company bai zarce ko ina ba sai Office d’insa don yasan Mom tana chan,saida ya tsaya ya daidaita nutsuwarshi sannan ya tura k’ofar office d’in ya shiga,zaune ya sameta tana waya tana ganin shi ta sakar mishi wata muguwar harara,shikuwa murmushi ya sakar mata tare da qarasowa wurinta yayi mata side hug yana kai mata peck a goshi.

“Yaushe ka fara min qarya Son?”.

Ta jefo masa tambaya don sosai tayi mamakin yanda yayi mata qaryar yana office, don qarya ba halin shi ba ce tin yana yaro.

Sosa kai yayi yace;

“Sorry Mom yau nayi babban laifi ki yafemin,naje wurin wani Meeting ne na sirri,ba kowa ma yasan bana Office ba”.

Sai a lokacin ta yarda dashi tace;

“Okay,Menene Abinda Meeting d’in ya qunsa”.

Shiru yayi yana tinanin qaryar da zai k’ara zabgo mata don shi sam bai iya qaryaba,har mamakin kanshi yayi da yayi mata wannan qaryar ta yarda.

“Wai suna son na sanya musu hannun ne akan wata Giya da za’a fara mai cike da sinadarai masu kyau”.

Murmushi tayi tace;

“Dakyau yarona,ni nasan cewa kai d’in a koda yaushe kaine a gaba saidai a bika a baya,Ina alfahri da kai sosai”.

Shima murmushin yai mata yana fad’in,

“Nima haka Sweetheart”.

Mik’ewa tayi tace;

“Zan wuce Church yanzu,kasan munada biki yau,k’arfe takwas tayi maka a chan kai da Taye”.

“Okay Mom”.

Ya fad’a ranshi a d’an jagule,daga haka Mom ta fice daga office d’in.

Meenal ta fad’o masa a rai,karo na farko da yaji wani irin matsanancin tausayin ta ya mamaye zuciyar shi,Wacece ita?,meke damun ta?.

Tambayoyin da ya shiga jero ma kansa kenan,d’an guntun tsaki yaja saboda rashin sanin amsar wadannan tambayoyin.

Ganin lokacin sallar la’asar har ya wuce ya sanya Anty Sadiya mik’ewa cikin sanyin jiki ta shige Toilet d’in d’akin tayo alwala, ta cire d’an kwalin kanta ta shimfid’a ta gyara mayafinta ta gabatar da Sallah, ta dad’e sosai tana yima Meenal addu’a hawaye sai ambaliya suke a idonta.

Haka taci gaba da zaman jugum tana kallon Meenal,sai a lokacin ta tino da Abban Bak’ir da shi kanshi Bak’ir d’in,Number shi ta lalubo ta danna mishi kira,yana d’agawa ta fashe mishi da kuka,cikin tashin hankali yake tambayar meya faru,da k’yar ta daina kukan ta shiga fad’a mishi abinda ke faruwa nan yace mata gashi nan zuwa,tace ya d’auko Bak’ir,daga haka suka katse wayar kowa da abinda yake sak’awa a ransa.

Ko Minti Ashirin basuyi da waya ba sai gashi ya iso,da kanta ta fito zuwa tarbon shi,Karb’ar

Yaronta tayi inda shikuma ya riqo ledoji a hannunsa suna tafe yana tambayar jikin Meenal d’in da haka har suka iso d’akin.

Sosai Meenal ta bashi tausai,don numfashin da takeyi kawai ze tabbatar maka da tana raye,zama yayi kan kujera yana kallon Anty Sadiya yace;

“To su Doctors d’in me suka ce ne?”.

Tana cire ma Bak’ir rigar sanyin da ke jikinsa tace;

“Wai lafiyar ta qalau,kawai shock ne maybe taga wani abun da ya firgitata ne da yawa,wa yasani ko wannan Aljanin ne dake bibiyarta ta gani”.

Girgiza kai Yaya Yayi yace;

“Na rasa gane kan lamarin Meenal,kawai addu’a zamu cigaba da yimata insha Allah za’a dace”.

“Allah yasa”.

“Ameen”.

Daga Haka suka cigaba da tattaunawa akan lamarin Meenal,daga k’arshe dai gida Yaya ya koma ya d’ebo musu kayan su da duk wani abun da zasu yi amfani dashi.

K’arfe takwas nayi Mom ta danno mashi kira akan ya tabbatar ya iso yanzu,laqe murya yayi yace;

“Mom Banda lafiya fa,kunnen nan nawa ya matsa min”.

“Oh my god!,Ka kira Doctor d’inka?”.

Ta fad’a cike da damuwa,don tasan yanda ciwon kunnen nan nashi ke basa wahala,ko kad’an baya raga mishi.

“Eh na kirashi Mom yace zaizo yanzu”.

“Good Boy,Kace mishi ya duba min kai dakyau kaji ko”.

Cikin ‘yar shagwaba yace;

“Okay Mom,Bye”.

“Bye Son”.

Daga haka ya katse wayar yana lumshe idonsa,miqewa yayi ya shiga Bathroom yayo wanka,yana fitowa ya sanya wasu qananan kaya tare da feshe jikinshi da turaren sa mai k’amshi,Keys d’in motarshi ya d’auka ya nufin harabar get,horn yayi ma masu gadi da sauri suka bud’e mishi get ya fice daga gidan,ya kama hanyar Hospital d’in da Meenal take.

Sosai yaya da Anty Sadiya sukayi mamakin ganin shi,tambayar me jiki yayi suka bashi amsa,nan yace zai wuce sosai suka hau yimasa godiya da zai fita ya ajiye musu wasu mak’uddan kud’i yayi ficewarsa,Kallon juna Anty Sadiya da Yaya sukayi saidai basu ce komai ba.

Wasa-Wasa har saida Meenal tayi 2days a Asibitin,har lokacin bata farfad’o ba amma lafiya lau take fitar da numfashi kamar me bacci,Anty Sadiya tashiga damuwa sosai ganin halin da Meenal ke ciki don sosai ta tsorata da lamarin,Doctors d’in da Yaya ke lallashinta tare da qarfafa mata gwuiwa,Sir Daniel kuwa be qara zuwa ba amma labarin ta yana a kunnensa shima duk ya shiga damuwa da wannan lamari na Meenal.

Anty Sadiya na zaune ita da Anty Rabi’a da tazo ganin Meenal,sukaji kamar Meenal d’in ta sauke ajiyar zuciya da qarfi,da sauri suka juyo suna kallon ta don tabbatar wa,a karo na biyu ta sake sauke ajiyar zuciya sai kawai Jini ya fara biyowa ta baki da hancinta.

A mugun firgice suka nufi inda take kwance,jijjigata Anty Sadiya ta shiga yi tana kiran sunan ta cike da tashin hankali amma shiru,sakinta tayi ta fice daga d’akin da mugun gudu ta nufi wurin Doctor.

A tare suka shigo d’akin da Dr d’in tare da wasu nurses,suma cike da mamaki suke kallon jinin dake fitowa daga Bakinta da hancinta,nan take suka shiga yimata aune-aune don ganin abinda ya haddasa mata wannan bleeding d’in, babu abinda suka iya ganowa,dubararsu ta likitoci suka shiga yimata dak’yar suka samu jinin ya tsaya, suna k’ara aunata sukaga jininta yayi qasa sosai,tana buqatar jini cikin gaugawa.

Kuka kawai Anty Sadiya keyi,Anty Rabi’a na lallashinta.

Number Sir Daniel Doctor ya kira ya sanar dashi abinda ake ciki,babu b'ata lokaci sai gashi ya iso Asibitin,Ana auna jininsa aka ga yana yimata nan aka d'iba aka zo aka sanya mata,sai kuma numfashinta ya fara barazanar d'aukewa take aka sanya mata Oxygen,haka suka cigaba da zama Asibitin babu wani cigaba,don sau uku ana qara mata jinin Sir Daniel,abunda yayi matuqar d'aurewa su Anty Sadiya kai kenan.

*After One Week*

Duk kaga halin da Meenal ke ciki dole ka tausaya mata,don kuwa duk ta rame kamar wacce ta shekara tana ciwo,Anty Sadiya ma ta rame sosai don ko bacci bata samunyi.

Ta b'angaren Sir Daniel ma sai a hankulla,babu abinda yake tsinanawa a office, ga baki d'aya baya jin d'ad'in komai,sai a lokacin ya qara tabbatar da yana k'aunar Meenal bada wasa ba.

***************************************

"Ina sanki Meenal,kece farin cikina".

Sassanyar muryarshi ta daki dodon kunnena.

Fuskata d'auke da murmushi na juyo na kallesa,yana tsaye kusa da wata bishiyar fulawa mai kyawawan furanni masu launin kala,hannu ya miqo min yana fad'in,

"Kizo gareni Meenal,nazo miki da wani muhimmin labari".

"Dagaske?".

Na fad'a ina kallonsa.

Kai ya gyad'amin alamar eh,wurinsa na nufo ina cigaba da yimasa murmushi, inda ya riqo

hannuna muka zauna akan wata lallausar capet.

“Kinsan labarin da zan baki?”.

Girgiza kai nayi ina fad’in,

“A’ah sai ka fad’a”.

“Kalli nan”.

Ya fad’a yana nunamin tafin hannunsa,

Zaro ido nayi ganin Sir Daniel zaune a office yayi tagumi.

“Sir Daniel!,Meyasa kuke kama dashi?”.

B’ata fuska yayi yace;

“Banason tambaya,Inason ki saurari duk abinda zan fad’a miki a yanzu,idan har kikayi amfani da abinda zan fad’a miki to tabbas kin tsiratar da rayuwarki daga fad’awa halaka,idan kuwa kika qi to lallai kuwa kina cikin had’ari Meenal”.

Ban iya cewa komai ba na zuba mishi ido,ina son jin abinda zai fad’a.

*#Comments*
*#Share*
*#Vote and like*

~Mrsbalarabe✍️~

*ƘAUNAR ƁOYE!!!*
_(THE SECRET LOVE!🖤)_

*Fatima Batula✍🏼*

_Wattpad:mrsbalarabe._

*Telegram*👇
https://t.me/joinchat/GxqDXvsOyg0Xr4s8

*Dedicated to my Anup(my happines) Allah ne kawai yasan irin son da nake yi miki, ke abun so ce dole duk wanda ya raɓeki ya soki, baki na bashi da kalaman godiya da nuna irin matsayinki a gurina sai dai kawai na ce ke ta musamman ce a cikin rayuwa ta, Allah yabaki Ify ya baki miji na gari. Amin thumma Amin.*

_Page_

_29-30_

✍ *✍ Ǵ́Ó́Ĺ́D́ É́Ń́ ṔÉ́Ń́ Ẃ́Ŕ́Í́T́É́Ŕ́Ś́ Á́Ś́Ś́Ó́Ć́Í́Á́T́Í́Ó́Ń́* ✍✍

*wє αrє вєαrєr's σf sσ gσldєn pєn*
*wє wrítє αssídíσuslч pєrcєívє nσ pαín,*
*sσ mαgícαl σur crєαtívє gσldєn pєn* ✍ *,вєhσld σur wσrds.α prσduct σf σur pєn* *,sαvσur σur

wσrds, fσr ít wíll* *cαuѕє чσu nσ pαín.*

*INA MASOYAN LITATTAFAN KUNGIYAR GOLDEN PEN?*

*NESA TA ZO KUSA, TUNANIN RASHIN SAMUN NEXT PAGE YA ƘARE!.*

Kasance mutum na farko da zai fara karanta sabbin littattafan marubutan mu, a duk lokacin da muka yi typing. Kina/Kana iya samu, ta wannan damar ce kawai idan ka bi wannan links tare danna *LIKE* a shafin mu na Facebook zaka/zaki iya samun cigaba ko kuma ki samu duk littafin da kike buƙata namu daga farko.

https://www.facebook.com/Golden-Pen-Writers-Association-102095951667849/

Sai kun zo, kar ku manta a koda yaushe comments da sharhin ku yana ƙara mana ƙarfin gwiwa a wajen rubutu mai yawa.

“Meenal Ina son kisan cewa Daniel ya kasance Amini a gareni,Tin yana qaramin yaro nake jikinsa saidai babu wanda yasan da hakan saboda bana yin duk wani abun da zai nuna ina jikinsa,amma nakan fito masa muyi ta wasanni lokacin yana yaro,daga lokacin da ya cika shekara 10 na dena fito masa muna wasa saboda tilastani da iyayena sukayi akan dole sai na rabu dashi saboda ni musulmi ne shikuma arne,ya shiga damuwasa sosai lokacin da yadena ganina kamar yanda nima na shiga,amma a koda yaushe ina tare dashi domin kiyaye lafiyar shi,Ina k’aunarshi ne shiyasa na rab’esa,na zauna a jikinsa duk da ya kasance shid’in maras tsalki da tsalkake ubangiji mahalicci, saidai duk k’ok’arin rabani dashi da iyayena sukayi hakan be yiwuba domin kuwa ina so na zame masa wani haske a rayuwarsa ta hanyar d’orashi akan tafarkin tsira wato addinin musulunci,bana son ya mutu cikin kafurci saidai gashi shikuma ya kasance mai taurin kai da tsananin qin musulunci da musulmai,Tin ranar da na ganki naji a raina kece wacce zaki iya bani goyon baya wurin kawo haske a cikin rayuwar sa,saboda naga ko kad’an ke bakisan miye tsoro ba sannan kinada Hankali da kuma hikimar iya magana bugu da qari kinason addininki kuma kina matuk’ar kishin addinin ki,wannan ne dalilin da yasa na fara bibiyar rayuwarki da sunan ni masoyinki ne kuma ina fito miki da siffar sa har saida nasamu na had’aku,nine na cilastamasa a ransa dole sai ya d’aukeki wurin aiki duk da ko kad’an matsayinki bai kai kiyi aiki a k’ark’ashinsa ba,wanda hakan yayi matuk’ar ba mutane da dama mamaki tare da sosa ran wasu”.

Cike da tsananin mamaki nake kallon sa,don gabaki d'aya jikina yayi sanyi,mik'ewa yayi ya cigaba da fad'in,

"Yanzu haka Daniel ya fad'a tsundum cikin kogin k'aunarki,wanda zan tabbatar miki bai tab'a son wata 'ya mace ba bayan ke kuma bazai tab'a son wata ba sai ke,Meenal ina so ki karb'i soyayyar sa,ki fitar da shi daga hanyar b'ata ki janyosa cikin hasken musulunci idan kikayi haka to zakiga sakamako mekyau a wurin Allah,sannan zaki samu lada mai d'umbin yawa,a halin yanzu kinada babban muhalli a cikin zuciyarsa,inada tabbacin zai iya yin komai a kanki".

Nima mik'ewa nayi ina kallonsa don na kasa gasgata abun da yake fad'a min,na kasa yarda da kalamansa don nasan wannan bazai zama gaskiya ba,saidai idan akwai wata manufa.

"Ni Meenal bazan iya soyayya da arne ba,taya kake tsammanin zan yarda da duk wannan bayanai da kake min?,Na farko dai ni bazan tab'a amincewa da wannan k'uduri naka ba sam,abu na biyu bazan iya ba,kai me zai hana ka musuluntar da shi?,ai kaima musulmi ne,abu na k'arshe ina so ka fita rayuwata ga baki d'aya saboda tin lokacin da ka shigo rayuwata na kasa samun sukuni a kullum cikin tashin hankali nake, ka hanani jin dad'in rayuwa".

Na k'arashe maganar cike da takaici don ganin nake wannan ai rainin wayo ne,taya za'ace duk fad'in duniyar nan saini zai jibgama wannan babban aikin da nake da tabbacin bazai tab'a yin tasiri ba ballanta akai ga zancen nasara.

"Meenal bijirewar ki shine zai zamo babban kuskure a rayuwarki,zan hanaki farin ciki na har abada idan har kika bijirema maganata,ga baki d'aya saina zamo miki masifa a rayuwarki".

Cike da dauriya tare da nuna jarumta mai tattare da rashin tsoro nace;

"Ni nasan cewa Akwai Allah kuma shid'in ba azzalumin sarki ba ne,shine zai sakamin akan cutarwar da kake min,don inada tabbacin baka fi qarfinsa ba,kuma kai baka isa ka cutar da ni ba saida izini da yardar sa".

Ina gama fad'in haka na fara waige-waige saidai bansan inda zan dosa ba,duk inda na duba sai inga ruwa masu yawan gaske a kwance.

Wata mahaukaciyar dariya ya bushe da ita yace;

“Bazaki tab’a samun kub’uta a gareni ba har sai kin amince da maganata,idan kuwa kika qi zan cigaba da azabtar da rayuwar ki ko yanzu kinsan irin wahalar da kike sha a gadon Asibiti,kuma wannan duk yana daga cikin aikina”.

Kallonsa na ke idona sunyi jawur,da qarfin gaske na furta,

“Ka mayar dani inda ka d’aukoni,idan ba haka ba jikinki zai gayama”.

K’ara sakin wata dariyar yayi yana tafa hannayensa,nan take ya rikid’a ya koma wani irin balagaggen zaki majiyin k’arfi,banyi auneba naga ya fara tunkaroni gadan-gadan.

Ja da baya na farayi don na tsorata ainun,addu’oin tsarin ubangiji na fara karantowa domin kuwa nasan shine kawai zai iya kub’utar dani daga hannun wannan azzalumin.

“La’ilaha illah anta subhanaka inni kuntu minazzalimin,Wala ya’uduhu hifzuhuma wa huwal aliyyul azim,Wallahu galibul ala amrihi wa la’ilaha ilallah wallahu akbar”.

Take naga fuskarsa ta chanja,inda wata bak’ar guguwa ta turnuk’esa rawa jikinsa ya fara kamar mazari daga k’arshe ya fad’i a qasa,nima wani irin jiri naji ya debeni na fad’i a k’asa har lokacin ban dena addu’o’in da nake ba.

Fitowar Anty Sadiya daga Toilet kenan ta tarar da Meenal na kwararo addu’oi,da mugun sauri ta iso gareta tana fad’in,

“Meenal kin samu lafiya?,Alhamdulillah,Allah abun godiya”.

A hankali na bud’e idanuwana da suka min mugun nauyi ga wani irin nauyi da kaina yayimin,dishi-dishi nake ganin Anty Sadiya,dak’yar na iya d’aga hannayena na mik’o mata da sauri ta rik’ani nasamu na zauna ina kallon Anty Sadiya da farin cikin ta ya gaza b’oyuwa.

“Sannu Meenal,Yanzu meke miki ciwo?”.

Ta fad’a tana zama kusa da ni cike da kulawa,Murmushin dole na sakar mata don Ko kad’an bana jin zan iya magana saboda wani iri da naji bakina yayi duk babu d’ad’i,ganin kallon da nake bin jikina dashi ya sanya Anty Sadiya fad’in,

“Bara naje na had’a miki ruwan wanka Meenal”.

Tana gama fad’in haka ta mik’e da sauri ta nufi Toilet,ba jimawa sai gata ta dawo hannunta d’auke da Towel,da taimakonta na cire kayan jikina ta rik’ani zuwa Toilet,saida ta tabbatar zan iya wankan da kaina sannan ta baro Toilet d’in fuskarta d’auke da murmushin farin ciki,wayarta ta d’auka ta kira Yaya domin sanar dashi.

Saida na fara yin brush sannan na yi wanka,abubuwa da damane chunkushe a k’wak’walwata,na rasa wanda zan tunkara in sanar dashi ainahin abinda ke damuna,inason tunano abubuwa da dama a raina amma na kasa tuno komai.

Idan naji ruwan comments zakuji new update a gobe.😅✋

~mrsbalarabe✍️~

*KAUNAR ƁOYE!!!*
_(THE SECRET LOVE!🖤)_

*Fatima Batula✍🏼*

_Wattpad:mrsbalarabe._

*Telegram*👇
https://t.me/joinchat/GxqDXvsOyg0Xr4s8

*Dedicated to my Anup(my happines) Allah ne kawai yasan irin son da nake yi miki, ke abun so ce dole duk wanda ya raɓeki ya soki, baki na bashi da kalaman godiya da nuna irin matsayinki a gurina sai dai kawai na ce ke ta musamman ce a cikin rayuwa ta, Allah yabaki Ify ya baki miji na gari. Amin thumma Amin.*

_Page_

_31-32_

✍ *✍ ǴÓĹĎÉŃ ṔÉŃ ẂŔÍŤÉŔŚ ÁŚŚÓĆÍÁŤÍÓŃ* ✍✍

*wє αrє вєαrєr's σf sσ gσldєn pєn*
*wє wrítє αssídíσuslч pєrcєívє nσ pαín,*
*sσ mαgícαl σur crєαtívє gσldєn pєn* ✍ *,вєhσld σur wσrds.α prσduct σf σur pєn* *,sαvσur σur wσrds, fσr ít wíll* *cαusє чσu nσ pαín.*

*INA MASOYAN LITATTAFAN KUNGIYAR GOLDEN PEN?*

*NESA TA ZO KUSA, TUNANIN RASHIN SAMUN NEXT PAGE YA ƘARE!.*

Kasance mutum na farko da zai fara karanta sabbin littattafan marubutan mu, a duk lokacin da muka yi typing. Kina/Kana iya samu, ta wannan damar ce kawai idan ka bi wannan links tare danna *LIKE* a shafin mu na Facebook zaka/zaki iya samun cigaba ko kuma ki samu duk littafin da kike buƙata namu daga farko.

https://www.facebook.com/Golden-Pen-Writers-Association-102095951667849/

Sai kun zo, kar ku manta a koda yaushe comments da sharhin ku yana ƙara mana ƙarfin gwiwa a wajen rubutu mai yawa.

Cikin sanyin jiki na fito daga Toilet d'in ina kallon Anty Sadiya da wasu nurses dake tsaye suna kallona wanda nake tinanin kallon mamaki ne,basarwa nayi Ina gyara d'aurin Towel d'ina,murmushi Anty Sadiya ta sakar min tana fad'in,

“Meenal kin fito?”.

Zama nayi a kusa da ita sannan nace;

“Eh Anty”.

Daga haka ban sake cewa komai ba,akwai abinda nake son tinawa a raina amma na kasa.

Cikin halshen turanci Nurses d'in suka ce min,

“Sannun ki,Ya kike jin jikin naki yanzu?”.

Kallon su nayi sannan na kalli kaina,sai chan nace;

“Lafiya”.

Ficewa sukayi daga Office d'in inda na samu damar sanya kayan da Anty Sadiya ta mik'omin.

“Karfe nawa?”.

Na tambaya don inaso in gabatar da Sallah,wayarta ta duba tana fad'in,

“K'arfe biyu da rabi,zakiyi sallah ne”.

“Eh”.

Hijab ta d’aukomin tare da shimfid’amin darduma,ba b’ata lokaci na fara gabatar da Sallar,bayan na sallame ne ta zubomin Abinci tana fad’in,

“Ki samu kici ko kad’an ne”.

D’an guntun murmushi na saki,don kuwa ni yanzu bata abinci nake ba,ina da muradin komawa gida,don a yanzu banida burin da ya wuce in ganni a garin Kano kusa da Mama nah,farin cikin rayuwata.

Anty Sadiya na k’ok’arin magana aka turo k’ofar d’akin,dukan mu daga kai mukayi muna kallon k’ofar Yaya ne hannunsa d’auke da Bak’ir,tsantsar farin cikine bayyane a fuskarsa har ya iso inda muke.

“Meenal!,ya jikin ki,fatan kin samu sauk’i sosai?”.

Rungume Bak’ir da yayo kaina nayi ina murmushi cike da Qaunar wannan ahalin nace;

“Alhamdulillah Yaya”.

Murmushi yayi yace;

“Masha Allah,Gaskiya tsiwa baby rashin lafiyar nan taki ta tayar muna da hankali sosai,dubi yanda Sweetheart duk tabi ta rame kamar itace mara lafiyar”.

Turo baki nayi,ina b’alla mishi harara nace;

“Kanka akeji wallahi,ni nan da kake ganina bar muku garin ma zanyi don bazan k’ara koda kwana biyu ba a garin nan”.

Nan take naga fuskokin su sun sauya cikin mamaki Anty Sadiya tace;

“Kamar ya?,Ban fahimceki ba Meenal”.

“Ina nufin jibi zan koma gida,saboda ina kewar Mama da yawa”.

“Haba Meenal,ai inace mun riga da mun kai k’arshen wannan maganar tunda nace miki tare

zamu tafi kamin Sallah”.

Anty Sadiya ta fad’a fuskarta d’auke da damuwa,kawar da kai nayi daga gareta don banajin zan iya fasa tafiyar nan,akan me?,akan wane dalili za’a wani bi a rik’eka garin arna?,akan me zasu hanani tafiyata,gaskiya nikam jibi sai Kanon dabo,duk a raina nake wannan zance.

“Zaifi kam kibari kuje tare,inada tabbacin Mama zatayi farin ciki da hakan”.

Cewar Yaya yana kallona,cike da ba matarsa goyon baya,shiru nayi ina nazari a raina,daidai lokacin Dr ya shigo tare da Nurses d’in da suka fita.

Tun kafin ya k’araso garemu yake min murmushi nikuwa na wani had’e rai don bansan me murmushin nashi ke nufi ba.

“My Patient ya jikin naki?,Akwai wani wurin da ke miki ciwo?”.

“Naji sauk’i”.

Na fad’a ina hararar shi k’asa-k’asa,bai k’ara cewa komai ba ya fara aunani domin k’ara tabbatar da lafiyata,murmushi yayi ganin yanzu kam komai lafiya,nan ya shiga rubuce-rubucen sa bayan ya kammala ya mik’ama Yaya takardar Sallama,bayansa Yaya yabi suka fice daga d’akin.

Wani sanyi naji a raina don duk takure nake zaune a Asibitin,Mik’ewa Anty Sadiya tayi ta fara harhad’a kayan mu,Yaya yazo ya kwasa ya kai mota,cikin d’an k’ank’anin lokaci muka gama komai,Yaya yajamu muka koma gida,dukan mu a pallor muka yad’a zango muna fira jefi-jefi daga bisani Yaya ya fice daga gidan ya barmu.

Hannayena Anty Sadiya ta kama tana fad’in,

“Ina son in tambaye ki Meenal”.

“To ina jinki Anty”.

Na fad’a ina murmushi.

“Wai menene ya faru dake ranar a ma’aikata?”.

Dummm naji k’irjina ya buga,a mugun tsorace na kalleta, take naji abubuwan da suka faru a baya suna dawomin a kai,wani shahararren tsoro naji ya mamaye zuciya ta.

“Kinyi Shiru Meenal”.

Mik’ewa nayi da sauri ina girgiza mata mai,da gudu na nufi hanyar d’akina,ina isa na fad’a kan gadon ina dafe saitin zuciyata da nake jin yana bada dam!dam!!.

Cike da dana sanin wannan tambayar Anty Sadiya ta nufi d’akin ta tana ji inda ma bata tambayi Meenal ba,yanzu shikenan idan wani abu ya faru da ita kuma?,duk ita ce taja,fashewa tayi da kukan tausayin Qanwar tata.

Sai k’arfe Shidda Na falka daga b’arawon baccin da ya saceni,da sauri naje nayo alwala nayi sallar la’asar,bayan na kammala na d’auko Al-Qur’ani na fara karanto suratul Kahfi,Ina gaf da kammalawa Anty Sadiya ta shigo d’akin zama tayi akan gado har saida na kammala karatun sannan na juyo ina kallonta fuskata d’auke da murmushi nace;

“Ina yini Aunty”.

“Lafiya Lau,Meenal”.

“Ya kike?”.

“Alhamdulillah”.

“Masha Allah,ki taso muje ga Abinci can muci”.

“To Anty nah,muje muci”.

Na fad’a ina mik’ewa duk da banso hakan ba,saidai nayi ne don kawai faranta ranta,kan dainy muka isa inda ta zuzzuba muna abincin muka fara ci,sosai abincin yayimin dad’i inaci ina santi sai dariya ta Anty Sadiya keyi,bayan mun kammala cin abincin muka koma pallor muna kallo tare da fira jefi-jefi,sosai na saki jikina don fitar da su daga cikin yanayin damuwar da suke,da dare Yaya ma da ya dawo mukaita kaftawa dashi, sai firar da dariyar mu mukeyi cike da Qaunar junan mu.

*Washe Gari*

Cikin shirin zuwa aiki Anty Sadiya ta shigo d’akina,inda ta sameni zaune inata karatun Al-Qur’ani na don yanzu shine ya zamar min maganin damuwata,saida na kai aya,na ajiye ina mik’ewa nace;

“Anty har kin shirya?,gashi ni ko wanka banyi ba”.

Zaro ido tayi tace;

“Idan da kinyi wankan ina zakije?”.

Cike da rashin tunanin komai nace;

“Wurin Aiki manah”.

“Hmmm Meenal kenan,ai Boss ya baki hutun aiki har sai kin murmuje sannan zaki koma,nima naji dad’in hakan”.

“To shikenan a dawo lafiya”.

“Yawwa Meenally tah,to kizo muje muyi break ko”.

“A’ah Anty,je kiyi abinki ni sai anjima zanyi”.

Ficewa tayi daga d’akin inda nikuma na cigaba da Karatun da nakeyi inajin wata nutsuwa na wanzuwa a cikin zuciyata tare da wani nishad’i wanda na dad’e banji irinsa ba.

_Sharhi mai tsayi shine ze bani k’warin gwuiwar antayo muku typing ba tare da na gaji ba_

*#Vote*
*#Comments and like*

~mrsbalarabe✍️~

*ƘAUNAR ƁOYE!!!*
_(THE SECRET LOVE!🖤)_

*Fatima Batula✍🏼*

_Wattpad:mrsbalarabe._

*Telegram*👇
https://t.me/joinchat/GxqDXvsOyg0Xr4s8

*Dedicated to my Anup(my happines) Allah ne kawai yasan irin son da nake yi miki, ke abun so ce dole duk wanda ya raɓeki ya soki, baki na bashi da kalaman godiya da nuna irin matsayinki a gurina sai dai kawai na ce ke ta musamman ce a cikin rayuwa ta, Allah yabaki Ify ya baki miji na gari. Amin thumma Amin.*

_Page_

_33-34_

*Wannan page nakune K'AUNAR B'OYE FANS GROUP da kuma FATIMA BATULA PALACE. Mrs balarabe na godiya sosai da nuna soyayya ga littafina na  K'aunar b'oye,Ina alfahri daku a

koda yaushe,son so fisabilillah♥😍😊*

✍ *✍ GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATION* ✍✍

*wє αrє вєαrєr's σf sσ  gσldєn pєn*
*wє wrítє αssídíσuslч pєrcєívє nσ pαín,*
*sσ mαgícαl σur crєαtívє gσldєn pєn* ✍ *,вєhσld σur wσrds.α prσduct σf σur pєn* *,sαvσur σur wσrds, fσr ít wíll* *cαusє чσu nσ pαín.*

*INA MASOYAN LITATTAFAN ƘUNGIYAR GOLDEN PEN?*

*NESA TA ZO KUSA, TUNANIN RASHIN SAMUN NEXT PAGE YA ƘARE!.*

Kasance mutum na farko da zai fara karanta sabbin littattafan marubutan mu, a duk lokacin da muka yi typing. Kina/Kana iya samu, ta wannan damar ce kawai idan ka bi wannan links tare danna *LIKE* a shafin mu na Facebook zaka/zaki iya samun cigaba ko kuma ki samu duk littafin da kike buƙata namu daga farko.

https://www.facebook.com/Golden-Pen-Writers-Association-102095951667849/

Sai kun zo, kar ku manta a koda yaushe comments da sharhin ku yana ƙara mana ƙarfin gwiwa a wajen rubutu mai yawa.

<><><><><><><><><><><><><>

A b’angaren Sir Daniel ana sallamar su Meenal,Likitan ya buga masa waya ya sanar dashi,yaji dad’i sosai da samun lafiyarta,don sosai yake missing d’inta,beda burin da ya wuce ta dawo office ya d’ora idanuwansa akan kyakkyawar fuskarta.

Yau da wuri Anty Sadiya ta dawo daga wurin aiki,nidai ban tambayeta daliliba duk da nasan bai

rasa nasaba da rashin lafiyata,A tare mukayi girkin rana duk da tayi qoqarin hanani amma nak'i hanuwa dole ta barni muka gama tare,wanka naje na sake yi na sanya wata Arabian gown bak'a wacce tayi mugun amsar jikina,kallon kaina nayi a mirror duk na rame nayi k'assa kamar ba niba saida nayi sallar la'asar sannan na wuce pallor,Ina fitowa Anty Sadiya ta hau kod'ani akan nayi kyau sosai,nidai murmushi kawai nayi mata na baje kan Capet inda ta baje muna abinci,muna cin Abincin muna fira,wayar Anty Sadiya ce tayi k'ara ta d'aga,banji mai aka cemata ba naga dai tayi murmushi tana fad'in,

"Okay Sai kunzo".

Tana katse wayar ta kalleni tace;

"Anty Rabi'a ce da Khalid ke tafe".

Sosai naji gabana ya fad'i ambatar sunan Khalid da tayi don ni harna manta da wani Khalid,d'an guntun murmushi nayi mata nace;

"Allah ya kawo su lafiya".

Daga haka muka cigaba da cin abincin,tsawon 20 minutes mukaji ana k'wank'wasa k'ofa,Mik'ewa nayi naje na bud'e,Anty Rabi'a ce ta fara shigowa tana ganina ta saki murmushi tana fad'in,

"Masha Allah,Meenal Kam jiki yayi sauk'i,Ya k'arfin jikin naki?".

Nima ina murmushi nace;

"Alhamdulill....".

Na kasa k'arashe zancen sakamakon sark'ewa da idanuwan mu sukayi wuri d'aya,inda ya kafeni da rikitattun idanunsa kamar wani tsohon maye,da sauri na janye idona,na matsa gefe don basu hanyar shigowa,saida suka wuce nasamu damar rufe k'ofar na biyo bayan su,inajin kamar in shigewata d'aki saidai nasan Anty Sadiya zata tuhumeni akan hakan.

Gaisawa suka shiga yi da Anty Sadiya inda Anty Rabi'a ke k'ara tambayar k'arfin jikina,naji dad'in hakan a raina saboda matar ta nunamin k'auna,Anty Sadiya ce ta kalli Khalid tace;

"Bakazo ganin Meenal a hospital ba".

D'an Sosa kai yayi yace;

"Wallahi Anty naje kotono sai jiya na dawo,Shine Anty take fad'amin Meenal batada lafiya".

Ya k’arashe maganar yana kallon inda nake zaune yace;

“Meenal Ya jikin?”.

Ba tare da na kalleshi ba nace;

“Naji Sauqi Alhmdlh”.

Fuskarsa d’auke da murmushi yace;

“Masha Allah,Allah ya k’ara sauki”.

Dukan mu muka amsa da Ameen, nan su Anty Sadiya suka shiga duniyar su wacce a koda yaushe basa gajiya da fira kala-kala,nikuwa duk na tsargu da kallon da Khalid kemin wanda har kallon ya fara zama na wulak’anci,wulak’anci manah,to miye mutum zai rik’a kallon ka tun daga k’asa har zuwa sama sannan ya d’auko daga saman zuwa k’asa?,hak’urina ne ya k’are na mik’e da sauri zan bar wurin Anty Sadiya tace;

“Yauwa Meenal,Please ki d’auko Musu Drinks”.

Kamar in fasa ihu naji,a dak’ile nace;

“Uhum”.

Sannan na wuce zuwa kitcheen k’afafuwana sai hard’ewa suke kamar zan fad’i,nasan ba komai ne ya haddasa min hakan ba sai kallona da Khalid keyi wanda na rasa tantance wani irin kallo ne yake min,plate biyu na d’auko na jera drinks d’in a ciki na kaimusu sannan nashige d’akina,kan gado na fad’a ina nazarin wannan kallo da Khalid kemin.Bansan tafiyar su Khalid ba sakamakon baccin da yayi awon gaba dani,saida na fito pallor kallo ne Anty Sadiya ke cemin ai sunyi jiran in tashi bacci ban tashi ba suka wuce,murmushi kawai nayi bance komai ba.

Washe gari

Tin safe muke faman aikace-aikacen gyaran gida Dayake weekend ne Anty Sadiya bata fita aikiba,ko ina na gidan yayi fess gwanin birgewa.bayan mun gamane muka dawo pallor muna kallon shirin Asintado a tashar d’ad’in kowa.

“Anty akwai inda ake saloon nan kusa?”.

“A’ah,amma kibari anjima muje inda nake zuwa”.

Ta fad’a hankalinta na akan kallon da muke don Anty Sadiya na mugun son shirin Asintado.

“To shikenan,wallahi duk banajin dad’in kan nan”.

Na fad’a ina mik’ewa zuwa d’aki,don dama ni kallon ba wani damuwata yayi ba,harna kai k’ofar d’akina bugun k’ofar da najine ya tsaidani,juyowa nayi na kalli Anty Sadiya ko zataje ta bud’e amma naga batada alamar tashi,hakan yasani juyawa na koma wurin k’ofar na bud’e tare da d’an lek’awa ina fad’in

“waye?”.

Yana tsaye fuskarsa d’auke da murmushi ga wasu uban manyan ledoji da ke rik’e a hannuwanshi,manyan kayane sanye a jikin shi farar shaddar tayi mugun amsar farar fatarhi,sai zuba k’amshi yake na fitar rai.Da sauri nayi baya ina fad’in,

“Au ashe kaine?,Sannu da zuwa”.

Murmushi ya sake min yace;

“Nine kuwa,ko na koma?”.

Dariya nayi nace;

“Inhar komawar bazatayi maka wuya ba shikenan”.

Na k’arashe maganar ina yin gaba.

“Keda waye Meenal?”.

Anty Sadiya ta tambaya tana kallo na,gefenta na zauna kafin na kai da bata amsa ya shigo yana fad’in,

“Khalid ne Anty”.

Cikin fara’a Anty Sadiya tace;

“Sannu da zuwa”.

Bayan sun gama gaisawa ne,Anty Sadiya ta mik’e don ta d’an fahimci wani abu,bin bayanta

nayi da kallo harta shige d’akinta,me Anty ke nufine?,meyasa zata tafi ta barni?,Na shiga tambayar kaina.

“Ya k’arfin jikin naki?”.

Na tsinkayo muryar Khalid,murmushin yak’e nayi nace;

“Nifa naji sauk’i sosai,harma na fika lafiya”.

“Taya zan iya tabbatar da hakan?”.

Ya fad’a yana d’age min gira d’aya fuskar nan tashi d’auke da murmushin dake k’ara bayyanar da kyawunsa,haka dai muka tsinke da fira nida shi,sai labarai yake bani,sosai na tsinci kaina a cikin nishad’i saboda na fahimci shid’in mutum ne mai son barkwanci,cikin dubara ya amshe number wayata nikuwa ban kawo komai a raina ba.

K’arfe uku dai-dai Khalid ya mik’e yace zai wuce,hakanan kawai sai naji a raina kamar ya tsaya mu cigaba da firar mu bansan dalili ba,nima mik’ewa nayi nace;

“To bara na kirama Anty kuyi sallama”.

“A’ah kawai ki barta,idan ta fito kyace  mata na wuce”.

“Shikenan”.

Na fad’a,har ya fara tafiya ya juyo

“Bazaki rakani ba?”.

Ya fad’a yana kallon yanda nayi tsaye ina jiran fitar sa,bance komai ba nabi bayan sa,a bakin kof’a nayi tsaye ina fad’in,

“Nagode sosai”.

“Karki damu,sai munyi waya”.

Ya fad’a yana sakemin wani murmushi mai wuyar fassarawa sannnan ya wuce,rufo k’ofar nayi daidai lokacin Anty Sadiya ta fito d’auke da yaronta Bak’ir da ya tashi daga bacci,harara na b’alla mata nace;

“Sannunki da tafiya ki barni”.

K’yalk’yalewa da dariya tayi tace;

“To ai naga bak’on naki ne shiyasa”.

Zaro ido nayi nace;

“Kamar ya bak’ona?,Duka yaushe na sanshi ma har zai zamo bak’ona?”.

Zama tayi tana murmushi tace;

“Nidai rabani da wannan tambayoyin naki,bara muga me aka kawo munane kayan dubiya”.

Daga haka ta janyo ledojin ta fara bud’awa,d’ayar ledar shak’e take da kayan marmari dangin su Apple,ayaba,lemo,gwanda da dai sauran su,d’ayar ledar kuwa gasassun kajine guda biyu.

“Lallai abun nayine,wannan hidima haka”.

Anty Sadiya ta fad’a tana rik’e baki,nidai ina tsaye ina kallonta na kasa cewa komai,saboda wani tunani da naji ya d’alsu a zuciyata,da sauri na kawar da tunanin don banason yayi tsawo,da haka na d’auki Bak’ir ina mishi wasa.Mik’ewa Anty Sadiya tayi ta nufi kitchen ta dauko plate,ta fasaltamuna naman muka ci.muna kammalawa ta sanya sauran a fridge tare da fruits d’in,Saida muka gabatar da sallar la’asar sannan shirya muka fice daga gidan zuwa wurin Saloon,bamu dawo ba sai k’arfe bakwai saboda layin da muka tarar a wurin Saloon d’in.

Da dare Ina k’ok’arin kwanciya naji wayata ta fara k’ara,bak’uwar number nagani hakan ya tabbatar min da Khalid ne,wayar na shirin katsewa na d’aga,shid’in ne kuwa,bayan mun gama gaisawa nanma muka d’inke da fira sai k’yalk’yala dariya nake sai kace sabon kamu,sai da nafara jin bacci sosai mukayi sallama na katse wayar daga haka bacci ya d’aukeni.

Cikin d’an k’ank’anin lokaci mukayi mugu-mugun shak’uwa da Khalid,don kusan kullum sai munyi waya,ko kuma yazo wurina musha fira,tuni Anty da Yaya suka halbo jirgin Khalid nikuwa ban kawo komai a raina ba har zuwa yanzu,don ni na d’aukesa a matsayin abokin firata na musamman.

Zuwa Yanzu na dawo normal kamar bani bace Meenal da na rame kwanakin baya,hankalina kwance har na manta da wata abu wai damuwa,a kullum cikin farin ciki nake,nadena jin d'uriyar dan rainin hankalin nawa nasan hakan yana daga cikin add'u'oin da nakeyine Allah yayimin gaba dashi.

Rayuwata nake cikin walwala musamman ma da Khalid ya shigo cikin rayuwar tawa don yana d'ebe min kewar abubuwa da dama,aiki kuwa sam naji ya fitar mun a rai, saidai inga Anty Sadiya na zuwa,nikuwa kullum ina gida ina hutawa,don yanzu sam bana muradin sake had'a ido da wannan arnen don gani nake shine damuwata,nisanta kaina da nayi dashi kuma na samu kwanciyar hankali sosai.

************************************

Sir Daniel yayi kewar Meenal sosai wanda har saida yayi 'yar rama,yana muradin ganin Meenal saidai gashi yau tsawon kwanaki masu yawa baiji d'uriyarta ba,duk yabi ya damu da rashin Meenal,tinani ya shigayi a ransa kodai tabar aikin ne?,Meyasa zata bar aikin?,daga haka ya yanke shawarar tambayar Anty Sadiya yaji miye dalilin rashin dawowar Meenal wurin aiki.

*Sharhinku shike k'aramin kaimi wurin yimuku typing a koda yaushe,nagode fans abun alfahri*💃🥰

*#Vote*
*#Comments and like*

~mrsbalarabe✍️~

*KAUNAR ƁOYE!!!*

_(THE SECRET LOVE!🖤)_

*Fatima Batula✍🏼*

_Wattpad:mrsbalarabe._

*Telegram*👇
https://t.me/joinchat/GxqDXvsOyg0Xr4s8

*Dedicated to my Anup(my happines) Allah ne kawai yasan irin son da nake yi miki, ke abun so ce dole duk wanda ya raɓeki ya soki, baki na bashi da kalaman godiya da nuna irin matsayinki a gurina sai dai kawai na ce ke ta musamman ce a cikin rayuwa ta, Allah yabaki Ify ya baki miji na gari. Amin thumma Amin.*

_Page_

_35-36_

✍ *✍ ĠÓĹĎĖŃ ṔĖŃ ẂŔÍŤĖŔŚ ÁŚŚÓĆÍÁŤÍÓŃ* ✍✍

*wє αrє вєαrєr's σf sσ gσldєn pєn*
*wє wrítє αssídíσuslч pєrcєívє nσ pαín,*
*sσ mαgícαl σur crєαtívє gσldєn pєn* ✍ *,вєhσld σur wσrds.α prσduct σf σur pєn* *,sαvσur σur wσrds, fσr ít wíll* *cαusє чσu nσ pαín.*

*INA MASOYAN LITATTAFAN KUNGIYAR GOLDEN PEN?*

*NESA TA ZO KUSA, TUNANIN RASHIN SAMUN NEXT PAGE YA KARE!.*

Kasance mutum na farko da zai fara karanta sabbin littattafan marubutan mu, a duk lokacin da muka yi typing. Kina/Kana iya samu, ta wannan damar ce kawai idan ka bi wannan links tare danna *LIKE* a shafin mu na Facebook zaka/zaki iya samun cigaba ko kuma ki samu duk littafin da kike buƙata namu daga farko.

https://www.facebook.com/Golden-Pen-Writers-Association-102095951667849/

Sai kun zo, kar ku manta a koda yaushe comments da sharhin ku yana ƙara mana ƙarfin gwiwa a wajen rubutu mai yawa.

---

Fitowata kenan daga kitchen Anty Sadiya tace;

“Zo Meenal”.

zama nayi gefenta ina fad’in,

“Gani Anty”,

“Yawwa dama akan maganar komawa wurin aikine,naga kin share zancen”.

B’ata fuska nayi nace;

“Nifa Anty na ajiye aikinnan,wallahi ya fitarmun a rai”.

Da mugun mamaki ta kalleni.

“Kamar ya kin aje aiki Meenal?,Wace irin magana kike haka?,Meye dalilin ki na yin hakan?”.

Turo baki nayi.

“Saboda ajiye aikin shine kwanciyar hankalina,Idan har na cigaba da aiki da Daniel to nasan bazan tab’a samun kwanciyar hankali ba”.

“Wannan ba hujja ba ce Meenal,kisani cewa Allah shine keyin komai,mutun bai isa ya miki

abunda Allah bai nufa ba,kima cire wannan a ranki".

Hannuwan Anty Sadiya na kama.

"Ya kamata ace kin fahimceni Anty,Tinda na fara had'uwa da wancen mutumen rayuwata take cikin matsala,a koda yaushe banida kwanciyar hankali kuma kun rasa naku,zanso ace kin amince da wannan dalili nawa".

Shiru Anty Sadiya tayi na wasu sakanni sannan tace;

"Shikenan tinda kin zab'i hakan".

Tana gama fad'in haka ta mik'e tabar wurin fuskarta ba yabo ba fallasa,da kallo nabi bayanta harta shige d'akinta,duk sai naji jikina yayi sanyi don koda Anty Sadiya bata fito ta bayyana mini b'acin ranta a fili ba nasan ranta ne ya b'ace.

Mik'ewa nayi na koma d'akina ina jin duk babu dad'i a raina,shawara nashiga yi da zuciyata amma sai rayamin take karna koma aikin,wani uban tagumi nayi ina tinanin meyasa zan b'atawa Anty rai?,bayan ita kullum batada burin da ya wuce taga ta farantamin rai,Indai cigaba da aikina zai faranta ranta to ba shakka dole nayi hak'uri na cigaba da aiki a k'ark'ashi Daniel koda kuwa hakan shine zaiyi sanadiyar rayuwata,da wannan k'udurin na mik'e da sauri na nufi d'akin ta,zaune na tarar da ita tayi shiru alamar tayi nisa cikin tunani sosai, dafata nayi ina fad'in,

"Anty!".

Da sauri ta d'ago ta kalleni,tare da sauke ajiyar zuciya tace;

"Ya akayi kuma?".

Cike da sanyin jiki nace;

"Kiyi hak'uri Anty nasan ranki ya b'aci,Insha Allah zan cigaba da aiki indai hakan zai faranta

ranki”.

Duk da Anty Sadiya taji dad’in maganar Meenal sai bata nuna ba,sai ma kawar da kanta da tayi gefe kamar bataji mai nake fad’a ba.

“Please Anty,Kiyi hak’uri”.

Na sake fad’a fuskata d’auke da damuwa,ba tare da ta kalleni ba tace;

“No raina bai b’aci ba,Bazan takuraki ba Meenal kinsan komai saida ra’ayi kuma kin nuna baki ra’ayin aikin shikenan ai babu damuwa”.

Daga yanda take maganar ma ya k’ara tabbatar min da tsantsar b’acin rai take wannan maganar,ban ankaraba sai kawai naji k’wallah sun gangaromin a kunci,durk’ushewa nayi a gabanta ina fad’in,

“Don Allah Anty kiyi hak’uri,Nasan ranki a b’ace yake,wallahi namiki alk’awalin zan koma aiki”.

Na k’arashe maganar kuka na cin k’arfina don har wani zafi nakeji a raina wai Anty Sadiya tana fushi dani?Ni Meenal insa kaina a ina?.

K’yalk’yalewa da dariya Anty Sadiya tayi tace;

“See you!,Miye na wani b’are baki kina min kuka sai kace wata baby girl,na zata ai ban isa dakeba ban kai matsayin da zansaki kiyi ba”.

Da sauri na girgiza kai ina fad’in,

“A’ah wallahi Anty,kin ma wuce hakan”.

Murmushi ta sakarmin tare da rik’o hannuwana na mik’e ta sharemin hawayen dake kwance a kuncina,sannan ta matsamin gefen ta na zauna kaina a k’asa ina wasa da yatsuna,cikin sanyin murya tace;

“Inaso ki fahimci cewa Sir Daniel bayada niyyar cutar dake,duk da kasancewarshi ba musulmi amma baya zalunci,ko kinsan cewa shine da kansa ya d’aukeki a jikinsa ya kaiki asibiti?,Kin kuwa san yanda yake k’yamar musulmai amma ko kad’an bai nuna k’yama a kankiba ya kaiki asibiti abunda yai matuk’ar bawa mutane mamaki har yanzu zancen ake a company,zaki yarda idan nace miki jinin Sir Daniel ya gauraya da naki?”.

Sai a lokacin na d’ago na kalleta cike da tsantsar mamaki don sam ban fahimci abinda take nufi ba,kai ta girgiza min tana fad’in,

“Tabbas jinin sa ya gauraya da naki,domin kuwa sau uku yana bada jininsa ana sanya miki,sannan ya d’auki nauyin komai a hospital,kinga kuwa Sir Daniel ya taka muhimmiyar rawa a cikin rayuwar ki,gode masa ya kamata kiyi ba bayyana k’iyayya a garesa ba,don haka ki zauna kiyi tunani,Bari kiji Meenal wallahi jiya Sir Daniel da kansa ya sameni a office d’ina yake tambayata meyasa har yanzu baki dawo aikiba?,abinda bai tab’ayi ba wato shiga office d’in ma’aikatan shi saidai mutun ya sameshi,amma a kanki ya d’auki k’afafuwansa yakai office d’ina,ga baki d’aya mamaki ne ya cika zuciyata daga k’arshe dai dole na masa k’arya nace kinyi tafiya ne,da kin dawo zaki cigaba da aiki”.

“Gaskiya nayi matuk’ar mamaki Anty,amma shid’in ya kasance yanada kyakkyawar zuciya tare da tausayi kawai fahimtarshi ce banyi ba,In Allah ya yarda zanje in gode masa tare da cigaba da aiki a k’ark’ashin sa har zuwa lokacin da zan bar garin Lagos”.

Murmushin jin dad’i Anty Sadiya tayi tare da rungumeni tace;

“Nagode Sister,Ina matuk’ar alfahri dake a koda yaushe”.

*Kuyi manage da wannan please🙌 Insha Allahu zuwa gobe zaku ga new update*🥳 🥰

*#Vote and like*
*#Comments and Share*

~mrsbalarabe✍️~

ƘAUNAR ƁOYE!!!*
_(THE SECRET LOVE!🖤)_

*Fatima Batula✍🏼*

Marubuciyar👇
~Bugun Zuciyata
~Nida Malamata
~Saif ko Maleek
~Alfarma
~Okhasha Dan Malan
~Billionaire Bilkisu-Paid Story
And Now
~K'aunar B'oye(The Secret Love)

_Wattpad:mrsbalarabe._

*Telegram*👇
https://t.me/joinchat/GxqDXvsOyg0Xr4s8

*Dedicated to my Anup(my happines) Allah ne kawai yasan irin son da nake yi miki, ke abun so ce dole duk wanda ya raɓeki ya soki, baki na bashi da kalaman godiya da nuna irin matsayinki a gurina sai dai kawai na ce ke ta musamman ce a cikin rayuwa ta, Allah yabaki Ify ya baki miji na gari. Amin thumma Amin.*

_Page_

_37-38_

✍ *✍ ǴÓĹĎÉŃ ṔÉŃ ẂŔÍŤÉŔŚ ÁŚŚÓĆÍÁŤÍÓŃ* ✍✍

*wɛ arɛ вɛarɛr's σf sσ gσldɛn pɛn*
*wɛ wrítɛ αssídíσuslч pɛrcɛívɛ nσ pαín,*
*sσ magícal σur crεatívε gσldεn pεn* ✍ *,вεhσld σur wσrds.α prσduct σf σur pεn* *,sαvσur σur wσrds, fσr ít wíll* *cαusε чσu nσ pαín.*

*INA MASOYAN LITATTAFAN KUNGIYAR GOLDEN PEN?*

*NESA TA ZO KUSA, TUNANIN RASHIN SAMUN NEXT PAGE YA ƘARE!.*

Kasance mutum na farko da zai fara karanta sabbin littattafan marubutan mu, a duk lokacin da muka yi typing. Kina/Kana iya samu, ta wannan damar ce kawai idan ka bi wannan links tare danna *LIKE* a shafin mu na Facebook zaka/zaki iya samun cigaba ko kuma ki samu duk littafin da kike buƙata namu daga farko.

https://www.facebook.com/Golden-Pen-Writers-Association-102095951667849/

Sai kun zo, kar ku manta a koda yaushe comments da sharhin ku yana ƙara mana ƙarfin gwiwa a wajen rubutu mai yawa.

---

Fuskata d’auke da murmushi nace;

“Nima haka Anty nah ta kaina,Allah ya barmin ke”.

Anty Sadiya na dariya tace;

“Ameen Qanwata”.

Daga haka muka b’arke da fira cikin matsanancin farin ciki tare da annashuwa,a haka Yaya ya dawo ya samemu munata firar mu,inda shima ya zauna aka cigaba da kaftawa dashi.

_Monday_

Tinda safe muka tashi,muka yi ‘yan aikace-aikacen da muka saba,yau ni na had’a muna breakfast Kunu na dama na soya k’osai don yau da marmarinsu na tashi,daga Yaya har Anty Sadiya sunji dad’in kunun da k’osan,don bazasu iya tuna rabon su dasu ba,ko banza Anty Sadiya tafi karkata wurin girkin turai,sam bata fiye yin abincin mu na al’ada ba,bayan mun kammala break d’in Yaya ya fice zuwa aiki don dama shi a shirye yake,Niko da Anty Sadiya ko wanka bamuyi ba,muma d’akunan mu muka wuce domin yin wankan muyi shirin zuwa aiki.

Shigar wani tsadadden bulan leshi me ratsin fari nayi wanda d’inkin yayi mugun amsar jikina,sai zuba k’amshi nake,gaban mirror naje na shafa powder tare man baki,sannan na yafa gyalena fari a kafad’a,na zura takalmina suma farare,pallor na nufa inda na tarar da Anty Sadiya na jiran fitowata,itama ta shirya cikin wasu riga da wando tayi rolling gyale a kanta.

Mik’ewa tayi tana murmushi.

“Masha Allah Auta,Kinyi kyau sosai”.

“Nagode Anty,Kema haka”.

Na fad’a ina d’aukar yaronta daketa min dariya,kumatunshi na lakuce nace;

“D’an albarka,gaskiya Anty yaron nan yanada hak’uri sosai wallahi,Shikenan shi kullum bakuda lokacin shi saina aikinku,indai ya rab’eku to weekend ne”.

“Ai Bak’ir beda lak’uwa ne,jiya ma munyi magana da Dady shi yace za’a kaishi wurin

lesson,kamin dai yakai lokacin shiga school".

"Gaskiya kam hakan ya dace,nidai gani nake ba wanda zai hanani zuwa da yarona wurin aiki,idan kuwa akace bazan je dashi ba,saidai in bar aikin wallahi".

K'yalk'yalewa da dariya Anty Sadiya tayi tace;

"Ai nasan zaki iya,rigimatu,nidai muje a kaishi mu wuce lokaci na tafiya".

Ban k'ara cewa komai ba don nasan Anty Sadiya bakin rai take da aikin nan nata,amma ina dalili yaro tun yana k'arami baisan dad'in iyayenshi ba?,to inaga ya fara zama babba?.

Wurin da take kaishi reno muka ajiyeshi sannan muka wuce Company,hakanan kawai nake jin gabana na fad'uwa,fitowa mukayi daga motar muka nufi public elevator.

Nafi minti uku tsaye a bakin k'ofar office d'in,gabana sai fad'uwa yake,abinda ya faru ranar naji ya dawo min sabo akai,da sauri na fara jero addu'oi a raina,dak'yar nasamu hankalina ya d'an kwanta,nasamu natsuwa.a hankali na tura k'ofar na shiga don ganin nake idan na tsaya neman izini zan b'ata lokacina.

Zaune yake shida wani Mutun,suna magana,fararen suit ne jikinshi da necktie ja,kayan sunyi mugun mishi kyau,yana ganin shigowarta ya mik'e da sauri yana kallonta,irin kallon mamakin nan,sai kuma yayi d'an murmushi tare da komawa ya zauna idon shi a kanta,ya kasa yarda wai itace yau a office d'insa,abinda bai kawo nan kusa ba.

Kaina na miyar k'asa,saboda wani irin kwarjini naga yayimin,ina isowa inda suke ba tare da na koma kallon shi ba nace;

"Good Morning".

Daidai lokacin Mutumen ya mik'e ya mik'ama Sir Daniel hannu suka sake gaisawa,sannan ya nufi hanyar fita.

"Good Morning Sir".

Na sake fad'a,ganin bai amsa na farkon ba,nanma shiru yayimin hakan yasa nayi saurin d'agowa na kalleshi,yana zaune ya kafeni da rikitattun idanuwanshi fuskarshi d'auke da murmushi mai tattare da tsantsar farin ciki,baiyi zato ko tsammanin ganinta ba,wani sanyi yakeji a cikin zuciyarshi,tabbas yayi kewarta sosai.saurin janye idanuna nayi don gabaki d'aya ya

kashemin jiki da kallon shi,dama haka yake da kyau?,na fad'a a zuci,don kuwa yau yayimin wani mugun kyau,amma kuma naga ya rame,dama indai ba sani kayiba bazaka kirashi arne ba domin kuwa siffar musulmai gareshi sam beda kama da arna,shi kyakkyawane,ina ruwana da kyaunsa?,nayi saurin tambayar kaina.

"Hey,Have a seat".

Najiyo muryarshi yana fad'a,da sauri na zauna kujerar dake kallon shi,saidai nakasa d'ago kaina.

"Ya jikin naki?".

Ya tambaya cikin halshen turanci,Nidai hakanan kawai na tsinci kaina da fad'in,

"Alhamdulillah".

"Alhamdulillah".

Ya maimaita cikin muryar shi ta inyamurai,da sauri na d'ago na sake kallon shi da mugun mamakin yanda ya maimaita duk da nasan bai san mai nace ba,murmushi yayi min yace cikin turanci;

"Menene Ma'anar hakan?".

"Thanks God".

Na fad'a,ina kallon yanda ya maida idanuwansa ya lumshe tare da bud'esu ya sauke a kaina.

"Okay,Na d'auka kin barmin aiki".

Samun kaina nayi da murmushi,don tunda naji irin taimakon da yayimin naji haushi da tsanar shi sun gushemin a zuciyata.

"Meyasa zan dena?".

D'an shafa kyakkyawan sajen fuskarshi yayi yana fad'in,

"Dunno,kawai nayi zaton zaki dena ne".

"A'ah bazan dena ba".

“Well,naji dad’i sosai”.

Ya fad’a yana k’ara sakarmin wani k’ayataccen murmushi.

A hankali nace;

“Nagode sosai da taimakona da kayi,Naji dad’in hakan”.

“Karki damu”.

Ya fad’a,tare da janyo wasu files dake gabanshi ya turosu zuwa gabana yana fad’in,

“Ko zaki taimaka ki mik’ama Pa wannan”.

“Okay,babu damuwa”.

Na fad’a tare da mik’ewa na d’au files d’in,saida nakai bak’in k’ofar fita naji yace;

“Thanks You,Alhamdulillah You’re coming back”.

K’yalk’yalewa nayi da dariya,nace;

“Baka iya fad’a daidai ba fa,amma idan kanaso zan koyama”.

Da sauri ya girgiza kai yace;

“Yes why not?,dagaske zaki koyamin?”.

“Eh”.

Na fad’a tare da ficewa daga office d’in ina dariya,sai yanzu nake k’ara fahimtar kyawawan halayenshi,shi mutun ne mai sauk’in kai,daidai office d’in Pa Tiny na tsaya nayi knock.

“Yes Come in”.

Najiyo muryata,maras dad’in sauraro,tura k’ofar office d’in nayi na shiga,tana zaune da wasu figaggin kaya jikinta,shisha na rik’e a hannunta tana zuk’a,da mugun sauri ta mik’e tana kallona,tace;

“Kin dawo kuma?”.

Tambayar ma dariya taban,irin ta gaji da ganina a company,saikace company ubanta,amma sai nayi murmushi nace;

“Yeah,ga files nan Boss yace na kawo miki”.

Na k’arashe maganar ina aika mata da wani matsiyacin kallo sannan na fice daga office d’in,yayinda Tiny tabi bayan Meenal da wani mugun kallon tsana,don ita duk a zaton ta Meenal tabar aiki a ma’aikatar,ganin yanda ta dad’e bata dawo ba,Lallai ashe mayyar bata bar aikin ba.Ta fad’a a ranta cike da takaici,don tasan shikenan ita da sake shiga wurin Sir Daniel sai wani hali,don duk a ‘yan kwanakin nan duk ita ke aikin da Meenal keyi,da hakane take samun ganin shi,sai gashi yanzu Meenal d’in ta kuma dawo.

Office d’ina na wuce,nayi mamaki sosai da ban tarar da aikin komai ba,sannan office d’in a share kamar ina ciki,zama nayi kan kujerata ina jujjuyawa sanyin Ac na ratsani ta ko’ina,idanuwana na lumshe daidai lokacin wayata ta fara ruri,a hankali na sauke idanuwana akan Screen d’in wayar,wani murmushi nayi ganin me kiran nawa wato friend Khalid sunan da nayi save number d’inshi kenan.

“Hey Meenal,kina gida kuwa?,inzo muje ki rakani wani wuri?”.

“A’ah wallahi,ina office kasan na koma wurin aiki yau”.

“What!?,kin koma wurin aiki shine bazaki sanar dani ba ko?,Yayi nagode”.

Yana gama fad’in haka ya katse wayar,daidaituwa nayi akan kujerar ina bin screen d’in wayar da kallo,k’yalk’yalewa nayi da dariya nace;

“Tofah!,Irin ubana d’in nan”.

Wayar sa na gwada kira amma tana ringing yak’i d’agawa,nanma dariyar nayi ina fad’in,

“Lallaima wannan Khalid d’in,Zaka sani ne”.

Daga haka na bud’e Laptop d’in dake gabana na hau duba abubuwan da akayi lokacin da bana nan,murmushi nayi ganin yanda komai ya tafi daidai.

*#Vote and like*
*#Comments and Share*

~mrsbalarabe✍️~